_*🎀KIYARDA DANI...!🎀*_
🎀🐾🎀

*♝ IᗫTɵ˛˛IǤɵᗫT WɼITɵɼ'ی ASSɷ📚✍️*

*💫DEDICATED: to Sis naja'art*

_*WRITING BY: Zm (CHuBaDo)*_

*✨Special Gift for Hafsat Hafnan (my jika),.*

_Da sunan Allah me rahama mai jinqai, salati da daukaka su tabbata ga manzon tsira annabi Muhammad(s.a.w)_ _Tsarki ya tabbata ga ubangijin da mulkinsa bashi da iyaka, Wanda jinqansa da rahamar sa suka cika ko ina_
_Ya Allah yanda na fara wannan rubutun da ikon ka, ya Allah ka bani ikon saukeshi Ify_

_Page: 1_

_________Kwance take a kan madaidaicin gadon dake d'akin, duk tabi ta barbaza takardunta na makaranta kan gadon, sanye take cikin wasu riga da wando blue and white, wanda sukai matik'ar karb'an jikinta kasancewarta fara, gashin kanta a d'aure yake cikin wani blue ribom wanda ya k'ara fito da ainihin kalar bak'in gashin dake kanta, wani lumsashshen gashi ne ya sakko daga gaban goshinta ya kwanta wanda hakan ya k'arawa halittar fuskarta kyau, kallo d'aya zakayi mata ka fahimci tayi nisa sosai a cikin karatun nata sbda jarrabar dazasuyi ta Waec,

Qofar dakin aka shiga kwanjwasawa cikin nutsuwa, A hankali ta dago fararen idanunta masu matik'ar haske gamida wani irin maik'o a cikinsa, zubawa k'ofar idanu tayi cike da zak'uwar sin ganin wanda ke knocking din,

Rumana ce ta shigo dakin da sallama fiskarta dauke da murmushi, A nitse ta k'araso bakin gadon ta zauna tareda binta da wani irin kallon wanda yafi kamada na mamaki tace, "Umaisa kardai kice min har yanzu karatunnan kikeyi?" Tayi maganar cike da mamaki,

Yarinyar da aka kira da Umaisa ta dago fararen idanunta, tareda yi mata wani irin kallo tace, "gashi kuwa kin gani,"
Maida kanta k'asa ta sakeyi sannan tayi murmushi tace, "I don't won't fall my exam that's why

nake karatun  sosai," kin sani sanin kanki cewar a rayuwa ta na tsani fad'uwa, nasara kawai na sani kuma itace fatana, ta k'are maganar tana yatsina fuska tareda cuno d'an k'aramin cute pink lips dinta,

Dariya sosai Rumana tayi sannan tace, " to naji sarkin son karatu" , "idan kin  ga dama Dan Allah ki zama jikar manga pak.

dariya sukayi gaba daya
Sannan Rumana ta kalli k'anwar nata  tace, "yauwa kinga ma ni wllh har na manta ma da abinda ya kawoni gurinki wllh,"

Da kulawa Umaisa take kallonta sbda jin abinda Rumanan tace,

Murmushi Rumanan tayi sabida ganin ynda Umaisan take kallonta sekace bata tab'a ganinta ba sannan tace, " yauwa dama yaya khabeer ne yace in kira masa ke"

Gaban ta ne yay wani irin fad'uwa a  lokaci guda sbda jin sunan Wanda Rumana ta Ambata!!!

cike da karayar zuciya kamar zatayi kuka ta kalli Rumanan tace, " Dan Allah da gaske kike Ruman?"

Cike da jin haushi Rumana take kalonta sannan tace, "ai kinsan na saba yi miki qarya, 'yar renin hankali kawai," tana kaiwa nan ta fice daga dakin gaba daya, tana k'unshe dariyata,

Jikin Umaisa ne yay bala'in sanyi sbda tasan halin yayan nasu Sam baya wasa dasu musamman ma ita,

A hankaki ta fara k'ok'arin Mik'ewa tareda sakko da santala santalan fararen k'afafunta k'asa,

Zarazara   hannunta tasa ta dauki wani Dan k'aramin mayafi ta rufe kanta dashi sannan ta sinkuya ta jawo wani tattausan takalmi me yalwar gashi a jijinsa, a nitse ta zira kyakkyawar k'afarta ma'abociyar dogayen yatsu a ciki,

Masha Allah kawai na  iya firtawa sabida ganin cikar zatin da Umaisa take dashi,

Fita tayi tareda Jan k'ofar dakin nata ta rufe, sannan ta fara  takawa a sannu a hankali sekace wata me tausayin k'asa,

Wani siririn corridor naga ta biyo, sannan ta fito wani katafaren makeken parlor me azabar kyau gamida tsari, sbda yanda aka k'awata shi da mata'ulhayat na duniya,

A hankali take tafiya kamar wata wahainiya sabida tsari, har ta samu nasarar k'arasawa bakin k'ofar da zata sadata da side din yayan nasu, Da sallama ta tura k'ofar dakin tareda kutsa kai

ciki,

Parlor ne me girma wanda aka k'awatashi da wasu rantsatsun Royal chiars yan gaske  masu launin ruwan madara ganida yarfen ruwan zinare, komai na perlourn ya dace da inda aka ajiyeshi,

K'ofar bedroom din ta zubawa idanu tana jiran taji fitowar sa amma shiru babu alamarsa, Shirun da taji yayi yawa ne, yasa ta mik'e ta nufi bedroom din zuciyarta na dukan uku uku, Da sallama ta shiga had'e da tura k'ofar bedroom din,

A hankali ya amsa sallamar ta yanda ba lallai mutum yaji ba indai ba bakinsa kake kallo ba,

Zaune yake akan makeken gadon sa k'irar Italian,

Sanye yake da wata farar Riga armless, se wani black jeans dake jikinsa,  Ya Khabeer  irin black beauty dinnan ne, fiskarsa a d'auke take da dogo hanci da kuma madaidaicin baki Wanda yayi daidai da tsarin halittar fiskarsa,

idanunsa Fararene sosai Wanda launin k'wayar idanunsa ta kasance golden colour,  dogo ne sosai ma'abocin kwarjini da kuma haiba, kallo d'aya zakayi masa ka fahimci Shi ba ma'abocin yawan magana bane,

A zaune yake ya mik'e dogayen k'afafunsa a kan wani Dan k'aramin table na glass, gefansa kuma laptop ce wadda ya  maida dukkan  hankalin sa akan laptop din, da 'alama wani Abu me mahimmanci yakeyi a ciki,

Shigowa tayi tareda dan, rissinawa tace, "ya khabeer, sanu da aiki
Dagowa yayi tareda zuba mata manyan idanunsa,

 jikinta ne ya fara rawa a lokaci guda,

"Tsawa ya daka mata, nan da nan ta ida firgicewa, sbda a rayuwar Umaisa ta tsani tsawa, fashewa tayi da kuka tareda toshe bakinta da d'aya hannun nata,

Cikin daga murya ya fara magana yace , "Umaisa Ashe baki da hankali Dan k'aniyan ki,? yau kwannan ki nawa rabonki da islamiya?

cikin sark'ewar murya tace "wllh..da...dama"

A fusace yace, " rufe min baki kafin na tashi na ballaki a nan gurin, nonsense kawai"

"Wllh kinji na rantse, dik ranar da na kumaji ance bakije islamiya ba, wllh sena karyaki"

Cikin kuka tace, " I'm so sorry ya khabeer insha Allah baran k'ara ba wllh!!

A taqaice yace, "is better for you,
And This is the last warning da zan sake yi miki, a kan makaranta," yana kaiwa nan ya Nuna mata hanya yace get out !,

Da gudu ta fita tana kuka, D'akinta ta koma tareda fad'awa kan mdaidaicin gadon ta, sannan ta saki wani irin kuka me cin rai, Seda tayi kukan me isarta sannan tayi shiru sbda ciwon da taji kanta ya fara, mik'ewa tayi taje ta kulle k'ofar d'akin da key sannan ta shige toilet danyin wanka,

Bata dauki lokaci me tsawo ba ta fito sbda wani irin ciwon da kanta yake mata , a daddafe ta daura alwalar sallar la'asar sannan ta fito,

Wata doguwar riga maroon me k'aramin hannu ta dakko ta sanya a jikinta, sannan tasa hijjabinta ta fara gabatar da sallar la'sar din,
Ta jima kafin ta idar , bayan ta idar ne ta shiga gabatar da tasbihinta data sabayi ko wace rana,

Tana kammalawa ta mik'e ta hau kan gadon ta, lamo tayi sannan wasu sababbin hawaye suka shiga bin kumatun ta,
Har akayi magrib bata fito ba, kasancewar Ummien su yaya Khabeer ce da girki, shiyasa babu Wanda ya nemi inda take,

Har Abba ya dawo babu Wanda yabi takan Umaisa hakan ne yasa ta k'ara fashewa da wani sabon kukan takaicin, abinda ya Khabeer din yayi mata, har akayi sallar ishsha bata fitoba,

Seda kowa ya hallara  a kan dining, tin daga kan yaya khabeer da yay Usman har zuwa kan yaya Farouq kowa yana nan amma banda Umaisa,

Mamin Umaisa ce ta sakko sanye cikin wani dakakken lace maroon colour, wanda aka yalwata dinkin da fararen christel stons masu matk'ar kyau gamida daukar idanu,  hannunta sanye cikin wani murd'add'en zobe na zinare, inada hannunta na dama yake Rik'e dana Ameeyra wadda takasance k'anwa  ga Umaisa,

A nitse take sakkowa daga kan step din tamkar wata wahainiya sabida k'asaita harta iso daining aria din,

Da fara'arta suka gaisa da Ummie da kuma mamah, sannan su Khabeer suka gaisheta suma cike da girmamawa,

Ba'a dad'e da zuwan Aunty amarya ba  Abba ya k'ara so falon shima,

Cikeda kulawa ya dubi kowa sannan suka Dan taba wasa da dariya kamar yanda ya sabayi da iyalan nasa kullum, sannan Ummie ta fara saving kowa dake dining din,

Kujerar da Umaisa take zama Abba ya kallah sannan ya ajiye spoon din dayake k'ok'arin kaiwa bakinsa yace, "ina Mamaba  ta shiga ne haka ban ganta ba?

Rumana ce tayi sauri tace, " Abba tana dakinta, tin dazu bata fito ba har yanzu  ina zaton ko bacci takeyi ne shiyasa, ta k'are maganar tana kallonsa,

Harararta Abbah yayi sannan ya kalli Khabeer dake shirin fara cin abinci yace" son jeka dubamin Ifyr  Mamana na, sabida banaso ta dinga zama ita kadai a daki haka,

Wani malolon takaici ne ya tsayawa  Khabeer a wuya, dan haka dak'yar ya iya hadiye abincin dake bakinsa sabida takaici, amma babu yanda ya iya dolansa yaje yazo da ita kamar yanda Abba yace masa,

Yana mik'ewa Aunty Amarya tace, "Haba Alhaji don Allah, senake ganin Umaisa fa ba yarinya bace balle ace se'an kirata sannan zata fito taci abinci , "idan taji yunwa ai dole ne ta fito ta nemi abinda zata saka a  cikinta,"

Wani kallo Abba ya dinga bin Mamie dashi hakan ne yasa tayi shiru taci gaba da cin abincin ta ba tareda ta k'arasa abinda tayi niyar fad'ar ba,

Ganin hakan ne yasa Khabeer ya nufi nakin Umaisa zuciyarsa na masa wani irin tafarfasa, Knocking din k'ofar ya shigayi,

tanaji amma tak'i budewa , hakanne ya k'ara fisatashi, cikin d'aga murya yace, "zaki bude k'ofar ko sena shigo na karya ki sannan zaki bude"?

Da wani irin gudu  ta diro daga kan gadon har tana tin tibe sabda tsoro, tabbas koda ace bata nunfashi taji muryar nan seta shaida mamallakinta balle kuma yanzu da take tareda numfashinta, Budewa tayi jikinta banda rawa babu abinda yakeyi, buguda k'ari kuma ga wani irin recing da heart dinta keyi,

Da gudu ta juya zatayi baya sabida ganin irin yanayin dake fuskar yayan nata, Cikin wani irin mugun zafin nama yasa dogon hannunsa ya wani irin fuzgota sabida haushinta dayakeji, tsayawa yayi cak sbda wani irin zafin dayaji jikinta yayi a lokaci guda,

Da wata irin kakkausar murya ya kalleta yace, " are you sick?"

D'aga masa kai tayi a hankali tace , "yeah"

Cikeda kulawa yace, " Kinsha magani ne?"

Girgiza masa kai  tayi, idanunta a cike tab da k'walla alamar 'a'a

A hankali ya rage sautun muryarsa alamar rarrashi yace,, "meyasa bakijin magana ne ke a Raywarki?"Kinga dazu ma kece kika sa nayi miki fada sbda bakisan zuwa makaran ta," kinsani kema bazamu taba shiryawa dake ba muddin bazaki canza wannan dabi'ar taki ba", ya fada yana dungure mata kai,

Janta yayi har suka k'arasa parlon batareda k'ara cewa komai ba, yana zuwa yace, "Abba gatanan,"

Hannu Abba ya mik'a mata alamar tazo gareshi, da gudu ta k'arasa inda yake sannan ta fada jikinsa tareda sakin wani irin kuka,

Cikin sigar tsokana Rumana tace, "babbar magana yaufa shagwabar ta motsa", ta fad'a tana k'unshe dariyar datakeyi sabida Abbah,

"hararar ta Mamah tayi sannan ta dauke kanta tareda Jan tsaki, Sabida yanda lamarin Umaisa yake matiqar bata haushi, amma babu dama tayi magana yanzu Abba seya rufeta da fada,

Sam Abba baya son lefin Umaisa kokad'an shiyasa take zuba iskancin shagwabarta San ranta ,

Ya Usman ne yayi k'arfin halin daka mata tsawa,

shiyasa ta hadiye kukan da takeyi babu shiri,

*WAI WAYE ABBAH NE*

Alhaji Mahmoud Muhammad shine cikakken sunan sa ,Shi haifaffen garin Gano ne, wadda take daya daga cikin k'auyikan kano, shikad'ai iyayensa suka haifa, dan haka suka d'auki son duniya suka d'ora masa, duk inda mahaifinsa malam muhammadu zashi to da Abba yake tafiya, tun mutane k'auyen suna gulmarsa har suka gaji suka dena, lokacin da wayewar ilimin boko ta shiga garin na Gano dayawa iyaye sun nuna rashin amincewarsu dashi, dan haka suka hana yaransu yi,

Lokacin da Malam Muhammadu ya samu wannan labrin murmushi kawai yayi, sannan ya kalli me d'akinsa *BINTA* wacce Abba yake kiranta da suna *Gwaggo* yace, " Binta nifa jikina yana bani cewar nan bada jimawaba wannan al'amarin da turawannan sukazo dashi nan gaba ze iya zama me amfani a rayuwar mu, "dan haka zan sanya *mamuda* (Abba) ya dinga zuwa,

Shiru gwaggo tayi kamar me tinanin wani abu sannan ta kalli mai gidan nata tace, " nidai malam bank'i ta naka ba, ammafa magana ta gaskiya idan naga d'abi'ar mamuda ta sauya tofa ze dena zuwa, sabida ni baza'a koyawa yarona yahudanci ba.!

Murmushi kawai malm Muhammadu yayi batareda ya sake cewa komai ba,

washe gari kuwa da sanyin safiya mlm ya kama hannun Mahmoud ya kaishi makarantar Boko, wannan shine mafarin karatunsa, kullum idan ya dawo yana bitar karatunsa a gida, se Gwaggo tayita fad'a kamar ta ari baki, wai ya cika mata kunne da sunan yahudawa mak'iya Allah, shidai malam sedai kawai yayi murmushi yana kallonsu

A haka Mahmoud ya samu nasarar kammala karatunsa tun daga kan primarynsa har zuwa scondry,

daga nan kuma yanwuce K.S.U.T dake Wudil, inda ya yayi dgree dinsa na farko akan abinda ya shafi kasuwanci, haka ya dinga lallab'a rayuwarsa har ya samu nasarar fara aiki a *FEDIRAL WORKS OF HOUSING* dake garin abuja,

Dukda cewar Alhaji Mahmoud muhammad girman K'auye ne sam hakan besa mahaifinsa ya matsa masa kan seyayi auren wuri ba, har seda ya himmata dan ra'ayin kansa sannan sukayi aure da matarsa ta farko *Hadiza,* wacce itace ta kasance mahaifiya ga *Khabeer* da kuma *Usman,* suna kiranta da Suna *Ummie*

bayan aurensa da Hadiza Abba be d'au wani lokaci me tsaho a tare da ita ba ya sake auren matarsa ta biyu wato *Marym,* wadda itace ta kasance mahaifiya ga *Umar Farooq* da kuma *Rumana,* suna kiranta da *Mamah,* tundaga lokacin Abba be sake k'ara aure ba seda ya d'auki lokaci me d'an tsaho kafin ya sake Auren matarsa ta uku wato *Badi'atou,* wadda itace mahaifiya ga *Umaisa* da kuma *Ameerah,* inda su Khabeer suke kiranta da *Aunty Amarya* Sabanin su Umaisa da suke kiranta da suna Mamie,

Bayan haihuwar Ameerah Allah yayiwa mahaifin Abba malam muhammadu rasuwa, sosai Abba yaji mutuwar mahaifin nasa, dan haka yayi kuka harya gode Allah, gwaggo ma tayi kuka tamkar ranta ze fita, daga k'arshe dai suka hak'ura suka dinga binsa da addu'ah.

Bayan wani lokci Abba ya nuna yana son tafiya da Gwaggo Abuja amma fir tak'i yarda wai bazata tafi tabar garinta na haihuwa ba, badan Abba yaso ba haka dan dole ya barta a nan d'in, sedai duk abinda takeso yanayi mata Shi, haka kuma idan anyi hutu yakan sa a kai mata yaransa gurin mahaifiyar tasa.

Kaf cikin yaran Alhaji Mahmoud Muhammad yafi son Umaisa fiyeda kowa, sabida sunan gwaggonsa ne da ita Fatimah, shiyasa suke kiranta da Umaisa

Dan haka baya son bacin ranta ko kad'an, kuma baya sassautawa dik Wanda ya tab'a masa ita koda kuwa waye shi, Shiyasa shagwabarta tayi yawa sosai, ta yanda kowa ma yi masa takeyi ,

Dukda yawan shagwabarta amma Sam hakan besa ta kasance me raina mutane ba, tana da respect sosai fiyeda duk zaton me karatu, bugu da k'ari kuma gata da son mutane, Itadai kawai ka barta da yawan shagwabar ta,

D'abi'ar Shagwabar ce ma tasa yayyen ta maza suke yawan  jin haushinta, gata da shegen nacin kuka,

Abindai bekai ayi masa kuka ba a gurinta abin kuka ne, shiyasa suke yawan fad'a da yayyen nata idan aka cire yaya Usman,  shikam yana son 'yar k'anwar tasa sosai, haka kuma yana ji da ita,

Wani irin mugun  kallo Abba ya jefa masa Dan haka ya hadiye bacin ransa cikin sauri, sabida gudun bacin ran Abban nasu,

Sbda takaici Khabeer mik'ewa yayi yabar falon gaba daya sbda idan yaci gaba da zama a gurin to tabbas fa ransa ne zeta baci a banza,

Comment
Nd
Share

*Zm muhmd (ChuBaDo)*😁

_*🎀KIYARDA DANI...!🎀*_
🎀🐾🎀

*♝ IϽTɵ||IƓɵϽT WrITɵr'ی  ASSɷ📚✍️*

*💫DEDICATED: to Sis naja'art*

_*WRITING BY: Zm (CHuBaDo)*_

*✨Special Gift for Hafsat Hafnan (my jika),.*

_Page:2_

________Daki ya koma a ransa yana mamakin hali irin na Umaisa, wani siririn tsaki yaja tareda firzar da wata iska me zafi, a hankali ya firta cewar dole ne inyi maganin yarinyar nan tin kafin lamarin ta ya ida lalacewa,  Laptop dinsa ya jawo  ya cigaba da aiyukan dake gaban sa,

Washe gari da sassafe Umaisa ta tashi kasancewar mamien tace da girki kuma gashi zataje

makaranta, A nitse ta mik'e ta nufi kitchen Dan ta temakawa Mamien da wani aikin kamar yanda ta saba, da sallama ta shiga kitchen D'in, A tsaye ta samu Mamie se aikace aikacen ta take, a nitse tace Mamie ina kwana ?
Ko kallonta Mamie batayi ba har Seda ta sake maimaita gaisuwar sannan mamie takalleta a A dak'ile tace, "lafy lau,

Jikin ta ne yayi bala'in sanyi sbda ko ba'a fad'a mata ba tasan mamien ta fishi takeyi da ita, nan da nan k'walla ta cika mata idanu, cikin muryar kuka ta bude baki tace, " pls Mamie i'm so sorry don All...!!,

Da sauri Mamie ta dakatar da ita ta hanyar daga mata hannu, tareda nuna mata k'ofar fita daga kitchine d'in alamar ta fita,

Bakinta na rawa tace, "Dan Allah Mamie kiyi haqur....

Bata bari ta k'arasa ba cikin d'aga murya tace, "I said get out right now!!!! ta fad'a cikin b'acin rai,

Da sauri ta fice sbda ta San halin Mamie bata da wasa yanzu setayi mata shegen dukan da setaji a jikinta, sabida ko kad'an bata tolerating shirman ta,

Daki ta koma tana ta faman sharar hawaye sekace wadda aka zane da bulala, sannan ta fara shirin tafiya School, Seda ta had'a komai na tafiya school din sannan ta fito falon sanye da uniform d'inta wanda sukayi mata bala'in kyau a jikinta,

Ya Usman ta samu da Rumana suna breakfast se kuma ya Farouq, kujerar daining ta fara k'ok'arin ja, se faman cika take tana batsewa ita a dole anb'ata mata rai, babu wanda ya tankata se Ya Usman dinta,

Dan haka ta k'ara turo baki gaba tana yarfe hannu cikeda tsantsar shagwab'a, Seda ta zauna sannan tabisu d'aya bayan d'aya ta gaishesu,

Ba yabo babu fallasa suka amsa mata , a gaggauce Farouq ya gama break din sannan ya dau brief case d'insa ya tafi office ya barsu,

Chips kawai ta zuba kad'an a flet, sannan tasa pride egg a gefe, A hankali ta shiga ci kamar anyi mata dole, har Seda Rumana ta kammala amma ita ko rabi ma bataci ba, Kallonta Rumana tayi sannan ta kalli agogo tace, "pls Umaisa u should be fast mana Dan Allah time fa yana tafiya,

Hararar ta Umaisa tayi sannan ta dauke kai tace," to so kike na tafi School d'in banyi breakfast ba?

Hararta ya Usman yayi sannan yace, dalla malama tashi ku tafi,

Mik'ewa tayi da sauri ta nufi k'ofa, hakan ne yasa Rumana ta k'yalk'yale da dariya, har suka shiga mota, Rumana bata dena dariyar da take ba
Hakanne ya k'ara tinzira Umaisa, se kawai ta fashe musu da kuka a motar tamkar Allah ya aikota,

Malam Musa drivern su dake kaisu makaran ta  ya juyo yana 'yar dariya yace, "haba Rumana. Ya zakisa 'yar gaban goshin Abba kuka irin haka ?

Dariya sosai Rumana tayi sannan tace, " ai  Malam Musa kabar  ta tayitayin kukan taga zata iya ne, kokuma ince hawayen ne sukayi mata yawa shiyasa,  wllh  kaima ka iya taya bera bari Malam Musa. Ta k'are maganar tana murmushi,

Dariya Malam musa yayi sannan ya kalli Umaisa da ta kifa kai da gwiwa tana ta aikin kuka yace, "yahaquri 'yar Abba rabu da ita kinji?

Dak'ar ya dinga lallaminta harya samu tayi shiru , suna zuwa school kamar jira take ta bude murfin motar ta fice ta bar Rumana a motar,

Rumana na shirin fita daga motar Malam Musa ya kalleta yace, " af Rumana dan Allah kuyi hak'uri na manta ban sanar da Alhaji cewar med'akina bata da lfy ba, shine nace bari in gayamiki cewar bazan samu damar zuwa d'aukarku ba sabida zan biya na kaita Asibiti,

Murmushi kawai Rumana tayi sannan tace, "lah babu komai Malam Musa kaje kawai, idan an tashi zamushiga texi kawai,

Murmushin jin dad'i yayi a ransa yana girmama halin kirki irin na yarinyar, kokad'an basuda d'agawa irin ta yaran musu kudi.

Har aka tashi daga school Umaisa bata kula Rumana ba, sbda a cewarta wai Rumana itace silar shouting din da yaya Usman yayi mata, har bakin class din su Umaisa Rumana tazo tace mata tazo su tafi gida amma fir Umaisa taki koda kallonta, hakan ne yasa Rumana tayi fishi tayi tafiyar ta tabar Umaisan a School d'in, dama kudin break dinta ta ajiye sabida su samu su tafi gida dashi tunda Mlm Musa yace baze samu damar dawowa d'aukarsu ba, sbda uzirin daya bata dazu,

Tana fita bakin Gate din School din ta samu me taxi  tace masa "Apo zaka kaini don Allah,

Kallonta me taxi d'in yayi sannan  yace, wani guri zakije a Apo?

A tak'aice tace, " Zone E zaka kaini cikin legislative Quaters,

Kallonta ya sakeyi a karo na biyu sannan  yace,  "shiga muje.

Shiga tayi ta zauna amma zuciyarta Sam babu dadi a kan abinda Umaisa tayi mata,
Tsaki tayi tareda zubawa titi idanu a ranta tace, "dik abida Umaisa takeyi wllh duk lefin Abba ne daya shagwaba haka, shiyasa take abinda taga dama
A haka suka qaraso cikin unguwar,  a nitse ta dinga nuna masa hanya har suka k'arasa bakin k'ofar gidan,

Kallonta me taxi din yayi sanna ya kalli gidan a ransa yace ikon Allah amma gidan nan ya hadu, haka kuma ya tsaru matiqa,

Kamar daga sama yaji tace, " Mlm nawa ne kudin ka?
Washe baki yayi sanna yace nera dubu zaki bayar,
Dubu 2 ta dakko sabbi dal a jakar ta ta mik'a masa  sannan ta juya,

Da sauri yace k'anwa  dubud'ya fa nace miki ba 2 ba?
Juyowa tayi sannan ta sakar mai murmushi tace kaje na baka kyau ta ,
Godiya yayi mata sannan yaja motar  ita kuma ta shige gida,
A parlor ta samu su Ummie sunata hira, se kuma Ameerah dake ta faman wasa da Teddy's din dake gaban ta, Da sallama ta k'arasa parlon sannan ta zube akan d'aya daga cikin kujerun perlourn tareda fadin, "wash wllh nagaji sosai,

Murmushi mamah tayi sannan tace, " ai dole kicewa mutane kin gaji mana tinda garin Abuja gaba d'aya kika zagaye,
Dariya sukayi gaba daya , sannan ta gaishesu ta mik'e donta wuce dakinta,

Ummie ce tace, "Rumana ina kika bar Umaisa ne?

Tsaya tayi sannan ta labarta musu yanda sukayi da ita a makaranta sannan ta wuce  daki abinta,

Sosai abin yayiwa Mamie ciwo a ranta ta dan haka ta dinga k'isma irin dukan da zata yiwa Umaisa idan ta dawo,

A makaranta kuwa Umaisa na Zaune a kan sit dinta ta kifa kanta a kan jakarta se sharbar kuka take ,
K'awarta Nusaiba Hashim ce ta hangota Dan haka da sauri ta nufeta,  d'agota tayi lokaci guda ta shiga  tambayarta abinda ya sameta take kuka,

Cikin kuka umaisa ta fara labarta mata komai tin daga fad'an da ya Usman yayi mata har zuwa dariyar da Rumana ta dingayi  mata,

Wani irin kallo nusaiba ke bin Umaisa dashi, wanda yafi kama Dana takaici sannan  tace,

"yanzu ke Umaisa sbda Allah dan anyi miki fad'a shine zaki zauna ki b'are baki kiyita kuka ? Haba Umaisa yaka mata fa ki fahimci cewr kefa yanzu ba yarinya bace kin girma, komai naki kuka da abinda ya isa da Wanda ma be isa ba kuka?

haba Dan Allah, ai dole ne ki dinga bawa kowa haushi , wllh da a gidan mu kike inajin sekin hadiyi zuciya kin mutu sbda tsawar da zaki dinga sha a gurin yaya Khalil d'in mu sbda komai nasa fad'a ne, "amma kuma he is very social and nice, ta fad'a fiskarta dauke da murmushi Shiru. Umaisa tayi tana kallonta se kuma ta sunkuyar da kanta k'asa tana tinanin yanda za'ayi ta tafi gida,
Wayar Nusaiba ce ta fara ruri Dan haka da sauri ta d'aga tana dariya tace, "yaya wllh harna gaji da jiranka,

murmushi yayi sannan yace, "i'm sorry Lil sis ai gani ma nazo,

Dafa Umaisa tayi sannan tace, "taso mutafi se mu ajiyeki a gida tinda hanya ne
Da sauri ta mik'e kamar jira take suka fita daga Class din zuwa inda Khalil yayi parking motarsa.

Suna zuwa nusy ta bud'ewa Umaisa bayan motar ta shiga ta zauna sannan ita kuma ta bude front sit din ta shiga ta zauna,
Da murmushi akan fuskarta tace "yaya wllh harna kusa bushewa,

dariya yayi sannan yace Aida kin bushe din ma daya fi dariya sukayi gaba daya , sannan Umaisa ta gaisheshi cikin girmamawa,

Da sakin fiska ya amsa mata sannan yace kece Asha ko?
Da mamaki ta d'ago ta kalleshi a karo na farko tinda ta shiga motar, cikn sa'a kuwa suka had'a ido da ita , kasa d'auke idonta tayi daga barin kallonsa sbda ganin irin launin k'wayar idonsa ,
*(JANAF da qoqari😂 )*

mamaki ta dingayi a ranta tace "dama a kwai masu irin idon nan a qasar Nigeria?

Katseta yayi ta hanyar cewa "Lil sis ba wannan bace Aysha ?

Dariya Nusaiba tayi sannan tace "ba ita bace bafa yaya , wannan sunan ta daga U ya fara,

Hannunsa d'aya ya d'ora a kansa kamar me tinani wani abu sannan yace, "to nama San sunan ta,

Da mamaki sukace to fadi muji idan ka sani,
Murmushi yayi sannan yace sunan ta Ummi ne,
Dariya suka dinga yi masa
sannan Umaisa tace " niba Ummi bane sunana, ni sunana *Umaisa Muhammad Mahmoud,* kokuma kace *Fatimah.*

idonsa yad'an zaro kad'an sannan yace "wow nice name Umaisah,

Dariya tayi sannan tace "to kaifa ya sunan ka ?

Shiru ya danyi sannan ya saki wani k'aya taccen murmushi yace *"Khalil Nasir Abdullah*

Dariya tayi sannan tace nice to meet you ya Khalil
Amma ya naji sunan Abbanku ba d'ayaba da Nusaiba? kuma amma naji tace min kai yayanta ne,

Dariya tambayar ta bashi har seda fararen haqoransa suka fito, sannan yace "ae ni yayanta ne amma kuma baban mu ba daya ba,

Cikeda rashin fahimta tace "ban gane ba
Dariya Nusaiba tayi sannan tace ke cousin d'ina ne fa , se'a sannan Umaisa ta tsagaita masa da yawan tambayoyin ta
,
Hira suka dingayi kamar sun dad'e da Sanin juna , a ranta tace "dama haka su yaya khabeer suke Dana ji dadi,
Seda suka kaita har qofar gida, sannan suka kama hanyar nasu gidan dake Gaduwa Estate.

Qofar gate din ta tura zuciyarta fess babu fargabar komai ta shige gida ,
Takoyi sa'a babu kowa a falon Dan haka ta nufi dakinta,
Uniform din ta cire sannan ta shiga toilet tayi wanka,

seda ta d'au lokaci sannan ta fito, wasu Riga da wando ta d'kko Na Pakistan masu launin blue black ta sanya a jikin ta,

masha Allah kayan sunyi matiqar yi mata kyau kasancewar ta doguwa kuma fara,

Dining aria ta nufa ta cika cikinta sannan ta mik'e ta nufi d'akin mamie,

Comment
Nd
Share

*Zm muhmd*
*(ChuBaDo)*😁

_*🎀KIYARDA DANI...!🎀*_
🎀🐾🎀

*♝ IᗪTEᏞᏞIGEᗪT WᏒITEᏒ'ی ASSω📚✍️*

*💫DEDICATED: to Sis naja'art*

_*WRITING BY: Zm (CHuBaDo)*_

*✨Special Gift for Hafsat Hafnan (my jika),.*

_Page: 3_

____________ A hanali take hawa kan step d'in kamar wata mara gaskiya, cikeda tsoro ta murd'a handile din dake jikin k'ofar ta shiga d'akin tareda yin sallama duk a lokaci guda, a zaune ta samu mamie tana sanyawa Ameerah kayah,

Daga d'an nesa kad'an take kallon mamien kamar zatayi kuka tace, "mamie i'm sorry dan plssss.. Ta wani ja pls d'in cikeda marairaicewa, kokallonta Mamie batayi ba balle ma tasa ran zata kulata, har Mamie ta gama shirya Ameerah Umaisa na tsaye bata motasa ba, mik'ewa Mamie tayi tareda jan hannun Ameerah dake rike Bobo tana k'ok'arin budewa, da sauri Umaisa ta Rik'e hannunn Mamie tana kuka har da yarfe hannu, wani irin takaici ne ya cika zuciyar Mamie , dan haka ta fusgota a fisace tayi cikin d'akin da ita, wayar dake jikin hand drayer d'inta ta fizge cikeda b'acin rai tayi kanta da ita, sosai Mamie ta duka tsula mata wayar a jikinta, bakajin komai a d'akin banda ihun Umaisa,

Ummie ce ta shigi d'akin da saurinta, sabida jin ihun nata, Salati Ummie ta saki cikeda tsoro sabida ganin irin dukan da Mamien takeyiwa Umaisan, da sauri tasa hannu ta fisge wayar tana bin Mamie da wani irin kalo wanda yafi kamada na mamki sannan tace, " Amma wllh kin bani mamaki Badi'atou..!!, "yanzu fisabilillahi yarinya kamar wannan budurwa zaki saka a gaba kina duka da wannan murtikekiyar wayar kamar zaki kasheta? Angaya miki fishi haukane? Yanzu da kika sata a gaba kina duka me hakan ze canza iye?

A hankali Ummie ta dafa mamie sannan ta sassauta murya tace, " idan rai ya b'aci sam be kamata hankalin mu ya gushe ba Badi'atou! Komai na Rayuwa yana da iyaka, kedai kawai kici gaba dayi mata addu'ah insha Allahu komai zeyi daidai kinji? Ta fad'a tareda zaunar da mamien a bakin gadon dake d'akin,

Cikeda takaici mamie ta kalli Ummie tace, "har zuwa wani lokaci za'a d'auka a haka sabida

Allah? Wllh Allah shikad'ai yasan halinda zuciyata take shiga a kan wannan yarinyar!! Babban abinda yafi komai tsayamin a raina shine yanda Alhaji yabi ya sangartata, kokad'an baya la'akari da cewar ita mace ne kuma gidan wani zata nan gaba.

Murmushi Ummie tayi sannan tace," lallai Badi'atou kina mantawa da Alhaji indai akan 'ya'yansa ne, lokacin da ina goyom Khabeer wllh ya dingayi akansa, kokad'an baya son a tsawatar masa balle kuma ace za'a dakeshi, sekace a kansa aka fara haihuwar yara, danaga abin ya isheni se kawai na dage dayiwa yaron Addu'ah duk da cewa ma bashida wata k'iriniya,

Murmushi Mamie tayi har seda hak'oranta suka fito sanna ta girgiza kai, se'a sannan Mamah ta shigo tana gyara d'aurin d'an kwalin dake kanta....

Sankin baki tayi tana bin Mamie da kallon mamaki sannan tace, "yanzu Badi'atou seda kika daki yarinyar nan sabida Allah? Ta fad'a tareda maida kallonta ga Umaisa daketa faman sharb'ar kuka kamar zata hadiye ranta.

A nitse ta k'arasa inda Umaisan ke dunk'ule tana aikin kuka tace, " maganinki kenan ai ba kin iya Rashin jin magana ba, maza tashi ki wuce d'akinki kiyi wanka, sannan kisha pracetamol ki kwanta ki huta 'yar k'wal uba.

Da sauri ta mik'e tareda ficewa daga d'akin tana sharar hawaye, a hankali take sakkowa daga kan step d'in harta gaba sakkowa. A perlourn k'asa sukaci karo da Ya Usman d'inta ya dawo daga office,

Tsayawa tayi tana kallonsa lokaci guda kuma ta saki wani irin kuka tana yarfe hannu, Da sauri ya ajiye brief case d'in dake hannunsa a kan d'aya daga cikin Royal chiars d'in dake perlourn ya nufeta da wani irin mugun sauri, hannun ya kama da sauri yana dubawa, shatin bulala ya gani kwance a jikin farar fatar jikinta, nanda nan ransa yay masifar b'aci, cikeda fishi yace," who did this to you? Ya fad'a yana wani irin huci kamar macici.

Cikin kuka tace "Mamie ne wai da ban dawo gida tareda Rumana ba, kuma wllh yaya laifi Ruman d'in tayi min shiyasa nak'i yarda na biyota na taho ni kad'ai, ya fad'a tareda k'ara sautin kukanta,

Hannunta yaja suka koma saman, murd'a handile d'in kofar yayi, bisa ga mamakinsa seyaga duk iyayen nasu suna d'akin Mamie, kallonsa Mamie tayi sannan ta d'aure fuska tace " Ify kuka shigomin d'aki babu sallama, kodai zuwa kayi ka Rama mata ne?

Da sauri yace "A'a Mamie ba haka bane kawai dai naga kamar dukan yayima jikinta yawa ne, kumafa idan Abba ya dawo ya gani wllh Mamie zeyi fad'a. Wani d'an isakan kallo suka watsa masa a tare d'yansu, tun kafin suyi magana yaja hannunta suka bar d'akin da sauri, basu tsaya a ko ina ba se'a perlourn k'asa, zaunar da ita yayi a gefansa, sannan ya hawo jakar daya dawo da ita ya bud'e, kwalin sneeker's ya d'akko ya mik'a mata, sannan yace " oya jeki d'aki ki b'oye

nakine ke kad'ai na siyo miki.

Karb'a tayi lokaci guda ta washe baki tace " thank ya Usman, sannan mik'e ta nufi hanyar room d'inta harda tsallen murna, sekace ba ita bace wadda ta gama gurzar kuka ba.

_Comment_
_Nd_
_Share_

*Zm muhmd*
*(CHuBaDo)*😁

_*🎀KIYARDA DANI...!🎀*_
🎀🐾🎀

*♝ IᎠTҼllIǤҼᎠT WrITҼr'ی ASSϖ📚✍️*

*💫DEDICATED: to Sis naja'art*

_*WRITING BY: Zm (CHuBaDo)*_

*✨Special Gift for Hafsat Hafnan (my jika),.*

_Dan girman Allah masu bina prvt suna cewa in canza akalar labarina pls kuyi haquri, sabida bazan iya canza tsarin labarina ba, idan kinga hakan be miki na dan Allah ki barmin littafina babu dole🤷‍♀️_

_Afwan yau page din bashida tsaho, banida caji ne😊_

_Page:4_

_____________Tana shiga d'akin kan gadonta ta fad'a tareda d'aukar tellphone d'in dake gefan gadonta ta shiga kiran wayar Abbanta,

Abbah dake zaune bisa kujerarsa ta office, yayi nisa cikin nazarin takardun dake zube a gabansa, yaji wayarsa dake gefansa ta fara k'ara, murmushi yayi tareda mayarda hankalinsa kan wayar , amsawa yayi tareda yin sallama, murmushi Umaisa tayi sannan ta amsa

sallamar Abban nata tace "Abbaba ya office?

Da kulawa Abba yace " office Alhamdulillah my daughter ya gajiyar school?

Shiru tayi tareda yin narai narai da ido kamar zatayi kuka tace "pls Abbana ka dawo da wuri yau don Allah..!! Ta fad'a tareda fashewa da wani irin kuka,! gigicewa Abba yayi lokaci guda tareda da fad'in " Doughter meya sameki haka kike kuka? Waya tab'amin ke?

Sassauta kukan tayi sannan tace" ba kowa Abba kawai ina missing naka ne Abbana!

Rarrashinta Abbah ya dingayi sannan ya samu tayi shiru, seda ya tabbatar ta dena kukan sannan ya kashe wayar murmushi kwance a kan fiskarsa yace, "huh doughter sarkin Rigima.

Tunda ya khabeer ya fita da sanyin safiya, be dawo gida ba har yamma ta kawo kai, abin mamaki har ya Farouk ya dawo amma shiru Khabeer be dawo ba, shirun da Ummie taga yayi yawane yasa ta fara k'ok'arin kiran wayarsa dan taji ko Ify, hakanne yayi daidai da da shigowar Khabeer d'in, cikeda damuwa Ummie ta kalleshi tace "Babana Ify kuwa yau najika shiru?

Murmushi yayi sannan yace " Ummie wllh aiki ne yayi min yawa a Hospital shiyasa ban dawo da wuri ba, ya fad'a yana kwance agogon fatar dake d'aure a tsintsiyar hannunsa, murmushi Ummie tayi tareda shafa kan d'an nata cikeda soyayya tace " masha Allah son Allah ubangiji yayi jagora maza ka k'arasa side d'inka kayi wanka ka huta zansa Ruman ta kawo maka abinci, tab'e baki yayi sannan yace "no Ummie ba saita kawo ba ma naci abinci a office, ya fad'a tareda mik'wa yabar perlourn. Murmushi kawai Ummie tayi tareda girgiza kai.

*GARIN KADUNA, ANGUWAN RIMI.*

*Hajiya Murja* ce a zaune bisa k'ayataccen perlournta, wanda aka k'awatashi da dukkan kayan alatu na alfarma sanye take cikin wata dakakkiyar shadda gizna, anyi mata irin d'inki sinigalist wanda yay matik'ar karbar jikinta, hannayensa sanye suke cikin wani murd'add'en warwarayen zunare wayanda suketa d'aukar idanu,,

gefanta wata siririyar Matace wadda ake kiranta da suna, *Hajiya Binta 'yar kwabo* hajiya Binta 'yar kwabo aminiyar Hajiya murja ce sosai tun suna 'yan mata suke tare, Auren da Hajiya Murja tayine ya fara gina musu gatanga a tsakaninsu, lokacin da Hajiya Murja ta auri *Alhaji Nasir Lamid'o* wannan shine dalilin dayasa Hajiya Murja tabar Unguwar kusfa dake Zaria, aka kaita gidan mijinta dake Kaduna,

Duk da haka Amintar tasu bata Rabuba, musamman ma da Binta ta k'yalla ido taga irin tarin dukiyar da mijin Aminiyar tata yake dashi, kullum Binta 'yar kwabo tana tafe a hanyar Kaduna, ko tsoron titi ma ba tayi, yanzu da abin yay tsamari ma Hajiya Binta kwaso kayanta tayi gaba d'aya daga Zaria ta koma Kaduna gidan Alhaji Nasir Lamid'o da zama,

Bayan ta dawo Kaduna da kwana sati biyu Alhaji Nasir Lamid'o ya dawo daga London, koda yayi arba da Hajiya Binta sosai ransa ya b'aci da ganin ta a cikin gidansa , dan haka ya kira Hajiya Murja yace "maza maza ki gaya mata ta tattara komatsanta ta barmin gidana, dan wllh bazan amince da zaman wannnan matar a gidanan ba..!

Sosai Hajiya Murja ta tada fitina  a gidan kan cewar wllh Binta babu inda zataje, idan kuwa ya sake cewa Binta tabar masa gidansa to wllh sedai su tattara su tafi tare,  wannan Shine dalilin dayasa Alhaji Nasir Lamid'o ya haqura ya zuba musu ido,

Alhaji Naseer Lamid'o shahararren d'an kasuwa ne, wanda yayi fice a fanin kasuwanci daban daban, shiyasa ya mallaki kamfanoni da dama, tun daga kan kamfanin takalma har zuwa kamfanin k'erek'eran ababan hawa daban daban. Duk wannan tarin dukiyar da Alhaji Naseer Lamid'o yake da ita, yara biyu Allah ya bashi  a cikin wannan duniyar, Babban Shine ake kira da Maheer k'aramin kuma Abdussalam, suna kiransa da suna Abdul.

Maheer kyakkyawa ne ajin farko duk inda namiji me kyau da cikar halitta yake gamida cikar zati yakai tofa Maheer ya wuce nan,  fiskarsa a zagaye take wadda a turance ake mata lak'abi da (Roud face) yana d'auke  da manyan idanu ma'abota haske gamida d'aukar hankali,

Maheer  ba ma'abocin magana bane, haka kuma bashida sakin fuska ko kad'an, idan har kaga dariyarsa toda k'aninsa  Abdul ne.

Maheer yanada wata irin d'abi'a wacce a yanzu ta zame masa jiki dukda kasancewarta bame kyau ba, wannan dabi'a bata komai bace ta shaye shaye,  kai duk wani nau'i na abin maye maheer yana shansa, musamman idan ransa ya b'aci,   sedai duk irin shaye shayen da maheer yakeyi abin mamakin Shine baya neman mata ko kad'an,

Babban abinda ze bawa me karatu mamaki Shine,  a Rayuwar Maheer ya tsani mata, sabida a cewarsa wai gaba d'aya mata 'yan bin zak'i ne, haka kuma duk tinaninsu  d'ya ne,  suna da son kansu sosai, mace guda d'ayace a Rayuwarsa wadda ze iya fada'ar alkhairin ta....

Maheer yana da zafin Rai sosai gamida Rashin son Raini,   siyasa gaba d'ya basa shiri da matar mahaifinsa wato Hajiya Murja, ya tsaneta matik'ar tsana shiyasa ma take bala'in shakkarsa

Tofa wannan Shine Maheer Lamid'o yaro d'an gata me matik'ar jida kudi gamida Izzah.

*CIGABAN LABARI*

Hajiya Binta ta kalli Hajiya Murja tace " k'awata wllh wannan tak'adirin d'an naki ni tsoro ma yake bani, shege d'azu saura kad'an ya bangajeni, ni wllh gani ma nake anya kuwa ze barki ki ida nufinki a kan Mahaifinsa?

_Comment_
_Nd_
_Share_

*Zm muhmd*
*(CHuBaD'o)*😁

_*🎀KIYARDA DANI...!🎀*_
🎀🐾🎀

*♝ IDTellIGeDT WrITer'ی ASSѡ📚✍️*

*💫DEDICATED: to Sis naja'art*

_*WRITING BY: Zm (CHuBaDo)*_

*✨Special Gift for Hafsat Hafnan (my jika),.*

_Page: 5_

__________Cikeda damuwa Hajiya Murja tace "wllh kedai bari kawai, nikaina shegeb yaronnan ya gama tsayamin a Rai d'an iska!  ni abinda yafi damuna ma wllh baya tsoron uban kowa, idanfa yace zeyi abu wllh ko ubansa be isa ya hanashi ba, balle kuma ni karan kad'a miya, ta fad'a tana kallon idon binta 'yar kwabo.

Wata uwar harara Binta ta watsawa k'awar tata sannan tace "Amma wllh  kin ban kunya da har kika bari al'amarin Maheer ya tsaya miki a Rai haka batareda kin d'auki wani babban mataki a kansa ba, kinga malama kawai kud'i zaki fito dashi a tura Osun state gurin bokan mu yayi mana aiki akan Shege, kamar yanda yayi mana a kan Ubansa,  tayanda zamu dinga juyashi a tafin hannun mu se yanda mukayi dashi, kinga ai shikenan kin huta da taurin kansa.

Dariya sukayi gaba d'ayansu tareda tafawa,

K'ofar perlourn aka bud'e  dan haka suka maida hankalinsu gaba d'aya akan k'ofar perlourn, Maheer ne ya shigo perlourn cikin takunsa na isa da izzah,  sanye yake cikin wata rantsatsiyar suite wacce ta baiyana ainihin cikar zatinsa gamida haibarsa,  ko kallon inda suke beyiba ya nufi hanyar dazata kaishi d'akin Abdul, gaba d'yansu da ido suka bishi cikeda rashin sanin abin

cewa,

A nitse ya tura k'ofar d'akin tareda kunna kai ciki,  a kwance ya samu Abdul d'in dan haka ya k'arasa kan gadon da sauri ya d'agoshi yana tattab'a jikinsa, yanda yaji jikinsa yayi zafi ne yasa ya fahimci cewar Abdul d'in bashida Ify,  d'agoshi yayi sosai tayanda har suna iya jin numfashin juna, cikin husky voice d'insa yace"  whats wrong with you Dear re you sick?

Ya jefa masa tambayar cikeda kid'imewa, sabida a Rayuwar maheer ya tsani abinda ze taba masa brothern sa,  tun suna yara ma balle yanzu da suka girma,

Abincin dake cikin flacks Abdul ya nuna masa dan haka da sauri Maheer ya sakeshi  ya koma gurin flacks din dan ganin meye a ciki, yana bud'ewa ya kafe abincin da ido yana nazarinsa, spoon ya d'auka yad'an d'ebi abincin ya zuba a bakinsa,  lokaci guda ya furzar da abincin sabida wani masifaffen yaji daya gauraye bakinsa, nan da nan idanunsa suka canza launi, cikeda bacin Rai ya dauki flacks din ya nufi kitchine dashi, cikeda bala'i ya fara kwad'awa masu aikin gidan kira,  kafin kace me harsun taru a gabansa, a matik'ar hasale yace "uban waye ya dafa wannan abincin a cikin ku?  Cikeda fargaba gamida tsoro Zaliha tace" nice ranka ya dad'e dama hajiya ce tace a dafa mata sannan kuma asa yaji sosai,

A fisace ya koma perlourn yana binsu da wani irin d'an iskan kallo irin na Rik'ak'kun mazan nan yace" malam daga yau karki kuskura kisake sawa a kaiwa Abdul Abinci, idan kuma kika sake wllh zanyi abinda bana so. Yana kaiwa nan ya juya yabar perlourn zuciyarsa nayi masa zafi,

Wannan shine abinda yake faruwa a gidan Alhaji Nasir Lamid'o.

*********

A gidan Alhaji Mahmoud muhammad kuwa, tin wajen k'arfe 4:00pm na yamma Mamie ta shiga kitchine dan gabatar da aiyukan dake gabanta, kasancewar duk Ranar litinin Abbah yakanyi Azumi, shiyasa abin ya zame masa jiki,

Fride Rice Mamie take sonyi dan haka ta fito da duk kayan dazata buk'ata,  inda Rumana take temaka mata wajen wanke kayan lambun da mamien ta fito dasu,

gefe kuma Umaisa ce zaune bisa wata k'aramar kujerar Roba tana had'a coslow wanda yaji k'wai da kuma Bama,  cikin mintuna kad'an ta kammala had'awa sannan ta mik'e ta nufi babban prizern  dake kitchin d'in,

bud'ewa tayi sannan ta d'akko manya manyan kaji guda 3, ta nufi sink dasu,  wani madaidaicin kwanon silver ta d'akko ta zuba kajin a ciki, sannan ta sakar musu ruwa sabida k'ank'arar dake jikin kajin ta saki.   Seda ta tabbatar k'ank'arar ta saki sannan ta shiga wanke naman,  seda ta wanke shi tas sannan ta zuba a tukunya,  seda ta hada komai tin daga kan kayan k'amshi har zuwa kansu magi sannan ta d'ora a kan gas.

Cikin mintuna kad'an suka kammala aikin dake gabansu,  Mamie ce ta kalli Rumana tace " Ruman ki had'awa Abban ku pepe soup d'in kayan ciki sabida naga yana sonsa sosai.

Da sauri Umaisa tace " Mamie aina riga nayi masa tun d'azu kinga ma harna kaimasa shi kan daining.

Batareda da Mamien ta kalleta ba tace " Da kyau  tunda an gama komai se ku tashi kuje ku kai abincin kan daining d'in sabida magrib ta kawo kai, ana idar da sallah zakuga yayyenku sun dawo masallaci,

Ameerah ce ta shigo kitchine d'in hannunta Rik'e da Nutri milk duk tabi ta b'ata jikinta dashi, dariya Rumana tayi  sannan ta kama hannun Ameeran tace "hy sweetheart waya baki Nutri milk kika b'ata jikin ki dashi haka?

Se'a sannan mamie takai kallonta ga Ameerah, salati Mamie ta saki sannan tace " oh Allah na ni badi'atou wllh Ameerah lamarinki se ke wllh, dubi fa yanda kikayi da jikinki, ta fad'a tana nuna jikin amiran,

Washe baki Ameerah tayi  cikin kwab'abb'iyar hausanta tace " ya Faluk ne a bani kuma cinga hadda sweet abani, ta fad'a tareda nuna musu jakar Big Bom d'in dake hannunta.

Da sauri Umaisa tace " Rabin Rai zoki bani guda d'aya kinji?    Mak'e kafad'a Ameerah tayi sannan  tace "uhmm an baci ba, ni Aunty Ruman jan bawa.

Dariya sukayi gaba d'ayansu sabida yanda Ameeran take magana.  Fita Mamie tayi daga kitchine d'in  ta nufi Room d'in ta danyi wanka sannan tayi Sallah. Mamie na fita Ameerah ma ta nufi hanyar fita, tana ganin Umaisa ta mik'e aiko ta k'arasa ficewa da gudun ta, a zatonta alawar Umaisan zata karb'ar mata.

Dariya sosai tabawa Umaisa dan haka sukai Murmushi kawai sunabin hanyar data fita da kallo, mayan womers d'in da mamie ta zuba abincin suka dinga diba suna kaiwa daining, seda suka jera komai sannan ko wacce ta wuce Room d'in ta danyi wanka da kuma sallah,

Farouq da Usman ne suka fito cikin sauri don tafiya masallaci, sanye suke cikin jallabiyar su k'irar Emrati,  sedai banbancin colour kawai,  inda Farouq tasa ta kasance maroon shi kuma Usman tasa milk colour ce,  tafiya suke suna d'an tab'a hira a tsakaninsu,  Usman ne ya kalli Farouq yace" kai nifa yau kwatakwata ban sanya Goldeen a idona ba sam, dayake sunan da suke kiran khabeer dashi,

Batareda Farouq d'in ya kalli  Usman d'in baa yace "wllh bana ce ba ni kaina Rabona dashi  tin safe, kasan yanayin aikin nasa ne se'a hankali.

Suna cikin hirar ne suka hangi Khabeer d'in da Abba sun shiga masallaci, Murmushi sukayi a tare sannan suka mara masu baya zuwa cikin masallacin suma,

bayan an idar da sallar da jimawa sannan Zaratan mazan suka fito ko wanne da Murmushi akan kyakkyawar fuskarsa, kafad'unsu Abba ya dafa inda suka sanyashi a tsakiya cikeda tsantsar k'aunar mahaifin nasu sannan suka nufi hanyar gida,

Tun kafin su shigo gidan k'amshin turaren wuta ya bugi hancinan su, Murmushi Usman yayi sannan yace " wannan dagaji aikin Aunty Amarya ne, a haka suka shigo gidan fuskokinsu cikeda annuri,

Da sallama suka shg perlourn, da sakin fuska iyayen nasu suka amsa musu sallamar, daining d'in suka nufa sannan kowa yaja kujerar ya zauna, Rumana ce ta fara fitowa sannan Umaisa ta fito, sanye take cikin wata farar riga me fogon hannu, se kuma street siket baki, wanda yay bal'in karban jikinta,

A haka ta k'araso perlourn fuskarta d'aukeda Murmushi sabida ganin Abban ta, da sauri ta k'arasa kusa dashi tace Abba sannu da shan Ruwa, cikeda kulawa Abba yace "yauwa my precious daughter, washe baki tayi sannan tace Abbana nayi maka special pepe soup d'inan kayan cikin nan da kake so,

Murmushin jin dad'i Abba yayi sannan yace " ngde sosai diyar albarka Allah dai ya baku miji na gari nayi muku Aure, rufe fuskarta tayi da zarazaran hannanyenta cikeda jin kunya,

Dariya gaba d'aya sukayi amma banda golden daya k'ara had'e girar sama da k'asa, sabida shi ya tsani yawan surutu a rayuwarsa,

Kallonta Usman yayi sannan yace " to malama pepe soup, dan Allah ki rabu da Abba haka yasha ruwa, ya k'are maganar yana dariya, chuno masa baki tayi sannan tace "uhm aidai Abbana ne dai ko,

Dariya Abba da Rumana sukayi sannan ta shiga serving d'in kowa dake daining d'in, sannan ta zuba nata ta faraci, bata wani ci sosai ba ta mik'e tareda yiwa kowa sallama ta wuce Room nata sabida tana so ta sakeyin nazari akan littattafanta na makaranta....

_Comment_
_Nd_
_Share_

*Zm Muhmd* *(CHuBaD'o)😁*

_*🎀KIYARDA DANI...!🎀*_
🎀🐾🎀

*♝ IDTєℓℓIGєDT WяITєя'ى ASSϖ📚✍️*

*💫DEDICATED: to Sis naja'art*

_*WRITING BY: Zm (CHuBaDo)*_

*✨Special Gift for Hafsat Hafnan (my jika),.*

_Page:6_

____________📖 duk wannan budurin da Umaisa takeyi ko kad'an hakan besa khabeer ya kalli inda take ba, hasalima harkan gabansa kawai yakeyi, ita kanta Umaisan kusan hakan ya zame mata jiki, tun abin yana tsaya mata a rai har ya dena tsaya mata, a haka iyalan suka kammala Deenar d'in tasu zuciyar kowa a cike da tarin farin ciki,

B'angaran Gidan Alhaji Nasir Lamid'o kuwa, sosai Ran hajiya Murja ya b'aci bisaga abinda maheer yayi mata akan Abdul, hakanne yasa ta mik'e a fisace ta nufi Room d'inta, cikin mintunan da bazasu gaza 30 ba ta dawo perlourn hannunta d'auke da bunch d'in dubu dari ta wurgawa Binta 'yar kwabo tace "gashinan inaso ki turawa Adebayo kud'innan yanzu, sannan ki shaida masa abinda ya dace yayi akan wannan d'an iskan dayake shiga rayuwata, koma me zeyi yayi Alhaji ya kori Maheer da kansa yabar gidannan, kuma tafiya ta har abada,,,!! " murmushin mugunta Binta 'yar kwabo tayi sannan tace" angama K'awata dan haka kawai kijirani kawai kiga me zanyi a kai, daga yanzu zuwa gobe, ta k'are maganar tana murmushi irin na marasa imanin nan,

Koda Maheer yabar d'akin Direct Room d'in Abdul ya koma, taimakawa Abdul d'in yayi ya canza kayan dake jikinsa, sannan suka fito dan zuwa Hospital, a perlour suka wuce su Hajiya Murja wacce keta faman cika tana batsewa, ko kallonta beyi ba ya kama hannun k'anin nasa suka fice daga parlourn,

Parking lot suka nufa inda Maheer d'in ya nufi wata had'ad'd'iyar bak'ar venz me shegen kyau, a nitse ya bud'ewa Abdul d'in front sit, sannan ya koma mazaunin driver, a hankali yayiwa motar key cike da nutsuwa lokaci guda kuma ya nufi get cikeda k'warewa, horn ya saki me lafiya, da sauri malam Haruna ya taso ya wangale masa get d'in shikuna ya danna hancin motar zuwa kan titi, a nitse yake tukun sabida Abdul, jefi jefi yakan yakan kalli k'anin nasa cikeda tausayin yaron, a hankali wata irin tsanar matar uban nasa ta dinga ratsa masa zuciya,

tabbas dole ne ya d'auki tsatstsauran mataki akan wannan matar, jira yake kawai Dady ya dawo daga Yola, inyaso se'ai wacce za'ayi a gabansa,,,, wani siririn tsaki yaja hakanne yayi daidai da isowarsu wani babban asibitin kud'i dake cikin Anguwan Rimin,  perking yayi sannan suka fito daga motar, hannunsa Abdul ya Rik'e kamar ze sakin masa kuka yace, "pls ya Maheer dan Allah kada ka bari sumin Alura  wllh bana so, ya fad'a tareda shagwab'e fuska  kamar wani k'aramin yaro.  Wani irin murmushi ne yay escaping lips d'insa sannan yace" Abdul wai bakasan ka girma bane yanzu?  nasan da Momy tana nan da tuni kana da k'anwa, ya k'are maganar idanunsa suna kawo k'walla,   Rungumeshi Abdul yayi tareda fashewa da wani irin kuka sabida tuno masa da Momyn da yayan nasa yayi,

Sosai Maheer d'in ya rikice sabida jin kukan Abdul, d'in sabida a duniya ya tsani abinda ze sanya k'anin nasa kuka, to amma babu yanda ya iya akan abinda Allah ya k'addarowa rayuwarsu, cikeda damuwa ya shiga rarrashin sa, harya samu yayi shiru, a haka suka shiga cikin Asbitin,  suna shiga wata farar ma'aikaciyar asibitin ta tarbesu da kulawa, cikin mintuna kad'an tayi musu iso zuwa office d'in babban likita dake duty ranar,  sosai ya shiga duna Abdul d'in inda ya tabbatarwa da Maheer d'in ulcer ne take damun Abdul d'in, dan haka ya rubuta masa maganin tareda bashi shawaran ya guji duk wasu abubuwan dazasu sanya ta kuma tashi,

Godiya sukayi masa sannan suka nufi babban phamarcyn dake cikin asibitin suka siya maganin suka wuce gida,  bayan sun dawo Direct side d'in Maheer d'in suka nufa sabida Abdul d'in ya samu ya huta, suna shiga kwanciya Abdul d'in yayi akan doguwan Royal kujeran dake perlourn, inda shi kuma Maheer d'in ya nufi bedroom d'insa danyin wanka, yana shiga Abdul ya mik'e sabida wata irin k'ishirwa data matsa masa, madaidaicib prich d'in dake ajiye a perlourn ya nufa, batareda tunanin komaiba ya bud'e, wata irin fad'uwar gaba ce ta ziyarci zuciyat Abdul d'in, lokaci guda kuma idanunsa suka firfito alamar tsoro, sabida wasu manyan kwalaban giya dayay arba dasu a cikin prich d'in, hakanne yayi daidai da fitowar Maheer daga bedroom d'in,   juyowa Abdul yayi tareda d'akko d'aya daga cikin kwalbar giyar wacce ta d'au sanyi se faman gumi take,

Wani irin kallo Abdul yake bin Maheer dashi wanda yafi kama dana tuhuma, sannan yace " why ya Maheer? Har zuwa wani loakaci zaka d'auka a haka?  Kai kanka kasan da cewar wannan d'abi'ar bata dace dakai ba sam, musamman idan mukai duba da illar datakeyiwa garkuwan jikin d'an adam,  shin kanaso kaima na rasaka ne kamar yanda muka rasa Momy?   Ya fad'a tareda sakin wani irin kuka......!

Yaune karo na farko a Rayuwar Maheer dayaji wata  irin kunya ta kamashi dayaji irin kalaman da tilon k'anin nasa ke fad'a , tabbas yasan shangiya ba abubane me kyau, amma to ya zeyi tunda k'addaransa ne a haka?  Da k'yar ya iya tattaro maganar data rage masa, sannan yace i'm sorry brother, ni kaina bansan ya zanyi ba is just a destiny.....  But.  Kasa k'arasawa yayi sabida wani irin kuka dayazo masa. Da wani irin mugun sauri Abdul ya taho ya rungume yayan nasa cikeda soyayyah gamida tausayinsa.

Washe gari  tunda sanyi safiya Hajiya murja taketa faman zuruftu, kallo d'aya zakayi mata ka

fahimci tana cikin farinciki sabida  dawowar maigidan nata, sabida ko babu komai yau zata samu cikar burinta,  akan Maheer, wanda take kallo a matsayin matsalarta a rayuwa.  Wuraren k'arfe 2 jirginsu Alhaji Nasir ya sauka, dan haka Maheer da Abdul suka tafi d'akkoshi daga air pord d'in,  tunda hajiya Murja taji dawowar mijin nata dan haka da hanzari ta nufi bakin babbar k'ofa dake perlourn tareda d'aga d'an k'aramin kafent d'in daka shimfid'a a gurin, wani garin magani ta zaro daga bakin zaninta sannan ta barbad'a, sannan ta mayar da kafet d'in yanda yake,   wani sahid'anin murmushi ta saki sannan ta koma kan daining nan ma ta gama tsubbace tsubbacenta,

Su Maheer na zuwa suka samu dady A zaune yana jiransu, da sakin fuska suka nufi mahaifin nasu suka Rungumeshi, sabida wani irin mugun missing d'insa da sukayi a kwana 2n da baya nan,  Dady ma hugging nasu yayi back cikeda tsantsar k'aunar yaran nasa,  kallon fiskar Abdul dady yayi cikeda kulawa yace " lafiyanka kuwa Abdul naga fuskanka ya fad'a min sosai, shafa kai Abdul yayi tareda shafa dogon hancinsa yace, "dady ni lafiyana k'alau, dama ya Maheer ne bashida lfy amma bani ba, ya k'are maganar yana  kallon Maheer d'in cikeda tsokana, da gudu Maheer ya bishi yana son kamashi amma ina tuni Abdul ya bud'e mota ya shige yana dariya, murmushi kawai dady yayi a ransa yanajin wani irin dad'i sabida ganin hankalin yaran nasa ya kwanta,  a haka suka kama hanyar gida,

Cikin mintunan da bazasu gaza 30mn ba suka isa cikin anguwan Rimi, parking yayi a bakin makeken get d'in gidansu,  horn yayi sannan malam ya wangale musu get tareda d'aga musu hannu cikeda fara'ah, kunna kan motar Maheer yayi zuwa cikin gidan,

Parking space ya nufa sannan yayi parking,  Maheer da kansa ya fito ya bud'ewa dady kofan motar sannan ya fito, cikeda ladabi ma'aikatan gidan suka dinga zubewa suna kwasar gaisuwa, tun daga kan masu bawa flower ruwa har zuwa kan masu share-share,

Murmushi kawai dady keyi tareda amsa musu gaisuwan cikeda fara'a, wannan dalilin ne yasa ma'aikatan gidan suke jin dad'in zama a gidan, sabida kokad'an dady bashida raina mutane balle kuma ya keta alfarman su, a haka suka k'arasa babbar k'ofar da zata sadasu da babban perlourn gidan,  a hankali dad ya murd'a handile d'in dake jikin k'ofar,  batareda tunanin komai ba ya d'aga k'afarsa da sallama ya shiga perlourn, yana taka kafent d'in ya tsaya cak....

_Sisters kuyimin haquri da wannan insha Allah zuwa jimawa zanyi qoqarin ganin na qara muku wani idan  lokaci ya bani damar yin hakan.😁_

_Comment_
_Nd_
_Share_

*Zm muhmd*
*(CHuBaD'o)*😁

_*🎀KIYARDA DANI...!🎀*_
🎀🐾🎀

*♝ IᗪTᏋꪶꪶIᏀᏋᗪT WгITᏋг'ى ASSѡ📚✍️*

*💫DEDICATED: to Sis naja'art*

_*WRITING BY: Zm (CHuBaDo)*_

*✨Special Gift for Hafsat Hafnan (my jika),.*

_Page:7_

___________📖 da sauri Maheer ya jawo Abdul dake k'ok'arin bin bayan Dady, tsayawa Abdul d'in yayi tareda turo baki kamar zeyi kuka yace ""ya Maheer kakusafa kasa na fad'i, ya k'are maganar a shagwab'e kamar zeyi kuka, wani miskilin murmushi Maheer ya saki wanda ke k'arawa fuskarsa kyau, sannan yace " wai yaushe zaka dena wannan shagwab'an ne? bakasan ka girma bane? Yanzufa kana 23yrs nefa, " uhm ya Maheer niban girma ba har yanzu yaro ne ni a gurin yayana,

Jan hancin Abdul d'in Maheer yayi, hakanne yasa Abdul ya saki k'ara, tareda saurin d'ora hannunsa akan hancin, dariya sukayi gaba d'aya tareda kama hannun juna cikeda so gamida k'auna,

a haka suka marayawa Dady baya zuwa cikin hamshak'in katafaren perlourn nasu,

A tsaye suka samu Dadyn tareda hajiya Murja wadda keta zuba masa kirsa da kisisina.

cikeda barikanci ta kama hanun Dady ta nufi daining aria dashi, duk yanda Dady yaso yace mata zeje yayi sallah sam kasawa yayi, sabida wani bala'in shakkanta daya samu kansa da ita, shidai Maheer kallonta kawai yakeyi a ransa yana mamakin sauyin mahaifin nasu, musamman idan yayi duba da irin rawarkan da Dadyn yakeyi A kanta seyaji zuciyarsa nayi masa wani irin zafi, shiko Abdul sunkuyar da kansa kawai yayi yana aikin zancen zuci, lokaci guda kuma wani b'angaren na zuciyarsa na bugawa,

Wani had'add'en Flet tajawo zuwa gabanta, tareda bude babban food flacks d'in dake gabanta, nan da nan k' ayataccen k'amshin abincin ya karad'e perlourn, wani irin lumshe idanu Dady

yayi lokaci guda kuma ya saki murmushi tareda yabawa matar tasa,

tana gama zuba masa kayan alatun data shirya masa a flet d'in ta mik'a masa, da kulawa Dady ya karb'a seda ya gama kod'ata, sannan ya d'ebi abincin ya kai bakinsa batareda yin bisimillah ba, tunda ya fara kai abincin bakinsa tunaninsa ya fara sauyawa, lokaci guda yaji a duniya babu wanda yake so kuma yake k'auna fiyeda kowa Face Hajiya Murja, haka kuma babu wanda yake k'aunar yaga farin cikinta kamar ita, a yanda yakeji a gameda ita ze iya rabuwa da kowa a kanta, dan haka ya tsaya cak dacin abincin, tareda zuba mata manyan idanunsa,

Hakanne yasa ta saki wani d'an iskan murmushi tareda gyara zamanta ya koma irin na hamshak'an matannan, wani far tayi da ido hakanne ya k'ara k'ular da Maheer, hakanne yasa yaji ya  k'ara tsanarta fiyeda ko yaushe a rayuwarsa, wani siririn tsaki yaja, hakanne ya mayar da hankalinta gareshi,  wata uwar harara ta watsa masa tareda d'aure fiskarta tama'au ta kalli Dady tace " gaskiya Alhaji lamari yaron nan ya fara isata a gidannan, inda mutunci aini kamar uwa nake a gurinsa, tunda ina Auren ka, amma ko kad'an yaron nan baya raga min balle ya darajani, tamkar wata sa'ar sa haka yake kallona ta fad'a tareda fashewa da wani irin kuka wanda yafi kama da na munafurci,,,,,!

Kallonsa Dady ya mayar ga Maheer wanda ya gama k'ulewa da kalamanta,

Cikeda wani irin zafin Rai wanda shi kansa besan yanada shi ba Dady ya kalli Maheer yace " kai yaushe ka zama d'an iska ban sani ba? matar tawa zaka Raina min dan  gidanku?  Shin bakasan Albarkacinta kukeci a gidannan ba?  Mudin kuna son zama dani a gidannan wllh sekun yi mata biyayya, fiyeda yanda ma kukeyi min, dan haka ka bata hak'uri yanzun nan batareda b'ata lokaci ba"""""".....!  Ya fad'a  cikin d'aga murya.

Cikeda kad'uwa Abdul yake kallon Dady!!! Shikuwa Maheer daskarewa yayi sabida mamakin canzawar Mahaifin nasu a lokaci guda, sabida a iya Rayuwarsa dashi betab'a d'aga masa murya irin na yauba, kuma dukda hakan ma a kan wannan shaid'aniyar matar?.

Wani irin zafi zuciyarsa ta shiga yi masa, dan haka ya k'udurtawa kansa cewar baze tab'a bata hak'uri ba koda duniyar zata tashi gaba d'aya...

Cikeda tsoro Abdul yake kallon yayan nasa, sabida ganin sauyawar da yanayinsa yayi, tabbas yasan ya Maheer bashida hankali idan ransa ya b'aci  dan haka yayi hanzarin dafa kafad'arsa yana yi masa nuni daya bawa hajiya Murjan hak'uri amma fir Maheer yak'i yin hakan,

Cikeda munafirci hajiya Murja ta dafa kafad'ar Dady tana kuka tace " dama na fad'a maka wllh baze bani hak'uri ba, kana kallon yanda yake kallona kamkar ze dake ni...!

Cikeda k'unar Rai Dady yace "" wllh ko zaka mutu yau Maheer seka bawa Murja hak'uri, idan kuwa ba hakaba wllh sedai kabar min gidana kaji na gaya maka..!

Cikeda tashi hankali suke kallon mahaifin nasu sabida basu tab'a zaton wannan maganar daga bakin Dady ba,

Kuka Abdul ya saki sannan yace"" Dady mune fa yaranka Abdul da Maheer, shin ka manta maganar da kake gaya mana kullum cewar mu kaida'aine mahad'in rayuwarka Dady? Amma yau kaine da kanka kake cewa yaya Maheer d'in dakafi so yabar maka gidanka akan wannan matar Dady?

Wata uwar harara Dady ya jefi Abdul da ita, sannan yace """ wllh bazan janye k'udirina ba, koya bata hak'uri, kokuma yabar min gidana,,,

Da sauri Maheer ya kalli Dady yace" Dady zan bata hak'urin kamar yanda ka nema, cikin wata irin murya ya Kalleta kamar wani d'an daba yace " kiyi hak'uri!

Yanda yayi maganar kawai ya isa ka fahimci daurewa kawai yakeyi,

Murmushin mugunta Hajiya Murja ta saki sannan sannan ta kalli Dady ta k'ara fashewa da wani sabon kukan tace""" Alhaji kana ganin a yanda yake bani hak'urin kamkar wata sa'arsa....

Wani irin murmushi Maheer yayi tareda k'udirawa zuciyarsa cewar wllh baze sake bawa wannan shaid'aniyar matar hak'uri kuma ba sedai duk wacce za'ayi ayi,

Hakanne yayi daidai da fitowar Binta 'yar kwabo daga d'aki, cikeda munafurci ta k'araso perlourn tareda matswa kusada hajiya Murja dake kukan munafirci tace " haba kekuwa Murja dan Allah kiyi hak'uri ki manta da komai, na tabbata da Maheer yasan koke wacece da bazeyi miki haka ba,

Wani irin haushi ne ya ida cika zuciyar Maheer sabida jin abida Bintan tace, wani irin ja idanunsa suka k'arayi sabida b'acin Rai, a fisace ya fara tafiya cikin takunsa me cikeda izza taamar wani zaki ya tsaya a gaban Binta 'yar kwabon dake tsaye a kusada Hajiya Murja, cikin wata irin murya mai kama data 'yan daba yace """ wace ita kuwa? Ba haihuwarta akayi kamar kowa ba, aiba daga sama ta fad'o ba balle kice daban take da kowa, ya k'are maganar yana Binta da wani d'an iskan kallo, wanda yafi kamada saura k'iris na mareki,

Sosai Binta ta tsorata da yanayinsa Maheer, musamman yanda jikinsa yake tsima kamar wanda ake kad'awa gangi,

Koda wasa bata tab'a zaton tantirancinsa yakai haka ba,

Saukar Mari Maheer yaji akan fiskarsa, Dady ne ya d'aukeshi da wani lafiyayyen mari wanda yasa fiskarsa ta d'aure sabida Azaba, tun kafin ya dawo daidai ya sake k'ara masa wani marin wanda yafi na farko shiga, sannan ya nunashi da yatsa cikeda b'acin Rai yace ""Maheer Ashe Rashin tarbiyarka yakai haka dazaka dinga cin mutuncin matata a gaban idanu na? Wllh

Maheer ka gama fice min a rai, tayanda naji cewar na tsaneka, haka kuma nayi nadamar haihuwarka a Rayuwata, wllh dana san haka zaka zamemin da tin kafin kazo duniya nayi addu'ar Allah yasa ayi B'arinka!,  Dan haka ka tattara yinaka yinaka ka barmin gidana wllh daga yau na sallamawa duniya kai..!!!!

Wani irin bugawa k'irjin su yayi lokaci guda musamman ma Maheer wanda jinsa da kuma ganinsa suka fara barazanar d'aukewa!

zubewa kawai yayi a  k'asan tiles d'in dake perlourn cikeda tsantsar tashin hankali, lokaci guda kuma ya saki wani irin kuka kamar ransa ze fita,

Da gudu Abdul ya k'asa kuda Dady lokaci guda kuma ya zube a gaban k'afafunsa ya rik'e sannan ya fara magana cikin kuka yace, " dan girman Allah Dady kada kayi haka, wllh ya Maheer baya cikin hankalinsa shiyasa yayi abinda ya aikata, wllh Dady nayi maka alk'awarin ni zan sanyashi ya durk'usa a kan gwiwowinsa ya bata hak'uri, indai har zaka janye kalamanka a kansa pls Dady ya fad'a yana k'ara k'ara damk'e k'afar Dady n,

Fisge k'afarsa Dady yayi daga ruk'on da Abdul d'in yayi masa, sannan yace " na rantse da Allah mai girma bazan janye ba, kuma muddin ka k'ara Rok'ona akan wannan maganar senayi maka baki kaima Abdussalama"  ya fad'a a zafafe!

Maheer dake zaune bisa tiles  mik'ewa yayi idanunsa suna zubar da hawaye, wanda suka k'arawa idanunsa ja sabida tashin hankali yace " Abdul karkace komai kamar yanda Dady yace, dan haka zan tafi kamar yanda ya buk'ata, sedai ina neman Alfarma a gareka k'anina, dan Allah ko nan gaba kada ka aikata abinda Dady zeyi fishi dakai kamar yanda yayi dani a yanzu, inaso kayi min alk'awarin cewar ko babu Maheer a rayuwarka zakayi Rayuwa me Aminci fiyeda wacce mukayi tareda kai a baya k'anina, abu na biyu kuma shine don Allah Abdul ka kulada Dady sosai, sannan  karka bari tafiyata ta zama silar sauyawar Rayuwarka daga farin ciki zuwa k'unci, yana kaiwa nan ya mik'e tareda sakin wani irin  murmushi wanda yafi kamada na takaici ya nufi k'ofar fita daga perlourn,

Da wani irin mugun gudu Abdul yaje yafad'a jikin Maheer sannan ya rungumeshi ta baya, tareda fashewa da wani irin kuka yace " pls ya Maheer dan girman Allah karka tafi, i cn live without you ya Maheer plsssss, ya wani ja pls d'in tamkar ze shid'e,

Juyowa Maheer yayi ya tareda rungume k'anin nasa sabida jin yanda yake kuka kamar ze mutu,!!

bayansa ya dinga bibbigawa, lokaci guda kuma ya zare jikinsa daga na Abdul d'in ya fice daga perlourn.

Zubewa Abdul yayi a k'asa tareda sakin wani irin kuka me ban tausayi, lokaci  guda kuma ya maida kallonsa ga hajiya Murja, idanunsa a cike tab da k'wallah, daga irin kallon da Abdul d'in

keyi mata zaka fahimci na tsantsar tsana ne,

mik'ewa yayi da da sauri zebi bayan Maheer d'in, sabida bayajin ze iya barin yayan nasa ya tafi, dole ne ya tsayar dashi.

cikin d'aga murya Dady yace "wllh Abdul idan ka fita daga perlourn nan kabi bayan Maheer sena tsine maka....!

Wani irin kuka Abdul ya saki, cikeda tausayin rayuwar da yayan nasa, tabbas yasan halin Maheer yanada wata irin zuciya me wahalar tank'waruwa, babbar damuwar sa yanzu itace, yasan ya Maheer ze sake dawo da d'abi'ar daya bari a kwanakin baya ta shan Giya.

Sabida yayi imani da Allah kan cewar yanzu itace  zata zame masa abokiyar rayuwa a inda zashi, dama ya lafiyar kura balle tayi zawo?

Sautin kukansa ya sake k'arawa cikeda tausawa kansa ta yanda  ze rayu batareda ya Maheer d'insa ba,

hannunsa ya d'aga yana kallon sama cikeda k'ask'antar dakai yace _""" ya Rabbi ka tsaremin yayana daga dukkan sharrin mutanan dake cikin wannan duniyar, sannan ka cika rayuwarsa da dukkan farin ciki na har abada, ya Allah ka shiga lamarin mahaifin mu, kasa kuma ya fahimci illar abinda ya aikata a nan kusa ya Rabb🤲.._, ya k'are addu'ar yanabin Hajiya murja da wani irin kallo wanda yake nuna tsantsar tsanar dayake mata a fili,  a fisace Dady yabar perlourn yana huci tamkar wani bak'in kumurcin maciji.

B'angaren Maheer kuwa wata black d'in trolly ya janyo tareda bud'e hadadd'iyan drower d'insa dake manne a bango, wasu takardu ya shiga d'akkowa daga ciki drower d'in tamkar bazasu k'are ba,

da'alama takardun masu mahimmancin gaske ne, yana gama xubawa yaja zip d'in ya rufe,

wata trolly d'in ya sake janyowa, sannan ya d'ebi  kad'an daga cikin kayan sakawanshi ya zuba a ciki, babban abinda ze bawa me karatu mamaki shine wasu k'ananan kaya Maheer ya iba, wayanda sukafi kamada na jarirai ya zuba a cikin trolly d'in sannan ya jasu ya fita Dasu,

Yana fitowa masu aikin gidan suka nufoshi da sauri dan su karb'i kayan , tundaga nesa suka fahimci irin halinda uban gidan nasu yake ciki, dan haka suka ja burki batareda sun k'arasa inda yake ba,  booth d'in motar ya bud'e tin kafin ya k'araso, dan haka yana zuwa ya jefa manyan jakunkunan a ciki ya kulle, sannan ya figi motar da wani irin gudu, mamaki ne ya kama malam mai gadi, dan haka ya wangale masa k'ofar get d'in tun kafin ya k'araso,

Da wani irin mugun gudu ya kwashi motar tamkar ze tashi sama ya fice daga gidan, tareda k'udurtawa zuciyarsa cewar,,,,, komai daran dadewa baze sake waiwayar gidan ba, kamar

yanda Dady yace "ya sallamawa duniya shi, haka kuwa ze k'are Rayuwarsa a duniyar batareda ya sake waiwayar sa ba...!!!

*_Wannan shine mafarin labarin_*

_More comment_
_More typing_

_Share pls_

*_ Zaynab muhmd CHuBaD'o😁_*
_*🎀KIYARDA DANI...!🎀*_
🎀🐾🎀

*♟IᎠᎢᎾ|||ᏀᎾᎠᎢ ᎳrIᎢᎾr'ی ASSᏇ📚✍*

*💫DEDICATED: to Sis naja'art*

_*WRITING BY: Zm (CHuBaDo)*_

*✨Special Gift for Hafsat Hafnan (my jika),.*

*_A gaskiya jiya naji matiqar dadi duba da irin comment d'in da kuka dinga zubamin, ngde sosai Allah kuma yabar qaunar ta har'abada, yanda kuka farantamin jiya, haka nima zan faranta muku da yardan Allah, ammafa idan banga comment yanda ya kamata ba, tofa bazaku kuma jina ba senan da sati hudu🤣_*

*_Sanarwa ta musamman, kokuma ma ince albishirinku, Haziqan marubutan nan kokuma in kirasu da tagwaye, JAMEELAH UMAR JANAF tareda sahibarta HAFSAT MUSTAPHA (HAFNANCY) sun kawo muku wani irin salo wanda duniyar marubuta batatab'a zuwa da irinsa ba, akan farashin Naira 200 kacal kowani littafi, ga wanda yake son duka biyun kuma akwai garab'asar da marubutan sukazo da ita, inda zaku biya 300 kacal duka biyun. Wa'yannan litattafai sune kamar haka, MALIKA MALIK da kuma KISHIN MATA, kada ku bari Abaku Ibri😄_*

_Page: 8_

____________📖 tunda ya jefa motar kan baban titin daze kaishi garin Abuja yake ta faman zuba uban gudu kamar me shirin tashi sama,  a wannan yanayin abubuwa dayawa ne suka dinga dawo masa tamkar a lokacin suke faruwa,  lips d'insa ya had'e ya danne da fararen hak'oransa sabida irin k'unar da zuciyarsa takeyi masa, lokaci guda kuma wani b'angare na zuciyarsa ya aiyano masa cewar lallai yakamata yayi nisa da k'asar Nigeria gaba d'aya, badan komai ba sedan muddin idan yana cikin Nigeria wata rana zasu iya had'uwa da Dady wanda shi kansa bazeso hakan ba,  a haka ya isa garin na Abuja zuciyarsa na k'una,  Direct gidansa ya nufa dake Garki,  A wani madaidaicin gida yay perking wanda aka k'awata shi da kayan gini na alatu,  dukda cewar gidan ba wani babba bane sosai hakan baze hanaka ganin kyawunsa ba, horne yayi a bakin Get d'in  dan haka da sauri me gadin gidan mai suna Lawan ya wangale masa Get d'in,  da wani irin gudu ya danna kan motar ciki,

Ya jima a cikin motar bai fitoba, illa ma kifa kansa da yayi akan sityarin motar, gaba d'aya ji yayi duniyar tayi masa zafi, haka kuma lokaci guda yaji mata sun fice masa A rai, a yanzu babu wata mace wadda ze iya fad'ar alkhairinta  a Rayuwarsa, hasalima gani yake duk mata halinsu d'ya, a hankali ya bud'e murfin motar,  lokaci guda ya ziro kyakkyawar k'afarsa ma'@bociya dogayen yatsu waje, hakanne yay daidai da k'arasowan Get man d'insa bakin motar,  cikeda girmamawa Lawan yace "barka da zuwa Ranka ya dad'e.

Dak'ar Maheer ya k'ak'alo murmushin dole yayiwa Lawan, sabida a tsarin Rayuwarsa be yadda da wulak'anta duk wanda Allah ya had'ashi dashi ba, koda kuwa waye, nuni yayi masa da booth d'in motar dan haka da sauri Lawan ya k'arasa gurin ya fara sauke madaidaitan trolly d'in dake bayan motar,  a hankali ya fara takawa cikin takunsa me cikeda izzah gamida tak'ama har zuwa babban perlorn gidan wanda aka k'awatashi da had'add'un Royal Chiar's  'yan Asalin k'asar Turkiya.

Ajiye kayan Lawan yayi sannan ya juya dan ya koma bakin aikinsa,  zubewa maheer yayi akan d'aya daga cikin kujerun dake perlourn, lokaci guda ya saki wani irin kuka mai ban tausayi ga mai sauraronsa, sosai yake kukan cikeda tausayawa rayuwar kansa da kuma ta k'aninsa wanda ya kasance mafi soyuwa a gareshi, kiraye kirayen sallar da aka fara ne yasa Maheer ya tsagaita da kukan ya mik'e, wani wani madaidaicin corridor naga ya nufa sannan ya bud'e wata babbar k'ofa ya kunna kai ciki, wani katafaren dak'i, komai na bedroom d'in ya dace da inda aka sanyashi tamkar d'akin turawa babu wata hayaniya a ciki,  toilet ya nufa Direct  nan ma ban tsayaba seda na lek'a sabida in ganowa mai karatu wace duniyar ce a ciki, toilet ne mai girman gaske wanda aka k'awatashi da kayan kamfanin Mayeesh salam dake k'asar Turkiyar, da gudu na fito sabida ganin Maheer na k'ok'arin yin tsirara a gabana🤣

Kansa ya sakarwa shower cikin mintuna kad'an ya fito d'aure da towel sabida kar sallar ta wuceshi,  a gaggauce ya kammala shirin nasa sabida jin an tada ik'ama, da hanzari ya fito ya nufi masallaci, seda aka idar da salla sannan ya dawo gida, yana shiga perlourn Direct prich d'in dake perlourn ya nufa,  dukda cewar bashida tambacin samun mutuniyar tasa a ciki,

Yana bud'ewa kuwa babu komai a ciki se ragowar guda d'aya d'akkowa yayi tareda zama bisa kan kujera, se'a lokaci naga kwalbar giyar sosai an rubuta Brandy a jiki,  ko kad'an be jira wani cup ba ya tsige murfin ya kafata a bakinsa sannan ya wuce bedroom da kwalbar a hannunsa.

Afwan pls yau ba yawa sosai🙏

Comment
And
Share

*Zm muhd*
*(CHuBaDo)*😁
_*🎀KIYARDA DANI...!🎀*_
🎀🐾🎀

*♝IᑎTᗴ||IGᗴᑎT WrITᗴr'ی  ASSത📚✍️*

*💫DEDICATED: to Sis naja'art*

_*WRITING BY: Zm (CHuBaDo)*_

*✨Special Gift for Hafsat Hafnan (my jika),.*

_Page: 9_

__________📖 tin kafin yakai bedroom d'in ya fara tangad'i,  da k'yar ya iya k'arasawa tsakiyar d'akin sannan ya fad'i, lokaci guda wani irin nannauyan bacci ya samu nasarar d'aukesh a wannan hali,

Tun bayan tafiyar Maheer Abdul yaketa faman kiran wayansa amma kuma bata shiga balle ma yasan halinda yayan nasa yake ciki, tunda sauran haske yake jarraba kiran Maheer d'in amma haryanzu da Dare ya farayi kalma d'aya ake sanar dashi itace *_Swich off_*, jefar da wayar yayi a jikin bango sabida takaici, lokaci guda ta daki bango ta tarwatse,  wani irin ihu Abdul ya saki batareda yayi la'akari da  Dare ba!!  A haka baccin wahala yay awon gaba dashi a kan makeken Royal Bed d'in Maheer d'in,

*_B'ABGARAN GIDAN ALHAJI MAHMOUD MUHAMMAD KUWA_* khabeer ne zaune bisa d'aya daga cikin kujerun dake perlourn, gefansa kuma system ce K'irar Companyn Apple wadda ya mayar da dukkan nutsuwarsa a kanta, Umaisa ce ta fito daga Room d'in ta, sanye take cikin wata bak'ar jallabiya wadda aka yalwata gaban rigar da chiristel stone masu launin ja, hakanne yasa bak'in Rigar ya baiyana ainihin kalar hasken fatarta, a hankali take takowa tamkar wadda k'wai ya fashe ma a ciki,

A haka harta k'araso inda yake, kanta ta d'an sosa kad'an tamkar wata mara gaskiya sannan ta kalleshi tace, " ya khaberr, dan Allah dama so nake na fad'ama idan zaka tafi office da safe zan bika ka saukeni a gidansu Nusaibah tunda hanya ne.... Pls yaya don Allah...!

Tunda ta fara magana be d'agoba ya kalleta ba har seda takai k'arshen maganar sannan ya d'ago manyan Golden Eyes d'insa ya zuba mata, sosai yake nazarinta sannan yace " me zakijeyi gidansu? Kinsan dai bana son yawo ko? Shagwab'e fuska tayi kamar zatayi kuka tace " yaya ba yawofa zanje ba fa but she's not fleeng fine thts why nake so naje gidansu pls yaya don Allah karkace A'a...! Ta fad'a kamar zatayi kuka!

Tabe baki yayi sannan yace "its ok naji Allah ya kaimu goben, da sauri ta zauna a kusa dashi tareda k'ank'ameshi sabida murna, murmushi kawai yayi sannan ya maida hankalinsa kan abinda yakeyi, a ransa yana k'ara jinjinawa shirme irin na k'anwar tasa.

tashi tayi tana 'yar dariyar farin ciki sannan ta nufi Room d'in Ruman dan ta sanar da ita batun zuwanta gidansu Nusy, A Kwance ta Samu Ruman tana bacci, murmushi tayi sannan ta fita daga d'akin, d'akin ummie ta nufa, da sallama ta shiga madaidaicin perlourn, a zaune ta samu ummie tanacin dambun shinkafa, da sauri ta k'arasa inda ummien ke zaune tareda washe fararan hak'oranta, sabida a rayuwar Umaisa tana bala'in son Dambun shinkafa,

Dungure mata kai Ummie tayi sannan yace " meye kika wani zauna min a gaba kina kallon na? Dariya Umaisa tayi sannan tace "Eyyah ummie kinfa san meya kawoni nan dan girman Allah kisammin ko kad'an ne kinji Ummie na.... Ta fad'a kamar zatayi mata kuka, dariya ta bawa Ummie sosai sannan ta kalleta tace " ta uwar kwad'ayi, nima k'anwata ce ta aiko aka kawo min shi, dan haka kema sekije taki k'anwar ta baki. Zaro ido Umaisa yayi sannan tace Ummie ni inada k'anwar da akayiwa aure ne, dama yayata kikace se'ince na taso Aunty Rumana ta dafa min tunda munada komai,

Wani irin kallo Ummie watsa mata sannan tace "lallaima yarinyar nan, dayake cutarta zakiyi ai gashinan kina kiranta da Aunty wanda dacan ba hakan kike kiranta ba.... Da sauri tace "Ummie forget about this chapter nidai ki samun dambu kawai, ta fad'a tana dariya, zama tayi dirshan a kan tattausan capet d'in dake perlourn, sannan ta fara gabzar Dambun tana xubawa Ummie santi, seda suka cinye tass sannan ta kalli Ummie tace " wllh daga jin Dambun nan Aunty Maryamce tayi ba Aunty Beebah ba, nifa wllh Ummie nafi son Aunty maryam sabida tafi Aunty Beebah kirki, idanfa mukaje gidan nida Rumana sekiga tanayi mana kallon wulak'anci, nifa

wllh da yaya Golden zeji shawarana cewa zanyi karya Auri Aunty Beebah. Ta k'are maganar tana yatsina fuska, itadai Ummie kawai kallonta takeyi harta kai aya sannan tace

"Amma yarinyar nan kin iya iskanci wllh, dan gidanku surukar tawa kike kushewa,? Turo baki Umaisa tayi sannan tace " Ummie ai gaskiya na fad'a, kema kanki ai kinsan halinta sedai kik'i fad'a, wllh da yaya Usman ze Aureta sena zugashi yace ya fasa, inyaso senaga k'arshen jin kan da take tak'ama dashi, duka Ummie takaiwa Umaisa, da sauri ta mik'e da gudu tana dariya, Ummie ma dariyar tayi, a ranta kuma tana jinjina maganar Umaisan, tabbas tasan gaskiya ta fad'a Beebah bata da halin kirki, amma kuma batajin hakan zesa tasa a jjanye maganar Aurenta da Khabeer, sabida ko da babu maganar aure tsakaninta da Khabeer d'in ita me rik'eta ce, tunda ita d'in diyar k'anwar ta ce. Ta jima tana tunani akan maganar Umaisa da Umaisan ta fad'a, sosai abin yayi mata tasiri a zuciyarta har gari ya waye,

8:00am dai dai khabeer ya fito sanye cikin k'ananan kaya, wanda suka baiyana ainihin cikar zatinsa, mukullin motarsa ne kawai a hannunsa inda d'ayan hannun nasa ke rik'e da wani abu kamar file, a gaggauce ya fito daga side dinsa, da alama a cikin sauri yake, kacib'us sukayi da Dady wanda ke k'ok'arin shiga side d'in nasa, cikeda ladabi ya rissina ya gaida mahaifin nasa, cikeda kulawa Dady yace "ina zaka kuma da sanyin safiyar nan, bayan yau ranar hutu ne son? Shafa kansa ya d'anyi sannan yace "Abba Asbiti zani inada mara lafiyan daya kamata in duba ne, murmushi kawai Abba yayi sannan ya bashi hanya yay gaba, a hanzarce ya k'arasa parking space, wata bak'ar toyota benza naga ya nufa sannan ya fad'a ciki tareda ficewa daga gidan gaba d'aya,

Khabeefr bashi ya dawo gidan ba se wajen 2:00pm, a zaune ya samu Umaisa se faman kunbure2 take, kobi takanta beyi ba ya nufi side d'insa don ya huta, sabida sosai yakejin gajiya a jikinsa,

Kuka ta dingayi sabida ganin ko kallonta ma beyi ba, ya Usman ne ya fito da shirin fita, da alama shima wani abinne ya taso masa, mik'ewa tayi da sauri ta nufeshi tareda kama hannunsa tace " pls ya Usman dan Allah naxo ka saukeni a Gaduwa Estate? A tak'ace ya kalleta yace " wa kika fad'awa zaki fita da ranan nan? Shagwab'e fusaka tayi sannan tace " mamie na ta sani,sannan kuma na gayama ya khabeer, shiru yayi yana kallonta na d'an lokaci sannan yace" muje, da sauri tabi bayansa tana washe mai baki kamar taci caca,

Tunda suka fara tafiya take zuba masa surutu har suka iso Gaduwa Estate d'in, da sauri ta bude murfin motar zata fita, wani uban kallo ya watsa mata sannan yace " wllh ki kula dakanki, naga se wani rawar kai kikeyi, sannan kuma nan dan 4:00pm zanzo na d'aukeki kinji ko? D'aga masa kai tayi amar taji sannan ta fice daga motar shi kuma yay gaba abinsa,

A hankali ta dinga takawa harta shiga gidan, kasancewar irin manyan gineginen nan ne masu kamada kinin gwamnati, a hankali ta tura k'ofar glas d'in dake perlourn, Mu'allim ne ya nifota da gudu yana cewa "oyoyo Aunty Umaisa na, da fara'a ta d'agashi tana dariya, kasancewar suna bala'in shiri da ita, hancinsa taja sannan ta kama hannunsa suka k'arasa babban prlourn

gidan gaba d'aya, da sallama suka shiga, babu mutane a perlourn se Hajiya Mariya mahaifiyar Nusaiba, gefanta kuma Nusaibah ce se faman kunbure2 take sabida Rashin zuwan Umaisan, tanaji muryanta ta mik'e da gudu tayi hugging d'in ta tana dariya, itama dariyar tayi a haka suka k'araso cikin perlourn hannunsu a sark'e cikin na juna, har k'asa ta sunkuya ta gaida Maman su Nusaiban, da sakin fuska ta amsa mata tareda tambayarta muta nan gidan, tashi tayi tabarsu a perlourn ta koma d'aki sabida Umaisan ta sake da k'awar tata,

Sun dade suna hira suna dariya, a haka Khalil ya shigo perlourn ya samesu, sanye yake cikin wata blue d'in gizna wacce ta baiyana cikar zatinsa, se'a lokacin na k'are masa kallo sosai, dogo ne sosai ma'abocin kwarjini da kuma haiba, bugu da k'ari kuma gashi kyakkyawa, fad'a murmushinsa yayi tareda cewa " kai Ashe dai babbar bak'uwa mukayi yau a gidan namu kenan, ya fad'a tareda zama a kan d'aya daga cikin kujerun perlourn, dariya tayi harseda fararen hak'oranta suka fito sannan tace "Ae yau nice a gidan su Blue Eyes. Dariya yayi sosai a ransa kuma yana jin sunan data kirashi a dashi d'in,

Nusaibah ce ta kalleshi tace " ya Khalil dan Allah ka kaimu Millonian peck mana dan Allah, shiru yayi sannan ya kalleta yace " ku shirya muje, da sauri Nusaiba tace " yaya a shirye muke wallahi, mik'ewa tayi da sauri ta nufi Room d'in ta, cikin mintuna kad'an se gata ta fito da mayafi a jikinta, seda taje dakin mama ta sanar da ita sannan suka fita daga gidan xuwa perking space, wata bak'ar Anaconda suka shiga sannan Khalil yayiwa motar key sukabar harabar gidan gaba d'aya, seda suka biya ta *Spar* ya siya musu ice cream da kuma tarkacen su coclet sannan suka kama hanyar Silver bed, kasancewar yafi kusa da Da Spar d'in, sosai Umaisa ta saki jikinta tamkar tayi shekara da sanin Khalil d'in, shikuwa Khalil hakan ba k'aramin dad'i hakan yayi masa ba, musamman idan yaji ta kirashi da Blue Eyes. Duk inda tabi Khalil kallonta kawai yakeyi, sabida komai yarinyar tayi birgeshi takeyi,

A haka sukaita shagalinsu da Nusaiba suna dariya,

---

Maheer kuwa tunda ya farka a daddafe ya mik'e ya fad'a toilet yay wanka, sannan ya d'aura Alwala ya fara jero sallolin dake kansa, yana idarwa wayarsa ya jawo ya bud'e tareda zare Sim card d'in dake ciki, sannan ya shirya cikin wasu k'ananan kaya, inda rigar ta kasance fara sol, wandon kuma bak'i wuluk dashi, sosai kayan suka karb'i jikinsa, kallo d'aya zakayi masa ka fahimci ainihin murd'ewar jikinsa, duba da yanda rigar ta wani lafe a jikinsa, dukda cewar baya cikin walwala hakan baze hanaka ganin kyawunsa ba.

wata number yay dailing wadda naga an rubuta *MUJAHEED* a jiki da babban bak'i, Cikin mintuna kad'an mujaheed ya d'auka cikeda mamaki yace " hy friend yau ka tina dani kenan?

Murmushi kawai Maheer yayi sannan yace" kana inane haka? A tak'aice yace" ina *Silver ved* wllh nagaji da zaman gidan ne shiyasa nazo nan dan na huta.

A tak'aice myaheer yace " ganinan zuwa, sannan ya katse kiran,  car keys d'in sa ya d'auka sannan ya fice daga gidan, Direct perking space ya nufa ya fad'a cikin motarsa, lokaci guda yayi mata key,  tun kafin ya k'araso lawan ya bud'e masa get d'in ya fice,

Cikin mintunan da bazasu gaza 15 ba ya isa gurin, a nitse yay perking sannan ya fito cikin takunsa me cikeda izzah, a hankali yake takawa harya isa gurin, babu wasu mutane sosai  se wasu matasan "yan mata daketa faman tsalle tsalle,  wayarsa ya d'auko tareda k'ok'arin kiran Mujaheed d'in sabida yaji inda yake, hakanne yay daidai da fad'owar Ice Cream d'in dake hannunta a jikin bak'in wandon dake jikinsa,  a fisace ya juyo ya fara bin jikinsa da kallo,  wani irin tafasa yaji zuciyarsa tanayi,  lokaci guda ya aiyana cewar tabbas babu abinda ze hanashi shukawa yarinyar nan mari, a fisace ya juyo dan yaga wace shafaffiya da man ce ta zuba mishi Ice Cream a jikinsa haka....!!!!

Comment
Nd
Share

*_Zm CHuBaDo_*😁
_*🎀KIYARDA DANI...!🎀*_
🎀🐾🎀

*♝ IᎠƬɛ||IƓɛᎠƬ WґIƬɛґ'ى ASSѡ📚✍️*

*💫DEDICATED: to Sis naja'art*

_*WRITING BY: Zm (CHuBaDo)*_

*✨Special Gift for Hafsat Hafnan (my jika),.*

_Page:10_

____________📖 dunk'ulewa tayi da sauri sabida yanda ta tsorata dashi, hannunta tasa ta kare fuskarta idanun a cike tab da k'walla, bakinta banda rawa babu abinda yakeyi, da k'yar ta iya bud'e baki tace "d...an gir..man Allah ka k..ayi hak'uri wllh ban saniba na zuba maka, ta k'are maganar tareda fashewa da wani irin kuka,

Sosai abin ya k'ara bashi haushi, cikeda b'acin rai ya sunkuya  dab da fuskarta yace " dilla

malama rufewa mutane baki idiot!!

Wani malolon takaici ne ya tsaya mata a wuya, harya mik'e ze tafi cikin kuka tace" karka sake kirana da idiot, sabida niba ita bace, ta fad'a tareda turo d'an k'aramin lips dinta gaba, tsayawa yayi cak, lokaci guda kuma ya juyo gareta tareda zuba mata manyan idanunsa masu matik'ar haske gamida jan hankalin duk wani me kallonsa, shiru yayi yana kallon yanda taketa motsa baki tanayi masa k'unk'uni, lokaci guda murmushi yay Escaping lips d'insa, wanda iya kacinsa labbansa,

A fusace a k'aso gareta tamkar mayunwacin zakin dayay arba da abinci, da sauri Nusaiba dake tsaye ta ranta a nakare sabida gaba daya ita mutumin ma tsoro yake bata, sunkuyawa yay dab da fiskarta, cikeda zafin nama yasa hannu ya dank'e lips d'in data turo mai, zuciyarsa fal mugunta ya matse mata shi da k'arfi ta yanda har seda ta saki wani sabon kukan na azaba, wani miskililin murmushi ya saki tareda datse lips d'insa da hak'oransa sannan yace" dan kin samu na barki shine kike tunani har kinada zarafin dazaki zageni na k'yaleki haka? K'ara matsa bakin yayi cikeda mugunta sannan ya fisge mayafin datayi Rolling dashi, hakanne yay sanadiyar baiyanar doguwar kalban dake kanta, sautin kukanta ta k'ara sabida azabar da lips d'in nata sukeyi mata, gashi kuma ya hanata damar dazata bashi hak'uri,

Ice cream d'in data zuba masa ya shiga gogewa da mayafin abayar nata, seda ya gama gogewa tsaf sannan ya jefa mata mayafin a fiskarta ya mik'e tareda nunata da yatsansa na dama yace " idan kika sake bari wannan mummunar fiskar taki nayi ido biyu da ita koda kuwa a inane wllh senayi miki rashin mutuncin dayafi wannan Idiot ya k'are maganar tareda watsa mata ragowar Ice Cream d'in dake cikin robar, kuka ta fashe dashi zuciyarta nayi mata zafi, tanaji tana gani yabar gurin batareda ya sake waigenta ba, khalil ne ya k'araso gurin shida Nusaiba, a haka suka sameta ita kad'ai a gurin tana kukan bak'in ciki da takaici, abinka da farar mace tuni bakinta yay wani irin ja gamida kumburi, sabida tsabar matsar dayasha a hannun Maheer,

Cikeda takaici Khalik ya juya ga Nusaiba yace "uban waye yayi mata haka amma bakije kin sanar dani akan lokaci ba harya bar gurin? Muzurai Nusaiba ta fara sabida ganin yanayin yayan nata, kamar zatayi kuka tace " wllh ya khalil nima bansanshi ba, muna wasa ne fa shine ta zuba masa Ice cream bata sani ba shine fa yayi mata haka..! Ta k'are maganar tana matsa ido cikeda tsoro,

Ita dai Umaisa banda kuka babu abinda takeyi, gefe na zuciyarta kuma a cike yake taf da tsoron Maheer, koya ta rintse idanunta maheer take gani tareda jiyo sautin kashedin daya suburbud'a mata a kunnenta,

Kasa magana tayi dan haka da suri ta mike tareda barin gurin tana aikin kuka, sosai Khalil yakejin sautin kuka a saman zuciyarsa, tareda d'inbun takaici rashin ganin wanda ya aikata mata hakan, a haka suka mara mata baya shida Nusaiba, a mota suka sameta ta had'e kai da gwiwa tana gurzar kuka.

Kasa ce mata komai Khalil yayi illa key dayayiwa motar sukabar parck d'in zuciyarsu a dagule, tunda suka fara tafiya bata d'agoba har seda suka iso Zone E sannan ta bud'e idon ta, cikeda k'warewa Khalil ya danna hancin motar zuwa cikin get d'in legislative Quaters d'in, tafiya kad'an sukayi sannan suka  iso bakin makeken gidandu Umaisan, bud'e k'ofar tayi zata fita ba tareda tace da kowa komaiba sema share hawayen dake bin fiskarta datakeyi, da sauri Nusaiba itama ta bud'e murfin motar ta fito, kusan a tare suka tura k'ofar Get d'in, babu kowa a farfajiyar gidan se ya Khabeer da wani Friend d'in sa Hashim,  cikeda gimamawa suka gaishesu sannan suka kunna kai zuwa maine perlourn gidan, a nan suka samu mamie da kuma Ummie wadda keta faman magana a waya, da alama da mamansu Beebah takeyi,  katse wayar tayi tayeda cewa "zan turo su Ruman da driver su kawo miki insha Allah.

Zuba musu ido mamie tayi, hakama ummie aka rasa wanda zeyi magana sabida ganin yanda bakin Umaisan ya kunbuwa kamar wacce aka gabzawa naushi,

Nusaiba ce tayi k'arfin halin katse shirun ta hanyar gaishesu, ummie ce ta amsa tareda tambayarta abinda ya faruda Umaisan,  ko kad'an bata b'oye musu komaiba duk abinda ya faru a tsakanin Maheer da Umaisa seda ta gaya musu,  sosai ran Ummie ya b'aci da abinda Maheer yayiwa Umaisan, dan haka ta dinga sirfa fad'a kamar ta ari baki, ita dai mamie tab'e baki tayi tana binsu da kallo, sabida ita harga Allah bataga laifin yaron ba sema na Umaisan, dan haka ta mik'e tayi sama tabarsu a perlourn Ummie tana ta sirfa fad'a kamar wadda taga Maheer d'in a gabanta, ita dai Nusaiba sallama tayiwa Ummie ta kama gabanta kamar wata munafuka haka ta fice abinta.

Hannunta Ummie ta kama suka nufi room d'in ta sannan ta dakko wani balm ta shafa mata a bakin  sannan tace tahau gado ta kwanta, tana kwanciya kuwa baccin wahala yay awon gaba da ita.

_Afwan yau ban samu tim bane shiyasa banyi dayawa ba,🙏_

Comment
Nd
Share

*Zm (CHuBaDo)*

_*🎀KIYARDA DANI...!🎀*_

🎀🐾🎀

*♝ ıDTɵ||IƓɵDT WrITɵr'ء ASSŵ📚✍️*

*💫DEDICATED: to Sis naja'art*

_*WRITING BY: Zm (CHuBaDo)*_

*✨Special Gift for Hafsat Hafnan (my jika),.*

_Fatima Aliyu badamasi, ni zm chubado naga saqonki haka kuma nayi farin ciki sosai da irin soyayyar da kikeyi min, sedai ina roqonki wata alfarma pls kada ki sakeyin irin abubda kikayi akaina, indai har son da kikemin na gaskiya ne, ni zm chubado nima sonki fisabilillah❤️_

_Page: 11_

____________📖 A kwana a tashi babu wuya a gurin Allah, haka rayuwar gidan Alhaji Nasir lamid'o ta sauya, komai idan za'a gabatar seda sanin Hajiya Murja kokuma amincewarta, komai na gidan ya dagule hakama al'amuran Companynsa, a yanzu kwata-kwata bashida katab'us akan komai se'abinda Murja ta zartar, wannan dalilin ne yasa wasu daga cikin ma'aikatansa suka ajiye aikinsu, sabida bazasu iya jurar wulak'anci ba,

Shidai Abdul baya iya cewa komai, dukkan abinda suka ga dama shi sukeyi a gidan, wasu lokutan ma haka zata tara mata da maza a gidan suyita rashin mutunci, amma bashida damar dazeyi magana saidai kallo, idan abin ya isheshi ne ma seya saka takalmansa ya d'auki keys din motarsa yabar musu gidan har zuwa lokacin da zasu gama,

Binta 'yar kwabo kuwa idan ka ganta a yanzu seka rantse itama matar gidan ce, sabida yanda take cin karanta babu babbaka, abinda taga dama shi takeyi sabida yanda Hajiya Murja ta lamunce mata yin hakan, shikuwa uban gaiyar bashida tacewa sunan dai yana gidan ne amma bashida maraba da hoto,

Hatta 'yan uwansa dake yola bama ya zancen su, tun suna kiransa a waya baya d'auja har ya gaji yayi blocking d'insu, sannan ya sanar da masu gadinsa cewar duk wanda yazo nemansa muddin daga yola yake karsu kuskura su barshi ya shigar masa gida,

Wannan shine dalilin dayasa su Baffa Ibrahim suka janye jikinsu daga lamarin Alhaji Nasir lamid'o, sedai su kansu sunaji a jikinsu cewar a kwai abinda yake damun d'an uwan nasu dan haka suka yanke shawarar zasu tayashi da addu'a akan dukkan abinda yake damun sa,

Kusan kullum se Abdul ya gwada kiran wayar Maheer amma kuma kullum kalma d'aya ake maimata masa itace *swich off*, sosai hakan yake k'ara d'aga masa hankali sabida rashin sanin ainihin halinda yayan nasa yake ciki, wasu lokutan sedai yayta kuka yana rok'on Allah ya kawo musu d'auki a cikin wannan babban Al'amarin da suke ciki,

Binta 'yar kwabo ce zaune a kan makeken daining d'in dake perlourn, sanye take cikin wani d'anyen leshi wanda aka k'awatashi da d'inki na alfarma, gefanta kuma wasu manyan mata ne kokuma ma ince hajiyoyin bariki, kowacce se faman taunar cigam sukeyi, kallo d'aya zakayi musu ka fahimci cikakkun 'yan Bariki ne na ajin farko, duba da yanayin fuskokinsu yanda sukaci uban bleeching kamar sun k'one, hirar su kawai sukeyi suna shewa sekace a gidan karuwai.

Hajiya bintace tayi murmushi tace "hajiya sa'a wai yaushe zaki tafi Dubai d'inne? Wadda aka kirada Hajiya sa'a tace " wllh k'awata ni yanzu duk tafiye tafiyan nan isheni, ina ganin wani Alhajin zan samu na aura ko nima na samu hankalina ya kwanta waje d'aya.

Wani irin kallo suka dinga binta dashi, wanda yafi kamada na mamaki, tabe bak'i Binta tayi sannan tace " Amma dai wllh Hajiya sa'a kin tabbata sakarai muddin kika Auri babban mutum a wannan shekarun nakin, ina laifin ma ki samu k'aramin yaro sabon jini ki Aura, wanda ze mayar dake cikakkiyar mace a gado, sannan kuma ku more Rayuwarku dashi,

Karaf Hajiya Asiya ta cafe tace " wllh 'yar kwabo kamar kin shiga raina, ni kaina burina kenan in samu yaro shakaf in Aure, sannan in sangarta shi da kudi ta yanda zamuji dadin rayuwa dashi, kinga daga nan semuci duniyar mu da tsinke. Tafawa sukayi sannan suka shek'e da dariya, Hajiya sa'a tace "wllh mutanan nan bakuda dama, toni da kun barni ai tsoho zan kwasowa kaina, dariyar suka kuma kwashewa da ita, suna tsaka da dariyar ne Abdul ya turo k'ofar perlourn,

Da wani irin mayen kallo Hajiya sa'a da Hajiya Asiya suke binsa dashi sekace wasu tsofaffin mayu, ko wacce da abinda take sak'awa a ranta a gameda Abdul d'in, batare da yace dasu k'alaba yay wucewar sa, sabida kaf cikinsu bega wadda takai ya gaisheta ba. A ransa ya k'udurtawa kansa cewar seya d'auki mataki akan wannan shaid'ancin dayake shirin kutso musu cikin gidan su.

Muje zuwa

*Comment*
*Nd*
*Share*

*Zm chubado😁*

_*🎀KIYARDA DANI...!🎀*_
🎀🐾🎀

*♝ IDTeɭɭIGeDT WrITer'ی ASSѡ📚✍️*

*💫DEDICATED: to Sis naja'art*

_*WRITING BY: Zm (CHuBaDo)*_

*✨Special Gift for Hafsat Hafnan (my jika),.*

_Page:12_

__________📖 a haka yabar perlourn yana tunanin ta yanda ze b'illowa lamarin, hajiya sa'a ce ta kalli Binta 'yar kwabo tace "k'awata wannan yaron kuma fa daga ina? Murmushi Binta tayi sannan tayi fari da idanunta tace " d'an me gidannan ne wllh sunansa Abdussalam, shine ma k'arami, shegun yara haka suke da masifar kyau, wai dan ma bakiga yayansa Maheer ba wllh yafi Abdul kyau nesa ma ba kusa ba, kama suke da ubansu, garama Abdul yafi kama da uwarsa, idan kika ganta seki rantse ba *BAFULATANA* bace sabida tsabar kyanta.

murmushi suka saki sannan Hajiya Asiya tace " kai gaskiya Hajiya Binta ina kamun wannan d'an beautyn yaron, kin ganshifa santalele dashi, wllh daga ganinsa zeyi abin kirki ta k'are maganar tareda wani d'an iskan murmushi akan fuskarta, tab'e baki Hajiya Binta tayi sannan tace "hmm kuma kunsan dai wannan yaron baku isheshi kallo ba, balle ma a kai ga maganar Aure, indai har kinaso kuga komai ya tafi yanda ake so tofa sekun fito da kud'i ta k'are maganar tana kallonsu with serious face.

*GARIN ABUJA*

Tundaga ranar da Umaisa sukaje silver ved, bata sake tunanin kuma fita ba, yau ta kama Friday ne dan haka suka shirya cikin wasu riga da sket na atamfa itada Rumana, inada mamie ta shirya Ameerah cikin wasu riga wando 'yan kanti k'irar *_Companyn Herjireenash_* hakama takalmin k'afarta wanda ya kasance bak'i wuluk, kallo d'aya zakayiwa Umaisa ka Fahimci bata son fita, kawai dan ba yanda zatayi ne, Ummie ce ta kalleta tace " saura kuma wllh kije kiyi musu iskancin da kika sabayi a gida, kinsan dai halin Beebah sarai, dama maryam tana gidan ne toda banja miki kunne ba, tunda ita tana iya jurewa rawar kanki. turo baki Umaisa tayi sannan tace " uhmm to Ummie ai idan ma Aunty maryam bata nan ai Momynsu tana gidan, base na zauna tareda ita ba kafin ya Golden d'in yazo d'aukar mu ba. Shiru Ummie tayi tana kallonta, ita dai Mamah kallonsu kawai takeyi tana murmushi kamar bazata ce komai ba se

kuma can tace "to tunda basa shiri da Beebah meyasa bazaki tura Ruman da Ameerah kawai. Ta k'are maganar cikeda son jin ta bakin Umaisa,

Washe baki Umaisa tayi wanda tun fitowarta daga d'akinta ta had'e rai sabida a rayuwarta ta tsani zuwa gidansu Beebah, komawa tayi kusa da mama sannan tace " yauwa Mamah na dama kedai kike fahimtar uzirina indai akan maganar gidansu Aunty Beebah ne, dan Allah ki fahimtar da matar nan kozata fahimce ni, ta fad'a kamar zatayi kuka. Sakin baki Ummie tayi sannan ta kalleta tace " dan uwarki nice matar? Ta fad'a tana k'ok'arin dank'o ta, da sauri ta shige bayan Mama tana dariya a haka mamie ta sakko ta samesu, murmushi kawai tayi sabida tasan diramar Umaisa da Ummie, 'yar k'aramar jakar goyon dake hannunta ta mik'awa Ruman sannan tace "gashi nan duk abinda 'yata zata buk'ata na saka mata a ciki, saura kuma ku saka min ita kuka tunda kunga Uwarta bata tareda ku, ta k'are maganar tana kallon fiskar Ameerahn, dariya dukansu suka saki a haka Khabeer ya shigo perlourn fuskarsa babu yabo babu fallasa, sanye yake cikin wata skey blue d'in shadda anyi mata d'inkin jamfa, wadda ta baiyana cikar zatinsa da kuma haibarsa, k'afarsa sanye take cikin wani bakin takalmin fata wanda ya baiyana zarazaran dogayen yatsun k'afarsa, dukda cewar be sanya hula a kansa ba, hakan be hanashi yin kyau ba,

Seda ya sake gaida iyayen nasa a karo na biyu sannan yay musu sallama ya fice daga perlourn, kallonsu Mamah tayi sannan tace " jira kukeyi se ance muku ku bishi sannan zaku bishi ko kuma yaya?

Tab'e baki mamie tayi sannan tace "ki k'yalesu indai khabeer ne ai yana daidai da iskancinsu, tana kaiwa nan ta kama step tayi sama abinta, da sauri suka mara masa baya hannunsu sark'e dana Ameerah wadda keta murna za'aje da ita gidansu Aunty Beebah. A haka suka cin masa zaune cikin bak'ar motarsa k'irar *formatic*

Bud'e motar sukayi Umaisa ta shiga gaban motar Ruman da Ameerah kuma suka shiga baya, motar yayiwa key sannan mai gadi ya bud'e musu Get suka fice daga gidan suka d'auki hanyar Wuse 2, a bakin wani makeken gida tsaya tareda yin horne, cikin mintuna kad'an aka bud'e musu get din,

Hancin motar khabeer ya danna zuwa cikin gidan, tun kafin suyi perking suka hango Beebah a tsaye a harabar gidan ta cab'a uban ado sekace wadda zata zab'en sarauniyar kyau, a nitse ya k'arasa yay parking wanda hakan yay daidai da k'arasowar ta gurin, se faman shan k'amshi take tana zuba yauk'i, shikuwa uban gaiyar se faman basarwa yake shi'a dole beson raini, Rumana ce ta fara bud'e murfin motar ta fito sannan khabeer ma ta bud'e side d'insa ba tareda ya fito ba, itako Umaisa banda zunb'urar baki babu abinda takeyi, cikeda gimamawa Ruman ta kalli Beebah tace Aunty Beebah ina yini? Cikeda sakin fiska tace "ina gajiya Ruman ya kike? A tak'aice tace Ify lau. Daga haka bata sake ce mata komai ba ta kama hannun Ameerah suka nufi maine perlourn gidan,

Se'a lokacin Beebah ta mayar da kallonta ga Khabeer tace "yadai na ganka haka kamar baka

farin ciki da ganina? Tab'e baki yayi sannan ya kalleta kimanin mintuna kad'an sannan yace " ke a garin ku haka ake karb'an bak'o ba gaisuwa sedai a tareshi da surutun banza?   Tab'e baki Umaisa tayi sannan ta bud'e murfin motar ta fito,  tunda ta fito Beebah take kallonta sabida bata tab'a zaton a kwai Umaisa a cikin motar ba,  wani irin kalo ta dinga binta dashi,  itako Umaisa yi tayi kamar batama san tanayi ba, seda ta fara tafiya sannan ta juyo ta kalleta tace "Aunty Beebah ina yini?

Sabida takaici kasa amsawa Beebah tayi a ranta tace" yanzu dama dan rashin mutunci ya khabeer yasan da yarinyar nan a motar shine yake gaya mata magana   a gabanta danta raina ta!!!   Katse ta yayi ta hanyar cewa " tunda bazaki gaidani ba matsa kiban hanya na fito.  Cikeda jin kunya tace "i'm so sorry kazo Ify?

Be bata amsa ba yay gaba ita kuma ta rufa masa baya, A ransa yace " a kwai aiki a gabana muddin na bari su Ummie suka had'ani da wannan yarinyar,  da sallama ya shiga parlourn fuskarsa a  sake, zaune ya samu su Hajiya Fatimah itada su Rumana tana ta faman tsokanarsu musamman ma Umaisa,  fad'ad'a murmushinta tayi sabida ganin Surukin nata,  zama yayi a d'aya daga cikin Royal chairs din da sukayiwa perlourn k'awanya,  cikeda girmamawa ya gaisheta tareda  tambayarta mutanan gidan, da sakin fuska ta amsa masa sannan shiru ya ratsa perlourn na d'an lokaci, kasancewarsa ba ma'abocin son magana ba, Umaisa ce ta katse shirun da cewa "mamah ina Aunty maryam taje ne?  Murmushi Hajiya Fatima tayi sannan tace " mutuniyarki zakice min, bata nan tana gurin aiki se nan da jimawa zaki ganta, k'ilama kiji shigowarta yanzu,  murmushi Umaisa tayi sannan tace "Allah sarki Aunty maryam ba dad'e ban ganta ba wllh, dariya ruman tayi sannan tace " wllh nima nayi missing d'in Aunty maryam. Dariya sukayi gaba d'aya sannan mama tace " indai maryam ce nasan duk inda take yanzu tana hanyar dawowa gida, kamar had'in baki kuwa se gata ta shigo perlourn da sallama, da gudu Umaisa ta nufeta tana fd'in oyoyo Aunty maryam d'ina i miss you so much wllh ta fad'a tareda yin hugging d'inta, hunging d'inta back maryam tayi tareda cewa i miss you too sweetheart, a haka suka k'araso perlourn hannun maryam sark'e cikin na Umaisa  murmushi kawai maryam takeyi har ta zauna a kan kujerar dake perlourn, sannan kalli khabeer tace "ya khabeer sannu da zuwa, ina yini?  Da sakin fuska ya amsa mata sannan ya maida kallonsa ga Beebah wadda ta gama cika fam kamar zata fashe,  mik'ewa yayi ya fita daga perlourn dan haka Beebah ta mara masa baya,  guiding d'in gidan ya nufa sannan yaja flastic chair d'in dake gurin ya zauna, bata da wani zabi dan taja kujerar itama ta zauna, tsareshi tayi da madaidaitan idanunta tana kallonsa, tabbas ita kanta tasan tana matik'ar son khabeer, amma kuma har yanzu ta kasa gane ainihin abinda ke cikin ransa a gameda ita, komai tayi dan ta burgeshi sam baya gani, wasu lokutan ma har takanji cewar halaiyarsa ta ko in kula dayake nuna mata yana matiqar bata haushi.  duk wannan zancen zucin da Beebah takeyi khabeer bema san tanayi ba,  danne dannen wayarsa kawai yakeyi.

Wayarsa ce ta d'au Ringing dan haka ya maida kallonsa ga me kiran, Mamien Umaisa ce take kiransa, dan haka da sauri yayi picking cikeda girmamawa yace " Mamie, daga b'angaren Mamie tace " khabeer dan Allah idan zaku dawo gida ka tahomin da maganin ciwon kan  da ka tab'a kawo min daga Asibitin ku, wllh ciwon kan ne ya matsa min dayawa, cikeda girmamawa ya

amsa mata da to mamie Allah ya sawak'e, yana kaiwa nan ya katse wayar tareda mik'ewa, kallon Beebah yayi sannan yace " toni zan wuce, idan kin shiga ciki kice musu su fito mu tafi, yana kaiwa nan yay hanyar perking space batareda yaji tacewarta ba. Da ido tabishi da kallo harta dena hangensa, komai nasa masifar burgeta yake,   Jikinta ne yay masifar sanyi dan haka ta mik'e ta nufi cikin gidan kamar kazar da k'wai ya fashe mata a ciki, bata jima da shiga ba su Ruman suka fito tareda maryam wadda ke rik'e da hannun Ameerah, har bakin motar ta rakosu sannan ta kalli ya khabeer tace " har zaku wuce da wuri haka ya khabeer?  Murmushi yayi sannan yace" ae wllh maryam wani uziri ne ya taso min, dariya tayi sannan tace "ta likita bokan turai,  murmushi kawai yayi batareda yace komai ba,

Ledar hannun ta ta mik'a musu wadda ke shak'e da coclet da kuma sweet kala kala, godiya sukai mata sannan yaja motar suka kama hanyar gida,  a bakin wani babban phamarcy yay parking, wayarsa ce ta fara Ringing, dan haka ya maida hankalinsa sosai a kan wayar, picking yayi tareda kara wayar a kunnensa, wata k'aramar takarda ya zara a cikin aljihun gaban motar sannan yayi d'an rubutu kad'an a jiki, mik'awa Umaisa dake gefansa yayi sannan ya zari 2k ya mik'a mata, karb'a tayi sannan ta bud'e murfin motar ta nufin cikin pharmacy d'in, tana zuwa ta mik'awa wata mata wadda ta gani sanye da farar riga, karb'a tayi sannan ta saka mata maganin a ledar ta mik'a mata.

Karb'a tayi sannan tayi mata godiya ta juya, wata mata ta gani hannunta rik'e da wani cute popy wanda yay masifar d'aukar hankalinta, sabida yanda ta shagala da kallon k'aramin karen harta iso k'ofar glass d'in bata sani ba, kawai seji tayi tayi karo da mutum,  jikinta ne ya d'au ki wani irin rawa sabida tsoro

Hakanne yasa tatafi da baya zata fad'i Runtse idanunta tayi da k'arfi tana jira tajita a k'asa, da wani irin mugun sauri ya tareta ta fad'o jikinsa.

*_Muje zuwa sisters yanzu aka fara wasan😁_*

_Comment_
Nd
_Share_

*Daga alqalamin Zm chubado✍*
_*🎀KIYARDA DANI...!🎀*_
🎀🐾🎀

*♝ IᗪTҼʅʅIGҼᗪT WɾITҼɾ'ى ASSᏇ📚✍️*

*💫DEDICATED: to Sis naja'art*

_*WRITING BY: Zm (CHuBaDo)*_

*✨Special Gift for Hafsat Hafnan (my jika),.*

_Page:13_

___________📖 Rintse idanunta ta sakeyi da k'arfi sabida yanda ta tsorata, k'urawa fiskarta idanu yayi yana kallon yanda lips d'inta ya tattare sabida yanda jikinta ke rawa, kallonsa ya mayar kan dogayen lashes d'inta, wa'yanda sukayiwa idanunta ado, hannunsa yasaka a daidai kumatunta sannan yay taping kad'an, cikin huskey voice d'insa yace "ke zaki bud'e idanunki ko kuma sena watsa miki mari?

A hankali ta fara bud'e manyan idanun harta gama bud'e su tsaf a kan Maheer, zaro ido tayi sosai tana k'are masa kallo, nan da nan kashedin daya rangad'a mata last 2weeks da suka wuce ya fara dawo mata tsaf a tunanin ta, tamkar a lokacin ya kora mata shi, nan da nan idanunta suka cika taf da k'walla, banda motsi babu abinda lips d'inta sukeyi, a zahiri so take tayi magana amma kuma ta kasa sabida yanda tsoronsa ya samu gurbi a cikin zucyarta yay kanekane, mik'ar da ita yayi har ya samu ta daidaita tsayuwarta sannan ya sake kallon ta a karo na biyu yace " hy Queen of tears, ko ki goge wannan hawayen naki marasa dalili, kokuma yanzu in saki kukan idan shi kike buk'ata.

Da sauri tasa hannu ta goge hawayen tareda turo d'an k'aramin bakinta gaba, matsowa yayi dab da fuskarta sannan ya k'yasta hannunsa sau biyu sannan yace " ohhh da alama kina so bakinki ya sake kumbura ne a karo na biyu. Da sauri ta dafe bakin da hannunta, sabida bazata tab'a manta irin azabar daya gana mata ba, wani miskilin murmushi ya saki sannan ya ratsa ta gefanta ya wuce, da sauri tasa hannu tura k'ofar glass d'an zata fice, muryarsa ya d'an d'aga yace " heeey Queen of tears, karki sake bari mu had'u dake a karo na uku. Ko juyowa ba tayi ba ta kwasa da gudu tayi waje, seda ta kusa isa parking space d'in sannan ta fara k'ok'arin saita nutsuwarta, k'ofar motar ta bud'e sannan ta shiga ta zauna, bisaga mamakinta setaga har lokacin yaya khabeer wayar yake be gama ba, wata sanyayyiyar ajiyar zuciya ta sauke sabida tasan da ace ba waya yake amsawa da tini ya farayi mata fad'an taje ta zauna Daga zuwa siyan magani, tana rufe k'ofar khabeer ya figi motar suka nifi hanyar gida.

Minti 15minute ne ya d'aukesu zuwa gida, a nitse suka gita daga motar sannan suka nufi cikin gida, babu kowa a perlourn se Usman da kuma Farouq, gefansa kuma Ummie ce ya d'ora kansa bisa cinyarta, ya tsina fuska Usman yayi sannan ya kalli Ummie yace "pls Ummie don

Allah ku d'aga tafiyar nan naku mana, wllh Ummie banaso ku bar gidannan babu masu dafa mana abin.... "Usman ka kiyayeni wllh kudai yaran nan wllh kunada samun guri, in banda iskanci bakune kukace bakwason masu aikin ba da kanku? Turo baki Usman d'in a shagwab'e tamkar wani k'aramin yaro yace "Eyyah Ummie nifa akan su Ruman nake magana pls kubar mana su muzauna tare mana inyaso ku sekuyi tafiyar ku da Dadyn, mu mazo daga baya idan sunyi hutu pls. Ya fad'a yana had'a hannunsa duka biyun yana kallon Ummie

Tab'e baki Farouq yayi sannan yace "Ummie wai yanzu don Allah har son zuwa gidan wannan jarababbiyar tsohuwar kukeyi? Ni wllh bana son zuwa Gano sabida fitinar matar tsohuwar nan, kana zuwa zata ishe ka yaushe zakayi aure, idan kace kai ba yanzu ba kuma tasawa Abba kukan gulma.

Kunnensa Ummie ta murd'a sannan ta buge masa baki tareda ture kansa daga cinyarta tace " ai wllh Hajiya Babba takeyi shine daidai, Allah yasa ma dukanku ta zab'o muku matan aure a can garin naku inyaso muga ta tsiya, tashi yayi kamar zeyi kuka yace "haba Ummie don Allah....!!!

Dariya Usman yayi sannan yace "heey. dude ka rabu da Ummie kawai, taya za'ai Classy gay's kamar mu muk'are da auren zab'in wannan tsohuwar. Dariya suka fashe da ita, suna shirin barin perlourn su Rumana suka kunno kai da sallama,

Da sakin fuska Ummie ta tarbesu amma kuma kallo d'aya tayiwa khabeer ta fahimci babu walwala a tareda shi, a dak'ile yace " Ummie ya gidan? Be jira cewarta ba ya nufi upstears, Direct d'akin Mamie ya nufa, da sallama ya shiga perlourn tareda lumshe manyan Golden Eyes d'insa sabida wani daddad'an k'amshin turaren wutar daya bak'unci hancinsa, babu kowa a perlourn se k'arar Tv, a hankali ya nufi k'ofar bedroom d'inta, a hankali ya fara knowking d'in k'ofar, be jima sosai ba ta bashi izinin shiga, a kwance ya sameta a kan Gado ta rufe duk jikinta da babban blanket, da sauri ya k'arasa bakin gadon tareda bud'e bargon kad'an, cikeda damuwa ya sanya hannunsa a kan goshin Mamie wadda jijiyoyin kanta sukan suka tashi sosai sabida ciwon dayake mata,

Mik'ewa yayi da sauri yabar d'akin, da sauri ya sakko, be tsaya yiwa su Ummie bayani ba ya nufi side d'insa,

abin Auna jini (Sphygmomanometer) da wasu abubuwan da duk ze buk'ata, da sauri ya fito ya sake wuce su Ummie wadda Rumana ke bata labarin Aunty maryam, da ido Ummie ta bishi amma kuma se bata kawo komai ba, da sauri ya k'arasa cikin d'akin ya sameta a yanda ya barta, yaye bargon yayi tareda kiran sunan ta, shiru yaji bata amsa ba, da sauri ya kara hannunsa a bakin hancinta, k'irjinsa ne ya buga da k'arfi, da wani mugun sauri ya kara kunnensa a saitin k'irjin Mamie n, a hankali yaji zuciyarta na harbawa, sedai na normal yanda na masu lafiya yake beeting ba, hannunsa yasa a satin k'irjinta yana dannawa ko numfashin ze dawo amma kuma shiru, mik'ewa yayi da wani mugun sauri ya fita yay downster, side d'insa ya koma ya d'akko wayarsa da ya bari a gefan gadonsa,

Tun kafin ya fito ya kira waya Asbiti a turo musu Amblance, kashewa yayi sannan ya fito perlourn, har ze wuce Ummie tace " wai kai lafiyanka kake ta faman zarya kamar kayiwa sarki k'arya?  Ba tareda ya juyoba yace "Ummie this is Emergency case, ciwon Mamie ne ya tashi..! Da sauri Ummie ta mik'e tabi bayansa, inda Ruman da Umaisa suka fara kuka, Farouq da Usman ne suka marawa su Ummie baya,  cikin mintunan da basu gaza 15ba motar Asbitin ta iso, nan da nan me gadi ya wangale musu Get suka shigo.

Wani dogon gado suka fito dashi daga motar sannan suka kunna kai zuwa cikin gidan, Rumana ce ta kaisu har d'akin sannan su Farouq da khabeer suka kamata suka d'ora a gadon, k'arar jiniyar motar Asibitin ce ta tayar da Ummah dake bacci, da sauri ta diro daga gadon ta fito, da wasu noses ta fara cin karo dan haka ta fahimci tabbas jikin Badi'atou ne ya tashi, babu abida take firtawa se innanillahi'wa'ina'ilaihirraji'un!!!!!!

A haka suka fito da ita sanbal a kan gadon, a gaggauce suka fito da ita sannan suka sakata a motar, khabeer ne ya shiga tareda noses din sannan Drivern ya figi motar suka nufi Genarel Hospital da ita..

_Commet_
_Nd_
_Share_

*Zm chubado, sushmer😂*

_*🎀KIYARDA DANI...!🎀*_
🎀🐾🎀

* ♟ ꀤꈤ꓄ꍟ꒒꒒ꀤꁅꍟꈤ꓄ ꅐꋪꀤ꓄ꍟꋪ'ی  ASSѡ📚✍️*

*💫DEDICATED: to Sis naja'art*

_*WRITING BY: Zm (CHuBaDo)*_

*✨Special Gift for Hafsat Hafnan (my jika),.*

*_haqiqa qauna halittace ta ubangijin al'arshil'azeem, shikadai ne wanda yake sanya soyayyah

a zukatan al'ummah har su samu damar nunawa wanda suke so qaunah,  SUMAYYAH UTHMAN ADAM, and NUSAIBA ALI MUHAMMAD,  ni Zm Chubado naga sakonku da kuma irin tarin addu'o'in alkhairin da kukayi min, Allah ubangiji yabar zumuncin alkhairi, nima ina sonku fisabilillah❤_*

_Page:14_

___________📖 suna isa Asbitin  suka fito da ita a gaggauce sabida yanda condition d'in nata is very worst, turata sukayi zuwa wani d'aki na musamman domin bata taimakon gaggawa, da sauri Khabeer ya kunna kai zuwa d'akin da aka shiga da Mamien, tun kafin Dr. Abas muhammad ya k'araso d'akin tuni Khabeer ya fara gudanar da abinda ya dace,

Har Dr. Abas ya shiga room d'in amma dukda haka babu wani cigaba da aka samu gameda daidaituwar numfashin nata,

da sauri Khabeer ya kalli noses d'in yace " ku bani 325 miligram (preferably uncoated) na Aspirin injection da sauri pls!!

Wani d'an isakan kallo Dr. Abas yake bin Khabeer dashi,  sannan yace "taya za'ai kayi mata Aspirin injection bayan kuma muna sa ran daidai tuwan numfashin ta a hakan?   Wani kallo Khabeer yayi masa sannan yace "a hakan kake zaton zamu samu daidaituwar numfashi a hakan? Kaduba fa kaga a irin condition d'in da take ciki malam,   karkayi min kallon mahaukaci malam, i'm a madical Doctor kamar yanda kake, ya k'are maganar yana  gyara zaman oxcigyn d'in dake fuskar Mamie,

Ba tareda ya kalli Inda Dr. Abas d'in yake ba yace " abinda yasa kaji nace abata Aspirin injection sabida, Aspirine can help break up the blood clot that is cousing the heart attack shiyasa, a matsayinka na likita ya kamata ka fahimci hakan!

Alurar ya karba sannan yayiwa Mamie batareda ya sake bi ta kan Dr. Abas ba,

Jikin Dr. Abas sanyi yayi sosai sabida betab'a zaton Khabeer likita bane, shiyasa yayi masa hakan, sauke duk wani girman kai dayake ji dashi yayi sannan  suka had'u duka su biyun akan Mamie,  duk wani taimakon daya kamata su bata sun bata, amma sam babau wani cigaba da aka samu, sabida har yanzu basu samu nasarar  daidaituwar numfashin nata ba,

Ja sukai da baya duka su biyun sabida yanda sukaga numfahin mamien yana sakeyin k'asa, daga  100 ya dawo 60, wani irin bugawa k'irjin Khabeer yayi, lokaci guda ya maida kallonsa ga Dr. Abas, dafa kafad'arsa kawai Dr. Yayi sannan yace "im sorry Dr. amma munyi iya bakin k'ok'arin mu, sedai kawai mubarwa Allah sau...........      Tun kafin ya rufe baki Mamie taja wani dogon numfashi, bisaga taimakon oxcigyn d'in dake manne a hancinta. Ajiyar zuciya suka sauke gaba d'yansu sannan suka k'arasa bakin gadon da suri, Allurar bacci Dr. Abas yayi mata

sannan ya bada umarnin a turata zuwa d'aki na musamman, sannan kuma kar'abar kowa ya shiga inda take har seta farka,

Cikeda gimamawa suka amsa masa, cikin mintunan da bazasu gaza 15ba suka kammala komai cikin tsari, sannan Dr. Abas yabi bayansu ya sanya mata Drip ya fito daga d'akin,

kusan a tare suka fito da Khabeer, wanda keta faman kalon su Usman wanda suketa safa da marya a reception d'in Asbitin, mamaki halin Usman da Farouq kawai yakeyi musamman daya hangi uwar gaiyar da suka kwaso suka taho da ita, Dr. Abas ne ya katseshi ta hanyar mik'a masa hannu alamar su gaisa,

Ba musu shima ya mik'a masa nasa hannun, da sakin fiska Dr. Abas yace i'm Dr. Abas muhammad Adam. Murmushi kawai yayi sannan yace " i'm Dr. Khabeer mahmoud muhammad, murmushin jin dad'i Dr. Abas yayi sannan yace " nice to meet you Dr. Khabeer. A haka suka fito reception d'in Khabeer na biyeda Dr. Abas d'in a baya, da Abba suka fara cin karo, cikeda damuwa ya nufi Dr. Abas d'in tareda tambayarsa jikin matar tasa, murmushi yayi sannan yace "karka damu Alhaji insha Allah komai zaizo da sauk'i amma kafin nan mu k'arasa office inyaso semu tattauna akan matsalar, ba musu Abba yabi bayansa inda shi kuma Khabeer ya nufi gurin su Ummie.

Da sauri Ummie da Mamah suka kama hannnunsa sukace " ya jikin nata? Kasa magana yayi sabida bema san ta inda zai fara gaya musu girman matsalar Mamien ba, da sauri Umaisa tazo ta fad'a jikinsa tareda sakin wani irin kuka kamar ranta ze fita!!! Kasa ce mata komai yayi sabida bema san ta inda ze fara rarrashinta ba yanda take kukan ne ya fara d'aga masa hankali, dan haka ya zarota daga jikinsa tareda sunkuyowa dab da fuskarta yace, " kukan ya isa haka don Allah, addu'ah zakiyi mata bawai kuka ba, insha Allah zataji sauk'i kinji ko? Ya fad'a yana share mata hawayen dake zuba a kan fuskarta. Kallonsa kawai Ummie takeyi sabida tasan baze tab'a gaya musu komai ba akan ciwon Badi'toun, kodan karya d'aga musu hankali ma baze gaya musu ba.

Dr. Abas ya kalli Abba yace " magana ta gaskiya Alhaji gaskiya mara lafiyar nan she's in critical condition domin kuwa ciwon nata yakai satage d'in da a yanzu tana tsakanin rayuwa da kuma mutuwa, dan haka ina mai baka shawar cewa ka daure ka kuma dage wajen kiyaye dukkan abinda ze d'aga mata hankali, sannan kuma seta dage wajen ragewa kanta damuwa kodan cigaban lafiyata. Amma insha Allah Alhaji komai zeyi daidai da yardan Allah. Ya k'are maganar yanyiwa Abba murmushi.

Tunda Dr. Abas ya fara magana zufa take ketowa Abba, dukda sanyin Ac n dake office d'in, babu abinda yake nanatawa se innanillahiwainna'ilaihirraji'un! Shin ta ina ze fara fuskantar wannan matsalar datake tinkaro su? Daurewa kawai yayi sannan ya mik'e yayiwa Dr. Abas d'in sallamah, tabbas yasan cewar dukkan musulmi mai imani yana tareda jarrabawar ubangiji, amma kuma idan yayi hak'uri seka ga Allah ya kawo masa d'auki! Wani irin tausayin Mamie ne ya cika masa zuciya, lokaci guda kuma hawaye ya cika masa idanu, fitowar dayayi daga office

d'in ne yaja hankalin Umaisa zuwa gareshi, da gudu ta nufeshi tareda fadawa jikinsa ta saki wani irin kuka,  a hankali ya dinga bibbiga bayanta alamar rarrashi sannan ya zareta daga jikinsa ya dinga bata haquri kafin ya samu tayi shiru.

Yana zuwa yacewa su Ummie su tattara su koma gidan kodan sabida yaran, a nan yake gaya musu Dr. Yace abarta ta huta se zuwa gobe zasu samu damar ganinta, ba yadda suka iya haka suka juya Farouq da Usman suka maida su gida, inda akabar Khabeer da kuma  Dady.

B'angaren Maheer kuwa tunda yabar pharmacy d'in be dire ko ina ba se gidansa dake unguwar Garki, a nitse yay perking motar sannan ya fito, da sauri Lawan mai gadi ya k'araso gurin, cikeda girmamawa ya yayi masa sannuda zuwa sannan ya koma bakin aikinsa,

murmushi kawai Maheer yayi sannan yay cikin gida abinsa, sosai yake jin dadin zamada Lawan, Direct bedroom d'in sa ya nufa takalmin  fatar dake Manne a k'afarsa ya fara cirewa, sannan ya mik'e ya fara  b'alle botir d'in gaban rigarsa,  yana kammalawa ya nufi kafceciyar wodrobe d'insa dake Manne a jikin katafaren bangon dake d'akin ya bud'e, wani had'add'en white towel ya d'akko babba sannan ya d'aurashi a k'ugunsa,

Nanda nan taswirar halitatarsa ta baiyana, haka kuma cikar zatinsa,  toilet ya shiga tareda sakarwa kansa ruwa, nanda nan tunani Abdul ya ya fara kwaranya a zuciyarsa, ya jima yana wankan sannan ya fito d'aure da towel a k'ugunsa, inda ya ratayo k'aramin towel bisa lallausar sumar dake kansa wacce keta faman d'igarda Ruwa, a bakin dresing miror d'in dake d'akin  ya tsaya, sannan ya fara goge sumar tasa da towel d'in, wasu tsadaddun mayuka ya fiddo na companyn OLAY ya fara shafawa, cikin mintuna kad'an ya kammala sannan ya shiya cikin wata black jallabiya qirar companyn Emraty wadda ta baiyana hasken fatarsa.

A hnkali ya nufi inda ya cire kayan dake jikin sa kafin ya shiga wanka, takalman ya fara kwashewa ya kaisu mazaunin su, sannan ya sunkuya ya d'auki rigar da kuma wandon,  wani cute basket ya bud'e ze jefa kayan, ba zato yaji kamar abu ya sokeshi daga jikin rigar, a nitse ya fara warware rigar dan ganin abinda ya soken shin,  bisa ga mamakinsa seyaga d'an kunnen mace, da mamaki ya d'aga d'an kunnen yana kallo tamkar wani me son tina wani abu,  d'an kunne ne k'irar indian fashtion me azabar kyau, se faman baza k'yalli yake, kalo d'aya zakayi masa ka fahimci me tsada ne.

Ya jima yana kalon d'an kunnen tamkar baze daina ba,  wani siririn tsaki ya saki tareda dukan bangon d'akin yafirta "Queen of tears, tareda datse lips d'in sa da hak'oransa.

Comment
Nd
Share

*Zm chubado*😁
_*🎀KIYARDA DANI...!🎀*_
🎀🐾🎀

*♝ IᗪTɵ||IGɵᗪT WrITɵr'ی ASSɷ📚✍️*

*💫DEDICATED: to Sis naja'art*

_*WRITING BY: Zm (CHuBaDo)*_

*✨Special Gift for Hafsat Hafnan (my jika),.*

_Page:15_

___________📖 wani siririn tsaki yaja tareda jin wani irin haushinta, a ransa yace "yarinyar nan bazata fita a rayuwata ba muddin ban nuna mata iyakarta ba, wani sirin tsaki ya k'ara saki lokaci guda kuma ya saki tattausan murmushi, tareda maida hankalinsa kan d'an kunnen dake hannunsa, k'ara fad'ad'a murmushinsa yayi, lokaci guda ya fara tuna had'uwarsu da Umaisa ta farko a Silverbeard, har zuwa yanzu da suka sake had'uwa da ita a phamarcy, komai na yarinyar idan tayi tana tuna masa da Abdul,

musamman yanda ya lura tanada saurin tsorata, abu kad'an ne yake firgita ta, babban abinda yasa yarinyar take bashi haushi guda d'aya ne yanda take da arahan hawaye, sabida a rayuwarsa ya tsani mutum me saurin kuka musamman ma mace, tab'e baki yayi tareda d'aga kafad'arsa, sannan yace " meyasa ma nake b'ata lokacina ina tunanin wannan urgly yarinyar bayan itama macece? Lokaci guda ya sakejin wani irin haushinta yana kwaranya a zuciyarsa, tsaki yaja mai sauti sannan yace "i have to teach her a gud lession wanda ko mai kamada ni bazata sake marmarin ta dinga bibiyar Rayuwarsa ba, a haka ya fice zuwa masallaci.

Abba ne ya kalli khabeer yace "A gaskiya lamarin ciwon nan na Badi'atou yana matik'ar d'agamin hankali, musamman yanda Dr. Abbas muhammad yayi min bayani akai!!!.

Murmushin k'arfin hali khabeer ya saki irin nasu na k'asaitattun likitoci, sannan yace " Abbah hak'ik'a jikin mamie wannan karon yayi tsanani sosai, sabida yanda take matsawa kanta gamida

sanyawa kanta damuwar datafi k'arfinta, wllh Abba muddin aka sake bari ta kuma shiga irin wannan halin to a kwai yiwuwar ta rasa Rayuwarta ma gaba d'aya, shiru Abbah yayi yana nazarin maganar khabeer d'in, murmushin k'arfin hali Abbh ya saki sannan yace "hak'ik'a kowani halitta a duniya yana da irin k'addarar da Allah yake jarrabarsa a Rayuwa, mai imani shine wanda yake karb'ar dukkan jarrabawar da Allah ya aiko masa, dan haka nayi imani da Allah haka kuma na mik'a dukkan amarina a gareshi, idan har wa'adin Badi'atou yazo koda ciwo ko babu ciwo wllh seta tafi, dan haka kadena fadin haka Son Allah dai ya bata lfy kwai.  Cikeda damuwa khabeer ya amsa da "Ameen Abbah, a haka suka suka fito farfajiyar Asbitin suna d'an tab'a hira jefijefi.

***********

*KADUNA STATE*

Abdul ne zaune cikin k'asaitaccen perlourn Maheer wanda a yanzu ya koma tamkar nasa, gefansa kuma tarin takardune da kuma  system, sosai ya mayar da hankalinsa akan system d'in, kalo d'aya zakayi masa kasan abinda yakeyi is importan, turo k'ofar perlourn akayi babu ko sallama, hakanne yasa ya mayar da dukkan hankalinsa ga k'ofar dan ganin wanda ya shigo d'in,

Hajiya Murja ce tareda wani saurayi a bayanta wanda baze wuce sa'an abdul d'in ba a tsaye, kallo d'aya yayi musu ya d'auke kansa tareda cigaba da abinda yakeyi,

Tabe baki tayi sannan ta kalli matashin saurayin tace "Mustapha kadaiga yanda perlourn yake ko? Fatana dai Allah yasa yayi maka, idan kuma bemaka ba se mukoma wncan part d'in ka zab'i wanda yayi maka tunda ba laifi gidan a kwai girma, ta k'are maganar tana kallon fuskar mustaphan,

Washe baki Mustapha yayi sannan yace "a'a Mama wllh nan d'in ma yayi min sosai, sabida komai ya dace da irin Zab'ina tamkar  wanda ya shirya perlourn yasan Zabin Raina, wani k'asaitaccen murmushi tayi irin na nuna isar nan sannan tace "nayi farin ciki daka zab'i nan d'in, dama kai ya dace ka zauna a ciki,   ga bedroom d'in can seka shiga da kayanka ciki, inayaso shikuma Abdul din seya tattaro kayansa da kuma sauran kayan D'angiyan yayan nasa ya koma d'akin waj....... "Enoug malama, Abdul ya katse ta cikin d'aga murya gamida zafin rai, nunata yayi da yatsa, sabida b'acin Rai jikinsa banda rawa babu abinda yakeyi, nan da nan zuciyarsa ta fara tafasa sabida magana data jefi yayansa kuma mafi soyuwa a zuciyarsa da ita, wani banzan kallo yake binta dashi sannan yace "heeey you wiked women, stop saying wa'yannan banzayen maganganun  naki akan Yayana, idan ba hakaba wllh i will teach you a good lession wanda harki mutu you will never foget it in your life....! Ya k'are maganar yana dukan k'aramin table d'in glass d'in dake gabansa cikeda tsantsar b'acin Rai.

Kasa magana Hajiya murja tayi sabida tsabar yanda ta firgita da lamarin Abdul d'in, a Ranta tace " au ashe dama yaron nan shima dan iskan kansa ne ban sani ba! To kodai shima ya fara

shan wani abunne?? tabbas na rabu da bukar kuma ga habu an haifa..... "Mama ya zaki tsaya yaro k'arami yana gaya miki magana tamkar wata sa'arsa, wllh mama bazan k'yaleshiba sena koya masa yanda ake girmama manya, Mustapha ya fad'a cikeda b'acin Rai, tareda nufar inda Abdul ke tsaye!

Murmushin mugunta Abdul ya saki tareda fara k'ok'arin kwancen belt d'in Wandonsa, da sauri Hajiya murja ta fara k'ok'arin tsaida mustapha, sabida harga Allah ta gama tsorata da lamarin Abdul d'in, musamman yanda takaga jikinsa har wani rawa yakeyi kamar ana kad'a masa gangi,

A fusace Abdul yayi kansa, nan suka kaure da fad'a, abinka da maji k'arfi nan da nan Abdul ya had'awa mustapha jini da majina, seda yayi masa lilis sannan ya k'yaleshi, banda ihu babu abinda Hajiya Murja takeyi wai Abdul ze kashe mata d'a, har farfajiyar gidan ta fita tana ihub neman d'auki, amma kaf ma'aikatan gidan babu wanda ya kalli inda take ballema tasa ran zasu taimakawa mustaphan, haka ta gama kururuwarta babu wanda ya saurareta dan haka ta kwasa da gudu ta koma perlourn,

A fisace Abdul ya kinkimo jakar mustapha ya jefata waje tareda jifansa da wani irin kallo wanda yafi kamada na muzanci sannan yace " dalla malam tattara sauran k'azantar ka ka fice daga prlourn nan tun kafin nayi maka lahanin da Uwarka zata kasa ganeka!!

Sannan ya sake nuna Hajiya Murja da yatsa yace "kekuma daga yau zan nuna miki cewar nima cikakken d'an bariki ne, ta yanda zan gagari duk wani motsinki a rayuwa, ke barima kijima na fad'a miki wllh yanda kika saka zuciyata ta d'an d'ani bak'in cikin abinda kika dad'e kina aikata mana wllh kema sena sakaki kuka da idonki, ya k'are maganar yana huci...!!

Da sauri mustapha ya fara yunk'urin tashi daga inda yake kwance, hancinsa banda jini babu abinda yakeyi, Rungumeshi Hajiya Murja tayi tareda rushewa da wani sabon kuka, sannan ta kalli Abdul tace " tabbas nayi sake d'an zaki ya girma, ammafa ka sani haryanzu sunana Murja ban canza ba, kamar yanda ba'a canzawa tuwo suna, Narantse da Allah wllh sekayi nadamar wannan abinda ka aikatawa wannan yaron, haka kuma sena sa shigowa gidannan ta gagareka bama iya wannan perlourn ba, zan nuna maka cewar wanda ya rigaka kwana dolene ya rigaka tashi, ta k'are maganar tareda jan hannun mustapha suka nufi k'ofar fita daga perlourn tana huci kamar wata macijiya, harta d'ora hannunta akan handile d'in k'ofar zata murd'a Abdul yace " heeeeyyy wiked women, lets start the game with killer smile. K'ura masa idanu tayi zuciyarta na tafasa kamar zata mutu sabida bak'in ciki,

Tana fita motarta suka shiga itada Mustapha dan takaishi clinic, a fisace tayiwa motar key sannan figeta zuwa get, nan da nan mai gadi ya wangale mata get ta danna hancin motar zuwa waje, wani baban pravet Hospital suka nufa dake cikin Malali, cikin mintuna kad'an suka karb'i Mustaphan tareda bashi taimakon gaggawa, seda suka tabbatar jinin dake zuba daga hancinsa ya tsaya sannan suka rubuta masa magunguna harda pain Reliever a ciki suka sallamesu suka nufo hanyar gida, tun a hanya Hajiya Murja take neman layin wayar Dady amma kuma ta kasa samunsa, hakan ne yake matik'ar k'ara bata takaici.

B'angaren Abdul kuwa, tun bayan fitar Murja ya shiga zarya a d'akin yana tinanin ta yanda ze b'illowa al'amarin tun kafin Dady ya dawo, yana tsaka da wannan tunanin ne yaji k'arar tsayuwar motar Dadyn, k'irjinsa ne ya buga da k'arfi amma kuma ya dake, cikeda makirci Abdul ya fara k'ok'arin k'ak'alo hawaye, kasancewar yanada arhan hawashi cikin mintuna kad'an kuwa ya fara ambaliyar hawaye kamar an kunna fanfo, A haka ya fito fito daga part d'in hanayensa rik'e da cikinsa yana wani irin kuka tareda kiran sunan Dady, tun kafin Dady ya ida fitowa daga motar yakejin ihun Abdul, A rud'e Dady ya bud'e murfin motar tun kafin Driver ya gama parka motar,

Abdul na k'yalla ido yaga yanda Dadyn ya gama rud'ewa ne yasa ya wani fad'i k'asa yana juyi kamar wanda za'a zare masa Rai, da wani irin mugun gudu Dady ya isa gurin da Abdul yake kwance, in les than 2minute ma'aikatan gidan sun zagayesu, hakanne yay daidai da k'arasowar Hajiya Murja, wani mahaukacin horn ta saki, ba shiri Bala mai gadi yaje ya bud'e mata get d'in, cikeda k'warewa ta danno hancin motar zuwa farfajiyar makeken gidan, tun kafin ta k'arasa parking space ta kashe motar, wani irin ihu Abdul ya sake saki tareda narkewa a jikin Dady tareda k'ank'ameshi yana kuka kamar gaske, hakanne yajawo hankalin Hajiya zuwa gurin, tsaki ta saki tareda k'arasawa dan ganin abinda ke faruwa,

Tana zuwa gurin tayi truss tareda bin Abdul d'in da kallon mamaki, cikeda gadara tace "tace haba Alhaji don Allah wai meyasa kaketa biyewa wannan yaron har haka ne? Wllh ba wani ciwo dayake damunsa kawai tsabar k'warewa ce a iya Drama, ka dubafa kaga irin dukan da yaron nan yayiwa mustapha kamar ze kashemin shi, sannan kuma dan renin hankali ya wani zo yana juyi kamar wanda za'a zarewa rai? ta fad'a tanata faman hura hanci kamar wata zakanya,

Shiru Dady yayi yana kallonta sabida mamakin halinta yama kasa magana gabad'aya, " Alhaji ka gafarce ni don Allah, amma dole ne mu fadi gaskiya akan ainihin abinda ya faru, Musa ya fad'a, sannan ya cigaba da cewa "magana ta gaskiya wancen yaron shiya fara takalar me gidanmun Abdul da fad'a, amma kuma duk da haka Abdul d'in be kulashi ba, daga k'arshema shi mustaphan muka gani ya dunk'ule hannu ya gabzawa Abdul d'in a ciki kamar ze kasheshi, tun daga nan Abdul ya yanke jiki ya fad'i a bakin k'ofar part d'in mai gida Maheer, cikin ikon Allah kuma se gaka nan ka dawo.

kallonsa kawai Hajiya Murja takeyi tareda sakin baki,

kauda kai Musa yayi da sauri sabida kallon datake binsa dashi sannan ya kalli abokan aikinsa yace "koba haka akayi ba?

Da sauri suka amsa da tabbas kuwa Musa haka akayi akan idonmu akayi komai, kallonta ta mayar kan Abdul a ranta tace " lallai tsugune bata k'aremin ba, hakanne yay daidai da saukar idonta cikin na Abdul, wani d'an iskan kallo ya jefa mata taredayi sakar mata wata uwar harara, a fisace taja hannun Mustapha sukayi cikin gida, inda shi kuma Dady suka kama Abdul suka sakashi a mota dan su kaishi Asbiti.

*GENERAL HOSPITAL ABUJA*

Mamie ce kwance kance bisa d'aki na musamman, gefanta kuma Ummie da kuma Mama, se kuma Ameerah daketa faman zuba surutu, A haka su Ruman da Umaisa suka shiga d'akin hannunsu d'auke da manyan ledoji wa'yanda ke shage da kayan marmari,    da sallamah suka shiga d'akin,  mamah ce ta amsa musu sallamar sannan tace "tun d'azu se yanzu kukai R'ayin isowa aida kun sani ma kunyi zamanku  tunda muma yanzu zamu tafi gidan, Ummie ce ta karb'a maganar tace " hmm kina manta sha'anin Drivern nasu, ekace bakisan halin Farouq da shirita ba, hakanne yayi daidai da Shigowar Farouq d'in  dan haka ya kwabe fuska yace "Eyyah Ummie nine ma shiriricin😕 ?

Dariya su Ruman suka saki ciki kuwa harda Mamie wadda ke kwance tana jinsu, masha Allah jikin Mamie yayi sauk'i sosai, sedai yanayin jikin baikai a basu sallama ba shiyasa  aka bari ta sake warwarewa sannan a sallamesu.

*Comment*
*Nd*
*Share*

_*🎀KIYARDA DANI...!🎀*_
🎀🐾🎀

*♝ IᑎTеⅼⅼIGеᑎT WrITеr'ی ASSѡ📚✍*

*💫DEDICATED: to Sis naja'art*

_*WRITING BY: Zm (CHuBaDo)*_

*✨Special Gift for Hafsat Hafnan (my jika),.*

_Page:16_

___________📖 Hira suka dingayi suna dariya duk dan su d'ebewa Mamie kewa, ko babu komai zata rage yawan damuwar datake damunta,  a haka khaber ya shigo d'akin ya samesu,

kallo d'aya zakayi masa ka fahimci a kwai gajiya a taredashi,  d'aya daga cikin flastic chair dake d'akin yaja ya zauna, sannan ya gaida su Ummie,

Kansa yad'an shafa sannan ya mik'e zuwa kusa da gadon Mamie, hanunta ya kama ya rik'e gam a cikin nasa, sannan yace "Mamie ya jikin naki?  Murmushi Mamie tayi sannan tace "da sauk'i sosai Babana, ya gajiyar d'awainiya kuma?  B'ata fuskan khabeer yayi yace "haba Mamie don Allah, kemafa kamar Uwa kike a gurina, ban tab'a banbanta matsayinku keda Ummie ba a cikin zuciyata, badan komai ba sedan irin  d'inbin soyayyar da kika nunamin a rayuwata Mamie, i beg you Mamie karki sake fadar haka na rok'eki plss!

Wata kwantacciyar kwallace ta tasowa Mamie, da sauri khabeer ya girgiza mata kai alamar kartayi kuka sabida condition d'in ta,  damk'e hannunsa Mamie tayi batareda ta sake ce masa komai ba, inda a ranta take girmama irin k'aunar da khabeer d'in yake nuna mata a matsayinta na kishiyar mahaifiyarsa, amma dukda hakan yaran basa wani nuna banbanci a tsakanin ta da iyayensu.  Shirun da khabeer yaji yayi yawane yasa ya kalli Ummie yace " Ummie mamie kuwa taci abinci? Murmushi ta sakar masa sannan tace 'Ae taci sosai ma, a haka Dr. Abbas ya shigo d'akin ya samesu,

Da sakin fuska ya mik'awa khaber hannu suka gaisa, sannan ya kalli su Ummie dake zaune ya gaishesu, Ruman ce ta fara gaisheshi sannan Umaisa ma ta gaida Dr. Abbas d'in, murmushi yayi sannan ya kali khabeer yace Dr. Khabeer ka tattara iyalanka kuje zuwa waje sabida zan gana da mara lfy ta.

Murmushi kawai khabeer yayi tareda kallon su Ummie yace "iyalan Alaji Abba zakace bawai iyalan khabeer mahmoud muhammad ba. Ya fad'a yana dariya,

sosai abin yabawa Dr. Abbas dariya, a ransa yace lallai khabeer baka da dama wllh,  amma kuma a zahiri yanayin rayuwarsu da iyayensa tana bala'in burgeshi, musamman yanda suke wasa dakuma dariya a tsakaninsu, sekace wasu kakanni da  jikokinsu,

Suna fita wata nurse ta shigo d'akin hannunta d'auke da wani babban faranti me d'auke da magunguna da kuma injection da drip a ciki, da sakin fiska victoria ke tambayar mamie ya jikin ta?  Sosai mamie taji dad'in hakan harta kasa b'oyewa, a haka Dr. Yayi mata Alurar sannan ya mak'ala mata ragowar Drip d'in daya rage,  tun kafin ya gama saka mata drip d'in bacci yay awon gaba da mamien, sabida a cikin Alluran da akwai me saka bacci, koda su Mama suka dawo d'akin a haka suka sameta tanata kwasar bacci, don haka suka tattara suka bi Farouq ya maida su gida, inda sukabar Umaisa da kuma Ruman.

*KADUNA STATE*

Wani babban Asbitin kudi Dady yasa drivern sa ya kaisu, kasancewar ansan da zuwansu cikin mintunan da bazasu gaza biyarba suka karb'i Abdul cikin gaggawa,  wani d'aki na musamman suka nufa dashi don bashi taimakon gaggawa, lak'amewa Abdul yayi sekace wani mara lafiyan

gaske, ko motsin kirki bayayi illa hannunsa kawai daya d'ora bisa kan cikinsa yana juyi kamar ze mutu, Latsa cikinsa likitan yake ta famanyi cikeda k'warewa gamida son gano abunda ke damunsa, k'yallara ido Abdul yayi kad'an don ganin adadin mutanen dake d'akin gudun karya b'ata wasansa, ganin babu idon sani a ciki ne yasa Abdul yay zumbur ya mik'e yace "haba Dr. Don Allah, irin wannan matsamin cikin da kakeyi ai seka fasamin hanjin ciki, ya fad'a yana gyara zaman rigar dake jikinsa, hannun Dr. Ya kama sannan yace pls don Allah ina so nayi ganawar sirri dakai pls Dr. ! Ya fad'a yana wani shanye idanuwa kamar gaske.

Ba musu Dr. ya amince da batun Abdul d'in inda ya buk'aci da nurses d'in su fita su barsu, haka kuwa akayi, suna fita Abdul ya sanar da Dr. Uzirinsa tareda tarin hujjojinsa nayin hakan, sosai jikin Dr. Yayi sani dajin irin labarin k'aryar da Abdul ya zuga masa, nan da nan ya amince akan zai taimaka masa tareda bashi tarin goyon bayansa, wani mugun murmushi Abdul ya saki, a zuciyarsa yace i'm comming 4 you whitch, a zahiri kuma ya wani marairaice yace "pls Dr. Don Allah kasan yanda zakayi da babana sabida karya gane komai pls! Murmushi Dr. Yayi sannan yace " karka damu nasan ta yanda zan b'illowa al'amarim, insha Allah kuma zamu sami abinda mukeso, Rungumeshi Abdul yayi tareda share munafukar k'wallar dake idonsa.

Dr. yana fitowa daga d'akin ya kalli Dady yace "Alhaji muje office, ba musu Dady ya mara masa baya suka nufi office d'in likitan, wanda naga an Rubuta Dr. Hashim a jikin k'ofar, suna shiga Dr. Ya kalli Dady yace" ka zauna mana Alhaji, ba musu Dady ya zauna dukda cewar zuciyarsa babu nutsuwa a cikinta hakan bai hanashi zaman ba, sometimes yakanji wani irin abu a saman k'irjinsa tamkar an d'ora masa dutse a kai, sedai har zuwa yanzu ya kasa gane actueal abinda ke damunsa, musamman idan ya kalli Abdul wanda yake ganin tamkar wani babban jigone a Rayuwarsa, so tari idan ya kalli Abdul d'in yakanji wani bak'on al'amri a tareda yaron, sab'anin wasu lokutan kuma da yakanji cewar baya k'aunar ganinsa ma gaba d'aya. Katse masa tunani Dr.Hashim Yayi ta hanyar cewa" Gaskiya Alhaji Yaronka yana cikin wani hali, duba da irin ciwon dake shirin kamashi, wanda yake tamkar wata babbar barazana ce a cikin Rayuwarsa, don haka sekun kula sosai dashi, duba da irin matsalar dayake fama da ita, dole ne ku kiyaye b'acin Ransa, sabida idan har kuka bari Ransa ya b'aci a kwai wata jijiya dake tsakanin mahad'ar kansa da kuma k'wak'walwarsa, wadda idan jinin dake gudana ta jikinta ya tsaya tofa ze dingayin abu tamkar wani mahaukacin zaki, wanda idan baku mik'e tsaye bama ze iya zame masa tamkar hauka.

Zaro ido Dady yayi yace "Hauka kuma Doctor? Batareda Dr. Hashim ya kalleshi ba yace " tabbas kuwa Alhaji, don haka you have to very carefull. cikeda kad'uwa Dady yace "insha Allah zamu kiyaye, fatana dai Allah ya bashi lfy, murmushi Dr. Yayi sannan yace " karka damu insha Allah komai zeyi daidai, da zarar Drip d'in da muka saka masa ya k'are zamu sallameku zuwa gida.

mik'ewa Dady yayi tareda yiwa Dr. Godiya ya fita, chages d'in kudin yaje ya biya sannan ya koma reception d'in Asbitin ya zauna tareda yin shiru, duniyar tunani ya tsunduma ciki, zuciyarsa cikeda son tuna wani abu wanda har yanzu ya kasa tuna menene shi, so tari idan ya zauna haka yakeyi, amma dukda haka har yau ya kasa tuna komai, wasu lokutan sedai kawai

jikinsa ya dinga bashi cewar  tabbas a kwai abinda ya rasa a cikin Rayuwarsa mai matik'ar mahimmanci wanda ya kasa tuna ko menene shi,     *(niko nace babu abinda ke damunka se kewar gudan jininka Maheer!!!)*

Se wanjen magrib aka sallamesu zuwa gida,  tun a hanya Dady yake tattalin Abdul d'in, inda a zuciyar Abdul hakan yayi masa dadi sosai, dukda cewar yana mugun jin tausayin mahaifin nasa, sabida tunda ya dawo gida be samu ya huta ba ballantana ya samu damar cin abinci, amma kuma ta wani bangaren na zuciyarsa dad'in haka yajii, sabida ko babu komai  ze samu damar cin Uwar su Binta 'yar kwabo da kuma uwar gaiyar tasu wato Hajiya murja da tawagar da suke tara musu a cikin gida.

Tofa lallai Abdul zaka kirawa kanka ruwa😂

*ABUJA*

A kwana a tashi babu wuya a gurin Allah, haka kuma kullum kwanakin mu k'arewa sukeyi Batareda mun ankare ba,  a yau aka sallami mamie suka koma gida, sosai jikinta yayi sauk'i, dan haka ta kwantar da hankalinta cikin iyalinta tareda ragewa kanta damuwa, a haka rayuwar gidan ta dinga tafiya daidai kamar yanda suka saba, bayan sati biyu da sallamo Mamie Abba yace su shirya zasuje Gano don su gaida mahaifiyarsar,  sosai su Ruman suka dinga murnar tafiyar sabida har ga Allah sunyi kewar kakar tasu,

Wani mugun kallo khabeer yake binsu dashi, sabida ganin yanda suketa uban Rawar kan zasuje Gano, don haka ya kalli Abbah yace" Abbah banda su Ruman zasuje sabida a kwai makaranta dan haka su hak'ura kawai idan sun samu hutu se Driver ya kaisu, k'ura masa ido kawai su Ruman sukayi sabida  jin irin manakisar da yayan nasu yake shirin k'ulla musu,  Abba ne ya katse musu tunani ta hanyar cewa " hakane kam khabeer, hak'ik'a kayi magana me kyau, Ruman suka bari idan kun samu hutu seku tafi dasu Usman insha Allah,   kukuma Badi'atou seku shirya  gobe Driver seya kaiku. A haka taron ya tashi Umaisa se faman cika take tana batsewa sabida takaicin yayan nata,

Washe gari tunda sanyin safiya su Ummie suka gama shirin su, inda Ruman  taketa hawayen takaicin an hanasu binsu Ummie, Umaisa kuwa k'in fitowa ma tayi, sabida bazata jure ganin tafiyar tasu ba, Ameearh kuwa banda d'agawa Ruman hannu babu abinda takeyi tana murna, a haka Motar su Mamie tabar harabar gidan, kafin su dau hanya seda suka tsaya  a wani babban super maket suka jingi kayan abinci da kuma na tsarabar da zasu kaiwa mutanan Gano sannan suka d'auki hanyar Garin Kano,

B'angaren Maheer kuwa zaune yake cikin motarsa k'irar Formatic, sanye yake cikin wani farin yadi anyi masa d'inkin jamfa, dukda cewar kansa babu hula hakan be hanashi yin kyau ba, lallausar sumar dake kensa ya shafa har zuwa gemunsa wanda yayiwa zagayayyiyar fuskarsa ado da k'ara mata haiba, cikeda k'warewa yaje tukin harya iso Zone E d'in, wayarsa k'irar

sumsung ya zaro daga aljihun gaban motar tareda k'ok'arin kashe map d'in daya kunna dan yi masa jagora,  fitowa yayi cikin takusa me cikeda izzah gamida tak'ama, a kan boot din motarsa ya zauna tareda k'arewa Unguwar kallo agogon Rolex d'in dake d'aure a hanunsa ya kalla tareda jan wani siririn tsaki, tabbas yasan nanne legislative Quaters Unguwar su  Mujaheed amma sedai baze iya gane gidan ba sabida wasu sauye sauyen da aka samu,

hankalinsa ya mayar zuwaga wayar dake hannunsa, wata numver naga ya lalaubo wadda aka rubuta Mujaheed a jiki, be jimaba ya kara a kunnen sa,  tareda gyara zaman takalmin fatar dake k'afarsa,

Bugu d'aya Mujaheed ya answer tareda fad'in Lamido badai harka iso ba?  Tab'e baki Maheer yayi tamkar Mujaheed d'in yana kallonsa sannan yace " Yeah nazo mana amma kuma wllh idan baka fito da wuri ba yanzu zan san inda dare yayimin, dariya mujaheed yayi sannan yace "kaida bazaka tab'a canzawa ba Maheer,  katse kiran Maheer yayi tareda maida hankalinsa kan wani babban Get dake mak'otaka da inda yayi parking, wanda ake k'ok'arin bud'e k'aramar k'ofar dake jikin get d'in,  beautiful legs d'inta ta fara sanyowa, wa'yanda ke sanye cikin wani bak'in silipers k'irar companyn Vinci, fuskarta babu alamun dariya ko kad'an, sanye take cikin  wani brown yuniform wanda yay masifar yi mata kyau, dukda cewar doguwar rigace a jikinta da kuma babban hijab wanda ya tsaya mata a daidai gwiwarta hakan bai hana fitowar  shap d'inta fitowa ba, inda hannunta na dama yake rataye da wana cute jaka mai d'aukeda Al-Qur'ani mai gima gamida sauran litattafan addini, a hankalj take tafiya tana tura baki, da alama ba'a son Ranta zata makarantar ba, a hankali take takawa tamkar wahainiya sabida k'asaita  harta iso ta gefansa zata wuce, kauda kansa yayi da sauri, a ransa yace "amma wannan a kwai maiyar yarinya wllh, inba masifa ba wai meyasa bazata fita a cikin rayuwarsa bane?  Katse tunani yayi ta hanyar dirowa daga saman boot d'in dayake zaune, hakanne yay daidai da isowarta  gurin motar, shan gabanta yayi da sauri, hakanne yasa ta d'ago daradaran idanunta ma'abota haske ta saukesu a kansa, wani irin dogon numfashi taja a matik'ar tsorace tareda tafiya luuuuu zata fad'i.....

_Comment_
And
_Share_

*Zm chubad'o*😁
_*🎀KIYARDA DANI...!🎀*_
🎀🐾🎀

*♝ IᗪTᏋ|||GᏋᗪT WrITᏋrʾی ASSᏇ📚✍️*

*💫DEDICATED: to Sis naja'art*

_*WRITING BY: Zm (CHuBaDo)*_

*✨Special Gift for Hafsat Hafnan (my jika),.*

*_A yau sadaukarwar ta babban abokina ce, kokuma ince abokin fad'ana😂. Yau gagarumar kyautar takace HUSSAIN 80k, wannan shafi kyuta ce a gareka don hka na mallaka makashi halak malak_*

*_Gareku masu yad'a cewar soyayyace a tsakanina da Hussaini 80k wannan ba gaskiya bane, magana ta gaskiya itace babu soyayya ko kuma wani abu me kamada haka a tsakanina dashi banda mutuntawa, dan haka don Allah masu yad'a wannan maganar qaryar kuji tsoron Allah ku dena pls🙏_*

_Page:17_

___________📖 tafiya tayi gabad'ayanta zata fad'i lokaci guda kuma idanunta suka fara rufewa tamkar wacce ke shin suma, cikin zafin nama Maheer ya jawota da dukan k'arfinsa, bata dire a ko ina ba se akan faffad'an k'irjinsa, wani irin abu ne ya tsirga masa tundaga kan babban yatsansa har zuwa tsakiyar kansa nan da nan zuciyarsa ta sark'e da wani bak'on Al'amari wanda k'wak'walwarsa da kuma tunaninsa suka kasa fassara masa shi, hak'ik'a malam kimiyar soyayya sunyi gaskiya da suke cewa" abinda baki ya kasa isarwa, to babu shakka gabbai suna isar dashi yayinda suka had'u da junansu a guri guda, fuskarta ya zubawa idanu tamkar a yau ya fara ganinta, tunda yarinyar ta shigo cikin Rayuwarsa ya kasa gane dalilin dayasa take tsaya masa a rai koda kuwa ace be ganta ba, isowar Mujaheed gurin ne yasa Maheer ya farka daga duniyar tunanin daya afka, lokaci guda kuma ya saketa ta fad'i k'asa, fad'uwar datayi ne yasa ta bud'e idanunta da sauri tana zaresu cikeda tsoro, kallonta Mujaheed yayi tareda kiran sunanta yace "Umaisa are you allright? Kallonta ta mayar kan Mujaheed d'in tareda fashewa da wani irin kuka tace "pls ya Mujaheed tsoro nakeji, wllh tsoronsa nakeji, don Allah ka fad'a masa ya fita a rayuwata ya dena tsoratani haka plsssss ya Mujaheed!!! Ta fad'a tareda saurin mik'ewa tsaye, duk yanda taso ta tsaida kukan tayiwa Mujaheed bayani kasawa tayi, don haka ta figi jakarta ta nufi gida da gudu tana kuka.

A yau karo na farko a rayuwar Maheer yaji cewar be kyauta ba daya zamo silar zubar hawayen yarinyar, haka kawai seyaji zuciyarsa dukta dagule masa, dafashi Mujaheed yayi tareda fad'in "friend a ina kasan Umaisa pls?   Tab'e baki Maheer yayi tareda d'aga kafad'unsa yace " a ina

kuwa na santa banda a nan gurin? Nifa ban tab'a ganinta ba se yanzu,  kallon tuhuma Mujaheed kebin Maheer dashi sannan yace " baka santa ba kace friend? Amma kuma in har baka santa ba ya akai take cewa ka fita a rayuwar ta, sannan kuma meyasa ka tareta a lokacin datake k'ok'arin  fad'uwa?

Kallon tsaf Maheer keyiwa Mujaheed sannan yace "  don zata fad'i na tareta wannan bashi yake nuna alamar nasanta ba Mujaheed, kowama zan iyayi masa hakan a matsayin taimako, sannan kuma maganar in fita a rayuwarta kuma wannan shirme ne kawai irin na mata, wata k'ila ko tatab'a ganin mai kamada nine a mafarkin ta shiyasa take fad'ar hakan, ya k'are maganar tareda d'aure fuska tamau, shi'a dole beson renin wayo.    Shiru Mujaheed yayi yana bin Maheer d'in da kalon mamaki a ransa yace "amma Maheer a kwai cikakken d'an duniya, dubi yanda ya had'e rai tamkar besan wani abu waishi dariya ba.  Tab'e baki kawai yayi sannan yace masa "muje.

Suna shiga gidan direct maine parlourn gidan suka nufa dan Maheer d'in su gaisa da Ammi mahaifiyar su Mujaheed, da sallama suka shiga perlourn, babu kowa a parlourn se Shahida k'anwar Mujaheed tana kallon wani indian series a tashar Zeeworld, sosai ta mayarda dukkan hankalinta ga Tv, shiyasa duk sallamar da suke zabgawa ma bataji su ba, har Mujaheed ya shigo tsakiyar perlourn bata lura dashi ba, don Haka a fusace ya d'au remote d'in dake ajiye bisa rantsatstsiyar Royal chair d'in da sukayiwa perlourn Qawanya ya kashe Tvn, se'a lokacin ta lura dashi, kamar zatayi kuka tace " pls ya mujaheed kaban rimote  d'in na k'arasa kalla kar'ayi min nisa plssssss, ta wani ja pls d'in. Had'e rai yayi tareda galla mata harara yace "dilla can rufewa mutane baki, ai dama na lura dake na abinda kika iya se kallon film,  wllh idan kikai wasa sena hanaki kallon gaba d'aya, ya k'are maganar yana binta da harara, mik'ewa tayi tana wani tura baki kamar zatayi kuka ta nufi hanyar khitchine, a kausashe yace "inkinso ma ki mutu don Allah sabida haushi, shiru kawai maheer yayi yana kallon dramar da sukeyi tsakanin Mujaheed da kuma Shahidah,  haka kawai seyaji sun tuna masa da Abdul d'insa, juyowa shahida tayi se'a lokacin taga Maheer, washe baki tayi tareda k'arasawa inda yake tace " lah ya Maheer kaine yau a gidan mu, lallai shiyasa ashe naketa jin ana iska ashe mahadin kaduna ne ya shigo Abuja. Ta fad'a tana dariya sosai,   shima Maheer dariyar yayi sannan ya kalleta yace" au nine ma Mahadin ko??

Dariya tayi sannan tace "ae mana sabida wahalar gani dakai, shiyasa na kiraka da Mahadi me dogon zamani, hararartа Mujaheed yayi sannan yace " to suda  uwar zance  zoki kira mana Ammi a d'aki, tab'e baki tayi sannan ta fara tafiya, seda ta tabbatar kai hanyar da zata kaita d'akin Ammi sannan tace " indai ni sudace to wllh gado nayi a gurin yayana Mujaheed. Tana kaiwa nan ta arce sabida karya biyo ta, dariya Maheer ya kwashe da ita sannan ya Qaraso parlourn ya zauna suna jiran fitowar Ammi.

*Afwan bana samun tim sosai, don Allah kuyi haquri da wannan.*

_Comment_
Nd
_Share_

_*🎀KIYARDA DANI...!🎀*_
🎀🐾🎀

*♝ IᎠTЄ|||ĠЄᎠT WrITЄr'ی ASSѡ📚✍️*

*💫DEDICATED: to Sis naja'art*

_*WRITING BY: Zm (CHuBaDo)*_

*✨Special Gift for Hafsat Hafnan (my jika),.*

_Page:18_

___________📖Basu wani dad'e suna jira ba se gata ta fito, sanye take cikin wata doguwar rigar shadda, anyi mata d'inkin sinigalis, da fara'a ta k'araso parlourn tana fad'in lale maraba da d'ana Maheer, ta fad'a tareda fad'ad'a fara'ar dake kan fuskarta,

Sunkuyarda kai Maheer yayi cikeda jin kunyar Ammin sannan ya gaisheta tareda tambayarta ya samesu lafy? Da kulawa Ammi ta amsa tareda "fad'in ya mutanan gidan naku, fatan duk suna lfy? Murmushi yayi wanda iyakarsa lips d'insa sannan yace" duk suna lfy Ammi,

Murmushin jindad'i ta saki sannan tace " masha Allah, wannan karon bakazo da sarkin tsokana ba kenan? Dariya mujaheed yayi sannan yace" Ammi wai Abdul kike magana? Ai yanzu da zakiga Abdul wllh Ammi bazaki ganeshi ba shakiyi, ya fad'a yana murmushi, zaro ido Ammi tayi sannan tace "Abdul din girma ya k'ara sosai ne mujaheed? Kallon Ammi mujaheed yayi sannan yace wllh Ammi bakiga yanda ya zama babban mutum ba, saura kad'an ya kamo Momys boy, ya fad'a yana kallon Maheer yana k'unshe dariyarsa,

Wani d'an iskan kallo Maheer ya jefa masa sannan yace "heey dude wllh ka iya bakinka, wa kake kirada Momys boy d'in? Batareda Mujaheed d'in ya kalleshi ba yace "duk wanda ya tsargu to dashi nake, wata uwar harara Ammi ta wurgawa Mujaheed tace "ai gara Maheer akan irin iskancin daka dinga tatawa kana k'arami, dariya shahida ta fito tanayi, sabida duk taji abinda

Ammi ta fad'a akan mujaheed d'in, a jikin Ammi ta jingina sannan tace" oh gaskiya na godewa Allah daya tonawa wani asirin k'uruciyarsa har kunnuwana sukaji.  Ta fad'a tana k'ara k'yalkyalewa da dariya.  Mik'ewa mujaheed yayi tareda binta da wani irin gudu da niyar ya kamata, ihu ta dingayi tana zagaya perlourn tareda kiran sunan Ammi.

Da sauri Maheer ya mik'e yabar perlourn, lokaci guda kuma wani b'angare na zuciyarsa ya cika da kewar mahaifiyasu, wadd baze tab'a mantawa da itaba a rayuwarsa, nanda nan abubuwan da suka faru a rayuwarsa ta baya suka dinga dawo masa tsaf a k'wak'walwarsa tamkar a lokacin abin yake faruwa, wasu irin zafafan hawayene suka dinga bin fiskarsa tamkar wani k'aramin yaro, a haka ya fito daga gidansu mujaheed d'in ko sallama baiyiwa kowa ba illa motarsa kawai daya bude ya fad'a ciki tareda murza mata keyy yabar k'ofar gidan,  tabbas a rayuwarsa daza'ace ya fad'i wanda yafi tsana a duniya da rayuwarsa gabad'aya wllh zece Hajiya murja, a yanda yakejin zuciyarsa a yanzu wllh daze ganta seya kasheta har lahira sabida tsanar dayayi mata,

Kallo d'aya zakayiwa Maheer a wannan lokacin ka fahimci tsantsar wutar fansar dake ci a cikin idanunsa,  gabad'aya idanunsa sun rufe, babu abinda yake gani a idanunsa se abubuwan da suka faru shekaru Ashirin da suka wuce,  wata irin k'arace ta gauraye a kan tintin da Maheer yaketa sharara uban gudu, tun kafin yayi wani yunk'uri tsaida motar tini aikin gama ya gama, ji kake gammmmm motocin sun had'u da juna.........

Tun daga wannan lokacin Maheer be sake jin komai ba se iface ifacen mutane sama-sama, daganan kuma idanunsa suka rufe rub yadena jin komai......!

_Comment_
Nd
_Share_

_*🎀KIYARDA DANI...!🎀*_
🎀🐾🎀

*♝ IDTɵ||IƓɵDT WrIТɵr'ی ASSɷ📚✍️*

*💫DEDICATED: to Sis naja'art*

_*WRITING BY: Zm (CHuBaDo)*_

*✨Special Gift for Hafsat Hafnan (my jika),.*

___________📖 iya muni kam wannan hatsarin yayi shi, cikin mintuna kad'an sega ambulance ta hallara a gurin tareda motocin 'yan sanda, abinka da birnin tarayya,  kallo d'aya zakayiwa motocin da sukai hatsarin ka d'auke idanunka sabida yanda gaban motocin ya kwankwatse tamkar an saka gudumar k'arfe an dandak'a su,  banda salatin mutane babu abinda kakeji, nanda nan jami'an tsaro suka fara gudanar da aikinsu tareda malaman Asibitin, da k'yar da sid'in goshi suka iya b'anb'are murfin mitar da khabeer yake ciki suka fito dashi, kasancewar akwai motar tanada isashshen matakan tsaro na Baloons ne yasa khabeer d'in beji wani ciwo sosai ba, cikeda tsantsar tashin hankali gamida d'auriya  Khabeer ya mik'e da k'yar, dukda cewar shima ya bugu sosai a kansa da kuma k'afarsa hakan be hanashi k'arasawa jikin motar maheer ba, sabida tsabar yanda ya tsorata da ganin yanda murfin motar ya wani lauye tamkar an lank'wasashida gudumar k'arfe, babu abinda ke fita daga jikin k'asan murfin motar se jini, dan haka hankalin khabeer ya k'ara tashi sosai,

Dak'yar ya iya had'a kalaman bakinsa ya k'wallawa  malaman Asibitin kira,  da wani mugun sauri ya fara k'ok'arin b'alle murfin motar amma kuma ya kusa, hakanne ya jawo hankalin Matakan tsaron da suke gurin, da gaggawa suka qaraso tareda taimaka masa wajen b'alle murfin motar,  seda sukai da gaske sannan suka samu nasarar zaro maheer daga cikin motar, gaban khabeer ne ya buga. Dummmmm!! Sabida ganin yanda k'arfan dake saman sityarin motar ya huda k'ahon zuciyar Maheer d'in, cikeda tashin hankali yayi baya tamkar ze fad'i,  da sauri *Asp Bala muhammad* ya taroshi cikeda zafin Nama,  zaunar dashi yayi akan dandiryar titin donya samu nutsuwa,  sosai khabeer ya firgita da yanayin  Condition d'in Maheer d'in, sabida  duk abinda ya faru laifin Maheer d'in ne, da ace yabi doka ya tsaya ya wuce wllh da duk hakan bata faru ba,  dukda cewar khabeer babban likitan tiyata ne (surgeon) hakan be hanashi shiga tashin hankali ba,  sabida a iya Rayuwarsa gaba d'ayanta be tab'a zama silar zubar jinin dabba ba ballantana kuma mutum me rai!! Mik'ewa yayi da sauri sabida ganin yanda jini yaketa zuba daga k'ahon zuciyar Maheer, tabbas idan aka tsaya b'ata lokaci tofa tabbas ze iya Rasa Rayuwarsa ma gaba d'aya.

Matsawa yayi dak'ar zuwa gurin tareda bada umarnin abashi zaren k'arin ruwa, ada sunso suyi masa gaddama, har seda ya daka musu tsawa sannan suka bashi abinda yake buk'ata,  kallon norse d'in yayi sannan yace "ki bani ma sarrafin yanka, babu musu ta mik'a masa, yana karba ya saita askar ya yanka saitin gurin da k'arfen yake jiki sannan ya zura igiyar k'arin ruwan ta ciki, wannan dalilin ne yasa zubar jinin ta tsaya, da sauri ya mik'e dukda irin juya masan da kansa keyi, nan da nan ya bata Umarnin a kai Maheer *SUSHMAR INTERNATIONAL HOSPITAL ABUJA, wanda yake a Centaral aria* ma'ana inda yake aiki, ada sunso suyi masa gaddama amma kuma suka fasa sabida sun lura khabeer d'in ba k'aramin likita bane, nan da nan kuwa suka sakashi a motar tareda khabeer d'in, suka d'au hanyar sushmer Hospital,  Inda akabar Asp Bala muhammad tareda sergen bashir suna gudanar da bikice a gurin domin gano cikakken adreshin ma jinyacin, ko kad'an basu samu wata alama wadda zata iya nuna musu waye

majinyacin ba, abu d'aya kawai suka gani a cikin motar, Driving license d'in sa wanda sukaga sunansa k'uruk'uri A jiki wato *MAHEER NASEER LAMIDO*, se kuma wayoyinsa da suka samu suma, a haka suka tattara tareda kiran wayar sashin kula da titina ya sanar da su sannan suka d'inguma zuwa Asbitin suma, 10minute ce ta d'aukesu zuwa Asibitin daga inda abin ya Faru, tun kan su iso tuni har an shiga da Maheer tiyata, kasancewar khabeer yace mara lafiyan d'an uwansa ne,  seda ya tabbatar an shiga da shi sannan Khabeer ya yarda Dr. Abdullah ya fara dubashi.

A b'angaren Maheer kuma Dr. Biru Sahastara Budde, shine wanda yake gudanar da tiyatar tasa, ba indiye ne shi, aiki ne ya kawoshi Asbitin nasu Khabeer d'in, kaf Asbitin shine chf of surgieon na Asbitin gabad'aya, indai K'warewa ce tofa Dr. Biru yanada ita, dagashi se Khabeer wanda shine matemakinsa.

Masha Allah an kammala tiyata lfy,  inda aka tura Maheer d'in zuwa d'akina musamman, gado ne maidaidaicin a tsakiyar d'akin, gefensa kuma wata na'ura ce take nuna yanayin fitar Numfashinsa, komai na d'akin a cikin tsari yake sekace a k'asar waje,

Bayan Dr.Abdullah ya gama duba lafyar Khabeer d'in ne Asp Bala muhammad ya samu zarafin tambayar Khabeer d'in meye alak'arsa da Maheer har yace a kawoshi wannan tsadadden Asibitin?  Shiru Khabeer yayi sabida sam bayaso Asp wani abu a gamedashi, tabbas idan yasan basuda wata alak'a da Maheer d'in tofa ya dinga bibiyarsa kenan har seyasa 'yan gidansu sunsan Abinda ke faruwa, to amma idan yayi masa k'aryan ma still shine ze kwana a ciki, bashida wani zab'i dan haka ya sanar da Asp gaskiyar abinda ya faru, shuru Asp yayi sannan ya kalli Khabeer yace " Amma Dr. Ya kamata mu sanar da 'yan jarida sabida su sanar koza'a samu iyayensa su gani wata qilah hankalinsu zefi kwanciya, da sauri Khabeer yace "a'a Asp don Allah! Nidai banaso " yan jarida susan komai, da zarar sun sani tofa nima dolene iyayena suji labarin Hatsarinnan, kuma wllh hankalinsu tashi zeyi wanda nikuma bazanso hakan ba, don haka kabari nizan kula dashi har zuwa Ranar daze farka ya kuma dawo cikin haiyacinsa sannan mu nemi iyayensa da kuma gidansu,  da k'yar Khabeer ya shawo kan Asp ya amince, wayar Maheer d'in Asp ya mik'awa Khabeer tareda lasisinsa na tuk'i,  karb'a yayi tareda qurawa katin idanu,  a nan yaga cikakken sunan majinyaci. *MAHEER NASEER LAMID'O.*

Comment
Nd
Share

ZM chubado😁
_*🎀KIYARDA DANI...!🎀*_
🎀🐾🎀

*♝ IŊƬЄ[[IƓЄŊƬ WɼIƬЄɼ'ى ASSѡ📚✍️*

*💫DEDICATED: to Sis naja'art*

_*WRITING BY: Zm (CHuBaDo)*_

*✨Special Gift for Hafsat Hafnan (my jika),.*

*_A Yau saukarwar takice my tunkuzar quliqulin zuciyata MOMYN FADYL, haka kuma my abokiyar fad'a kokuma ince my abokiyar........😂😂😂😂, don haka wannan shafin nakine kiyi yadda kikaga dama dashi na mallaka miki shi halak malak, sannan abu na Qarshe kuma shine Chubad'o tana sonki fisabilillah❤_*

_Page:20_

___________📖 shiru khabeer yayi tamkar wanda yake son tuna wani abu, a haka ya mik'e dak'yar ya fito farfajiyar Asbitin, Dr. Abdullah ya hanga a prking space yana k'ok'arin shiga motarsa, da sauri khabeer ya nufeshi tareda d'aga masa hannu, yana zuwa gurin murfin motar ya bud'e tareda shigewa cikin motar ya zauna, tunda ya shiga motar Dr. Abdullah ya zuba masa ido yana kallonsa cikeda rashin fahimta manufar Abokin nasa,

tab'e baki khabeer yayi sannan yace " why are you loking at me like that uhmm? Ya k'are maganar tareda gimtse fuska,

Ajiyar zuciya Dr. Abdullah ya sauke sannan yace "bansani ba, me zan kalla a wannan kuburarriyar fuskar taka da kake tuhumata haka?  Murmushi khabeer yayi sannan yace " waya san maka, kaga malam muje ka saukeni a gida nagaji jikina duk ciwo yakemin wllh, all i need now is to reast. Ya fad'a yana wani yatsina fuska kamar wanda akayiwa dole seyayi maganar. Harararsa Dr. Abdullah yayi sannan yace "ok ammadai kasan i'm not your driver ko?  Dan haka seka fad'a cikeda girmamawa tareda lank'wasa hashenka sannan ni kuma na taimaka maka na kaika har gidan iyayenka yaro. Ya fad'a tareda gimtse  dariyar data taso masa,

Shiru Khabeer yayi bece komai ba, shikuma Abdullah beja motar ba, sabida yace " yau kam seyayi maganin Abokin nasa tunda be iya rok'ar abu cikin kwanciyar hankali da sanyi rai ba, sun kusa  30mnt a haka ba tareda ko wanne yaceda d'an uwansa  k'alaba, a k'arshe ma Dr. Abdullah wak'a ya fara rerawa tareda k'ok'arin kunna redion dake manne a jikin motar,  haushi ne ya kama Khabeer dan haka ya shiga gallawa Dr. Abdullah wata uwar harara,

dariya kawai Abdullah yayi batareda ya kalleshi ba, ya cigaba da abinda yakeyi, illa kawai k'udurtawa kansa da yayi cewar muddin Khabeer be rok'eshiba wllh baze kaishi gidan ba. Kamar khabeer yasan abinda Abdullah d'in yake k'udurtawa a zuciyarsa yace "pls don Allah ka kaini gida mana, wllh kaina ciwo yakemin sosai, a matsayinka na likita ya kamata ka fahimci matsalata, i cnt tolerate any iskancin ka pls.

Wata uwar dariya Abdullah ya saki harda tafa hannu sannan yace "ohhhh ashe dai ka iya karya harshe haka zuwa salon rok'o? Wllh nayi zaton kawai iy Rainin hankalin kafi iyawa. Ya k'are maganar yana " yar dariya, wadda ta k'ara hasala khabeer d'in, seda ya gama yi masa iskanci sannan yaja motar sukabar harabar Asbitin, a hanya ma be k'yaleshi ba har suka k'araso kofar gidan, khabeer yana sauka ya kalli Dr. Abdullah tareda gyara tsaiwarsa yace "ohhhhh thank you, but kasan wani abu? Wllh dama drivern taxi ka koma ba likitan ma jinyata ba, sabida na lura babu laifi kasan aikinka na tuka mutane a mota, ya fad'a tareda sakin murmushi sannan ya shige gida yabarshi nan tsaye,

dariya Dr. Abdullah yayi tarda barin k'ofar gidan, a ransa yana jinjina irin iskancin Abokin nasa,

Khabeer yana shiga cikin gidan be samu kowa a perlourn ba, sosai hakan yayi masa dad'i sabida be shirya amsa tarin tambayoyin k'annan nasa ba, musamman Farouq da Usman, muddin suka ganshi da wannan bandejin wllh ya shiga uku da tarin tambayoyin su, a hakan ma dan iyayensu mata basa nan, a hankali ya fara takawa zuwa hanyar da zata sadashi da d'akinsa, tsayawa yayi cak tareda zuba mata manyan Golden Eyes d'insa, sabida har ga Allah beyi tsammanin ganinta a gurin ba,

Washe baki tayi tareda cewa yaya khabeer kag....... Kasa k'arasa maganar tayi sabida Bandejin datayi arba dashi a nannad'e bisa kan khabeer d'in, nanda nan hankalinta yay masifar tashi, da gudu ta nufoshi idanunta a cike taf da k'wallah,

tun kafin ta fara magana hawayen sun wanke mata fuska, kasa magana tayi illa fad'awa datayi jikinsa tareda sakin wani irin kuka, kasa motsin kirki khabeer yayi sabida jin yanda k'anwar tasa take kuka sosai,

Kokad'an beso Umaisa ta ganshi ba dama Rumana ce to dayasan ta yanda zeyi ya fahimtar da ita ta yanda zata gane, amma se gashi wannan danger dince ta ganshi, yanzu koyaya zeyi da itama oho!

hanunsa ya sanya ya zarota daga jikinsa tareda fara k'ok'arin share mata hawayen daketa faman zubo mata babu k'ak'k'autawa.

Hannunta ya kama har suka isa perloursa sannan ya zaunar da ita a kan d'aya daga cikin kujerun parlourn sannan ya kama fuskarta da tafukan hannunsa yace" its ok dear kukan ya isa haka kinji? Kinga fa ba wani babban ciwo naji ba, kawai 'yar k'aramar kujewa ce so ki dena d'aga hankalinki kinji k'anwata?

Kukan ta kuma saki tareda fad'awa jikinsa a karo na biyu sannan tace " ya khabeer wannan ne k'aramin ciwo? Kallifa yanda fuskanka ya kumbura kamar ba kaiba, sannan a hakan kake kiransa da k'aramin ciwo? "wllh nikam zan kira Abba na fad'a masa haliinda kake ciki yanzun

nan basai anjima ba. ta k'are maganar tana kuka sosai,

shiru yayi batareda ya iya cewa da ita k'ala ba, shirun daya ratsa d'akin ne yasa bakajin komai se sautin kukan Umaisan.

Cikin sigar rarrashi da kuma dabara khabeer ya raba jikinsa da nata sannan ya kalleta yace" kinga malama har sonawa zan fad'a miki ki dena rungumata? Bakisan kin girma bane yanzu Umaisa, dafa ba yanzu bane k'anwata,

D'aga  masa kai tayi dukda haka tana kukan bata dena ba, murmushi ya sakar mata wanda ya baiyana ainihin kyawunsa, sannan yace " kinsan me nakeso dake?

D'aga masa kai tayi alamun a'a, fuskarta ya shafa sannan yace" kinaso na baki labarin yanda akai naji ciwon nan?

Da sauri ta d'aga masa kai, shiru yayi yana kallonta sannan yace " zan fad'a miki amma da sharad'in bazaki fad'awa kowa na gidannan ba, da sauri tace " wllh ya khabeer bazan fad'ama kowa na i promise,

Shiru yayi yana kallonta sannan ya kwashe koma ya gaya mata, kuka sosai ta saka masa, seda ya koma mata asalin yaya khabeer dinsa sannan ta shiga hankalinta tayi shiru,

Kallonta ya sakeyi sannan yace "zan dinga kaiki kullum gurin mara lafiyan ki dinga zama dashi batareda kowa na hidannan ya sani ba, sabida banaso hankalin kowa ya tashi,  sonake kidinga kula dashi har mu samu ya warke sannan mu sallameshi shima ya koma cikin familynsa ko?

d'aga kai tayi alamun gamsuwa sannan ya mik'e ya shiga bedroom dinsa ita kuma ta koma room dinta tareda fad'awa saman gadonta ta saki wani sabon  kukan cikeda tausayin yayan nata, dukda cewar Ya khabeer baya sakar mata fuska sosai amma dukda hakan tana sonshi sosai sabida ya nuna mata k'auna tun tana k'arama, shiyasa bata k'aunar dukkan abinda ze tab'a mata yayan nata, bama shi kad'aiba gaba d'aya ahalinta bata son wani abu ya samesu.

*GANO*

Tunda su Ummi suka iso garin aketa nan-nan dasu musamman ma Baba Binta, sosai tayi farin cikin zuwan surukan nata, mutanan gari kuwa  kusan kowa yasan da zuwansu, sabida gida-gida Baba Binta ta dunga aikawa ana kai musu tsarabar da su Ummien suka kawo mata,

Idan dare yayi kuwa kwanukan turowon da ake aiko musu dashi ko  Momyn fadyl bazata iya k'igawaba sabida yawansu😂, kunsan mutanan k'auye a kwai kara,

Seda sukai sati guda sannan suka fara haramar komawa Abuja, sosai Baba ta tada ballin cewar

itama seta bisu sun tafi tare sabida taje ta matsawa Usman da Farouq sesun fito da matan Aure tunda shi ubansu ya saka musu ido sunk'i suyi Aure,  dariya Mamie ta dingayi  nan ummah ta amshe maganar  da cewar wllh Baba ni kaina nagaji da zamansu haka babu Aure, dariya ummie tayi, a ranta tace "lallai idan su Farouq suka ga Baba a gida yau a kwai Drama, a haka driver ya kwashesu suka nufi Birnin taraiya Abuja.

*B'ANGAREN MAHEER* kuwa ba laifi jikinsa da sauki sosai, sedai har yanzu be iya bud'e idanunsa, sosai yake samun kulawa daga manyan likitocin Asbitin, Ranar da Umaisa ta fara shiga d'akin da Maheer yake ta tsorata sosai dataganshi a kwance sanb'al, nan had'uwarta dashi suka dinga dawo mata, dukda haka ba k'aramin tausayinsa taji a ranta ba, dan haka tun tana saka ran farkawarsa harta dena, wasu lokutan  har story books take zuwa dasu daga gida taita karanta masa, har wasu lokutan idan tana karantawar har murmushi takeyi, idan kuma ta gaji dayi sedai ta saka masa kuka wai yak'i tashi,

A haka harta cika sati d'aya tana abu d'aya, amma kuma dukda hakan babu wani canji, dan haka ta ajiye Novel d'in dake hannunta ta zubawa fuskarsa manyan idanunta masu kamada madara, ajiyar zuciya ta sauke sannan tace " kai wai yaushe zaka tashi ne? Nikam gaskiya na fara jin tsoron kar wani abu mummuna ya faru dakai, yaufa satina d'aya kenan ina karanta maka story books kala-kala amma ko sannu baka tab'a bud'e baki kace  ba, ballan tana kuma kacemin ka gode, oya bud'e idanunka ka kalleni, sannan kace min ka gode bisaga hirar danakeyi maka kullum, ta k'are maganar tana lakuce masa hanci,

Kwab'e fuska tayi tareda turo bakinta gaba tace " oh dis guy,  jibi yanda ya rufe idanu kamar baya son ganin fuskata ma.

Duk abinda take fad'a Maheer yana jinta, sedai idanunsa ne bashida ikon iya bud'e su, amma komai takeyi yana sauraronta, zuwa yanzu ma ya gama haddace muryarta  a k'wak'walwarsa, shi kansa a yanzu babu abinda yake fatan ya gani a rayuwarsa wanda ya wuce yarinyar dake karanta masa story books a kowace Rana, don haka yake addu'ar Allah ya bashi ikon iya bud'e idanunsa koya samu yaga wannan yarinyar ma'abociyar zazzak'ar muryar dake d'aukeda amo a cikin ta......
_*🎀KIYARDA DANI...!🎀*_
🎀🐾🎀

*♝ IᗪƬҿɭɭIƓҿᑎƬ ᗯɼIƬҿɼ'ی  ASSѡ📚✍️*

*💫DEDICATED: to Sis naja'art*

_*WRITING BY: Zm (CHuBaDo)*_

*✨Special Gift for Hafsat Hafnan (my jika),.*

*Aradu Banyi Editing ba😅*

_Page:21_

___________📖 haka   har yamma tayi sannan ya khabeer yazo ya d'auketa suka wuce gida, nan wata nurse me suna fatima ta shigo ta gyara masa kwanciya tareda gyara masa zaman robar dake hancinsa, a nitse ta yaye masa bargon dake jikinsa ta canza masa wani, a haka Dr. Viru ya shigo ya sameta, cikeda girmamawa taja da baya tareda gaisheshi, d'aga mata hannu yayi tareda yalwata murmushin kan fuskarsa, injections d'in dake zube cikin wani farantin silver ya d'auka tareda had'awa sannan yayi masa,  drip din dake manne a hannunsa ya zare masa sannan ya juya ya fice,

harsu umaisa suka koma gida su Ummie basu dawoba, da Ruman suka fara cin karo a harabar gidan, yamutsa fuska umaisa tayi sannan ta kaleta tace "Ruman don Allah me kika dafa wlh yunwa nakeji,  wani irin kallo Ruman ta watsa mata sannan tace " bansaniba 'yar renin hankali, kuma wllh ki wuce ki cire wannan Uniform  d'in kije khitchine ki k'arasa sauran aikin dana bari don wllh bazanyi ba sekinyi shi, kwab'e fuska tayi tareda turo baki tace "uhm to malama naji yanzu dai seki bari na fara cin abincin kafin surutun naki ya biyo bay...... "Kut nice ma nake miki surutu Umaisa? Ruman ta katseta cikin d'aure fuska,

Kallonta Umaisa tayi sannan tace " toda dawa nake kuwa inba ke b..... Tunkafin ta k'arasa maganar Ruman tabita da gudu sukayi cikin parlour,  ya Usman ne kwance bisa doguwar kujerar dake perlourn, da gudu Umaisa tayi kansa tana ihu,  da sauri ya mik'e amma dukda hakan seda ta fad'a masa a jiki, wata uwar harara ya watsawa Ruman dake tsaye tanata faman hura hanci, tun kafin yayi magana Ruman tace "ya Usman wllh kayimin tsakani da wannan yarinyar, bakaga irin Rashin kunyar datakeyimin ba dan taga bana lakad'a mata duka!!!

Had'e rai ya Usman yayi sannan ya kali Umaisa ya kalla mata harara yace " dalla malama fito daga bayana tun kafin kisa na kwad'amiki mari marakunya kawai,  kamar munafuka haka ta fito daga bayansa tana sunne kai,  a fusace yace " tell her sorry tun kafin nayi k'wallo dake a nan gurin idiot.

Da sauri tace "uhmm im sorry, tana fad'a tabar perlourn tana tura baki,  se'a lokacin ya Khabeer ya shigo perlourn, yana ganin Usman yay saurin dora lab cord d'insa bisa kansa sabida karyaga flaster din dake kansa,  a tak'aice  yace" Usman har ka dawo kenan?, tun kafin Usman ya bashi Amsa yayi saurin barin perlourn,  yana shiga side d'insa  kayan jikinsa ya rage sannan ya fad'a toilet.

5:30pm dai-dai su Ummie suka iso gida, sosai suka gaji sabida irin tafiyarda drivern yakeyi, tun 6:00am suka taso amma se yanzu suka iso Abuja sabida fad'an da  Baba takeyi akan se driver ya rage gudu indai bawai so yake ya kasheta ba😂,  shiyasa tafiyar tazo musu da haka.

Motarsu na tsayuwa Ruman ta fito da gudu ta rungume Ummah tana dariya, se bayan ta saki Umma sannan ta nufi gurin mamie ma ta ringumeta tana dariyar farin cikin dawowar tasu, a hankali tace "i miss you so much Mamie na.

Dariya mamie tayi sannan tace " i miss you to sweetheart, sosa kai Ruman ta fara sabida ganin irin kallon da Ummie take binta dashi, da sauri ta nufota zatai hugging d'inta, dakatar da ita Ummie tayi sannan tace " karkizo min nan bana buk'ar oyoyon ki, wato seda kika gama yiwa iyayanki sannan zaki nufoni ko???

Tun daga k'ofar parlour Umaisa ta fara ihun murna, da gudu ta taho ta fad'a jikin Ummie tana ihun murnar dawowar tasu, murmushi Ummie tayi tareda shafa fuskar Umaisan, kallon Ruman Ummie tayi sannan tace "nima ga d'iyata nan ta fitar dani kunya, a haka Baba ta fito dak'ar k'afafunta duk sun kumbura sabida zama, seda ta k'are musu kallo sannan ta tab'e baki tace "ohni Binta yanzu yarannan duk sunyi girman haka amma Mamuda ya zuba musu ido suke zaune haka babu Aure?

Da sauri  Ruman da  Umaisa suka nufeta suka Ringumeta suna dariya,  Umaisa ce ta kalleta tace " kai Granny kinga yanda kikai fresh kuwa? Wllh kamar wata 'yar budurwa haka kika zama, dingure mata kai Granny tayi sannan tace "ja'irah.

A haka suka d'inguma xuwa cikin gidan zuciyarsu fess, a perlour suka samu Usman kwance bisa kujerar da umaisa ta barshi d'azu, yana ganinsu ya mik'e zaune yana murmushi, harararsa Mamah tayi sannan tace " sannu malalacin mataimakin manaja, dubi yanda ka zube mana a parlour sekace wanda ya shekara yana aikin noma, dariya kawai Usman yayi sannan   ya kalli iyayen nasa yace "uhmm nikam bantab'a jin inda akeyiwa d'a gori ba se'a gidan Alhaji Mahmoud muhammad, ya Qare maganar yana " yar dariya cikeda shakiyanci, duka ummie takai masa tana dariya, Baba kuwa banda tab'e baki babu abinda takeyi sabida d'inbin gajiyar dake tareda ita,

Baki Usman ya saki yana kallon Baba sabida mamaki, a k'ufule ya kalli Ummie yace "haba Ummie don Allah, meyasa zaku kwaso mana wannan gaiyar ciwon kan kutaho mana da ita? Ni dana san da ita zaku taho wllh da senayi muku addu'a kunyi tayin faci a han......, "kaci gidanku dan me garin ku, Ummie ta katseshi tareda kai masa dundu a baya, ihu ya saka tareda saurin mik'ewa yana hararar Baba, nunashi Baba tayi sanan tace "Uwarka da ubanka Mamuda kake harara bani ba, d'an banza me kamada sadakar yallah, dariya su rumana suka saki sannan suka had'a baki sukace "amma dai dukda hakan yafiki kyau, carbin hannunta ta jefa musu tanata faman fad'a kamar ta ari baki.

Dak'yar su Mamie suka lallab'ata ta dena fad'an sannan suka kai mata kayanta d'akinta, sannan suma suka wuce nasu d'akunan dan suyi wanka, a haka har aka fara kiraye-kirayen sallah magrib, seda suka gabatar da sallar kafin suka fito daining don suyi Dinner, wanda gabad'aya girkin Ruman ce tayi shi,  a nan ma seda aka sha fama da Baba, dan cewa tayi wllh bazata hau Daining ba sedai a sakko mata da abincin k'asa taci abinta sabida bazata iya wannan rayuwar

ta yahudanci ba😂

Se wajen 10pm sannan Abbah da Farouq suka dawo gida, kasancewar yau d'in tare suka fita da Farouq ya kaishi wajen wani meeting da suka gabatar tareda Minister of Finance, se bayan ya dawo ya huta kasancewar a d'akin Mamie yake nan take sanar dashi zuwan Baba, sosai yayi farinciki da hakan, don haka yana fitowa daga wanka ya shirya cikin wata milk din jallabiya ya nufi masaukin mahaifiyar tasa.

*KADUNA STATE*
AL'amarin Abdul kuwa tun bayan dawowarsu daga Asbiti da Dady nan ya koma d'aki ya dinga tintsirar dariya harda rik'e ciki, seda yay me isarsa sannan ya fad'a toilet ya fesa wanka, be jimaba ya fito a gaggauce ya shirya cikin wata  brown jallabiya k'irar companyn Emraty, sosai tayi masa kyau ba kad'an ba, sabida yanda ta baiyana cikar zatinsa sekace bad'an shekara 22 ba,

Maine perlourn gidan ya nufa, a nan ya samu Dady yana korawa Hajiya murja bayanan likitan, yamutsa fuska kawai yakeyi tareda wani dafe ciki sekace majinya cin gaske,  kamar zeyi kuka ya kalli Dady yace "pls Dady ka sanar dani abinda Dr. Yace akan abinda yake damuna pls Dady...!      Hannu Dady ya mik'a masa alamar yazo gareshi, da sauri Abdul ya fad'a jikin Dady yana matsar k'wallar k'arya, time to time yakan saci kallon fuskar Hajiya murja ba tareda Dady ya lura da hakan ba ya galla mata wata uwar harara,

Dan dole ta mik'e tabar perlourn sabida bazata jure irin wannan muzancin da wannan d'an iskan yaron yake mata ba.

_*🎀KIYARDA DANI...!🎀*_
🎀🐾🎀

*♝ IDTɘ|||GɘDT WrITɘr'ی ASSɷ📚✍️*

*💫DEDICATED: to Sis naja'art*

_*WRITING BY: Zm (CHuBaDo)*_

*✨Special Gift for Hafsat Hafnan (my jika),.*

*_Not Edited, kuyi haquri da typing Erorr don Allah_*

*_A yau shafin na D'iyar d'akin chubad'o ne wato MAMAN KHAUSAR (Hauly) har kullum

chubad'o tana alfahari da irin Qaunar da kike nuna mata, haka kuma ni zainab ina sonki fisabilillah ❤_*

_Page:22_

___________📖 tun daga ranar Abdul ya shimfid'a tabarmar rashin mutunci a cikin gidan, duk abinda yaga dama shi yakeyi, don haka ya hanasu Binta 'yar kwabo saqat da bala'insa, a haka harya samu nasarar dasa tsoransa a xuciyar matan da suke tarawa a cikin gidan suka dena zuwa ma gaba d'aya.

*ABUJA*
tunda Baba taxo basu had'u da khabeer ba, ko sannu da zuwa beje yayiwa su Ummie ba har suka cika kwana uku da dawowa amma basuga k'eyar Khabeer ba, har break fast ma baya fitowa ballantana kuma  Deener, tun Abin baya damun Ummien sa harya  ya fara damunta, dan haka ta d'aga waya ta fara k'ok'arin kiran layinsa, bugu d'aya khabeer wanda ke zaune a office d'insa ya d'auka, tun kafin yayi magana Ummie ta katseshi cikin b'acin rai  tace " khabeer lallai idan ka dawo gida ka sameni a d'aki ina son magana dakai kaji na gaya maka!

Tun kafin ya samu zarafin magana Ummie ta katse wayar, wata sassanyar ajiyar zuciya ya sauke, tareda shafa gefan kansa inda ciwon yake, agogon fatar dake manne a hannunsa ya kalla, dan haka da sauri ya mik'e tareda d'aukar car key d'in motar Usman daya fito da ita,  a gaggauce ya shiga office d'in Dr. Abdullah dan ya kwance masa bandejin dake goshin nasa, nan Dr. Ya dinga takalarsa da surutu amma khabeer din ya shareshi,  ko kafin ya kwance masan ma seda yayta tsokanar sa sannan ya kwance masa,  shidai khabeer bece masa komaiba ya fice yabarshi yana 'yar dariya.

Yana fita Direct school d'insu Umaisa ya wuce, cikin mintunan da bazasu gaza 15 ba ya isa Makarantar, a nitse yayi parking motar sannan ya fito,  se'a lokacin na k'are masa kallo, sanye yake da wata farar riga me ratsin sea'green a jiki, hakanne yasa ya dora sea'green d'in suite a kan rigar, wadda ta dace da blue black d'in jeans d'in dake jikinsa, inda k'afarsa kuna take sanye cikin wani dakakken takalmi k'irar companyn Batozy, a nitse yake takawa zuwa office d'in principal d'in Makarantar cikin takunsa me d'auke da k'asaita da kuma tak'ama a cikin sa, yana shiga    suka gaisa da matar gaisuwar mutunci, bayan sun gaisa ne ya sanar da ita cewar shi yayan Umaisa Mahmoud muhammad ne, kuma yazo d'aukarta ne bisa wani mahimmin uziri daya taso, sosai ta nuna masa jin dad'inta, sabida tasan Umaisa sosai yarinyace me k'ok'ari sosai, sedai a kwai shagwab'a,

nan da nan ta tura aka kira Umaisan batareda wani b'ata lokaci ba,  godiya yayi mata sannan suka tafi,

Tun'a mota Umaisa take tambayarsa jikin Maralafiyan, shiru yayi mata hakanne ya bata tabbacin bazata samu amsar datake nema ba, tuk'insa kawai yakeyi cikeda k'warewa, cikin mintuna kad'an suka isa Asbitin, bud'e motar yayi ya fita, da sauri itama ta bud'e motar tabi bayansa, tsayawa yayi cak yana binta da kallo se faman kokawa take da Baread d'in dake kanta, wata uwar hararar yajefa mata, tun kafin yayi magana ta juya da sauri ta koma mota ta d'akko d'an k'aramin hijabin uniform d'in, wanda ko k'irjinta be gama rufewa ba, a haka tabi bayansa zuwa office d'insa, a tsaye ta sameshi yana k'ok'arin saka lab cord d'insa da alama duba marasa lafyansa zeje, wata farar ledah ya nuna mata wadda ke d'auke da manyan Robar Fresh Milk guda 2 a ciki da kuma cups suma guda biyu a ciki yace " ki d'auka kije dashi, ki tabbatar kin bashi yasha sosai sabida naga kwana 3 da suka wuce baya wan iya shan komai, saura kuma kice sekin k'oshi sannan zaki bashi yasha. Ya qare maganar yana dingure mata kai.

D'aga masa kai kawai tayi tana tura baki sannan taja ledar ta fice, wayarsa ya d'auka ya jefa a aljihun wandonsa sannan shima ya fice dga office d'in a ransa yana mamakinta.

A hankali ta tura k'ofar d'akin tareda sallama, wata sassanyar ajiyar zuciya Maheer ya sauke sabida jin sautin muryar wadda zuciyarsa ta cikada cewar besan ya kamanninta suke ba a idanunsa ba, amma hakan be hanashi yin farin ciki da zuwan ta ba, tabbaswani b'angare na zuciyarsa na shiga damuwa idan kunnuwansa d kuma jijiyoyin jikinsa basuji sautin muryarta ba, so tari wasu lokutan yakan samu kansa da tsananin kewarta musamman ma a kwanaki ukun dabeji d'uriyarta ba!!

a hankali take takowa har zuwa gaban gad'on da Maheer din ke kwance, murmushi ta saki sabida ganin bakinsa na motsawa, a hankali ta kalleshi tace "lallai sauk'i ya fara samuwa tunda gashi har maralafiyana ya fara k'ok'arin motsa bakinsa kamar kowa, yanzu dai bari na fara baka abincin ka kaci sabida D.r yace kwana biyu baka son cin abinci, yau dai sena tabbatar da ka k'oshi sannan zan k'yaleka, nan da 1:30pm senaje masallaci nayi salla, idan na dawo sena karanta maka New Novel d'in danazo maka dashi me dad'i.

Wani cute Murmushi ya sakar mata wanda ya k'ara fito da tsantsar kyawunsa da kuma ramar dake fuskarsa, dukda cewar har yanzu baya iya Magana sabida yanayin aikin da akayi masa hakan be hanashi motsa bakinsa ba,

Dariya tayi me sauti tareda tafa hannunta tace " kai Ashe dama wannan fuskar taka tanayin kyau da murmushi? Kasan mene? "Wllh kafi kyau idan kana murmushi, seka zama kamar ba kai ba. Ta k'are maganar tana dariya, idan ka ganta a yanayin datake maganar seka rantse kan cewar ta samu matsalar k'wak'walwa ne yasa take hakan.

Gadon ta d'ago ta yanda zataji dad'in bashi Fresh Milk din, wani farin towel ta shimfida masa a qasan wuyan sa, sabida karta b'ata masa jiki, a nitse ta fara zubawa a cikin cup d'in sannan ta fara bashi, a hankali yake seeping Fresh Milk d'in kamar anyi masa dole haryata samu ya shanye dika, goge masa baki tayi da tishu, sannan tace " to bari na tafi masallaci sabida kar time ya wuce, fita tayi ta barshi a zaune sabida abinda yasha yayi dagesting a cikinsa kmar

yanda ya kamata,

Bayan fitarta babu jimawa Dr. Viru ya shigo shida team d'insa suka tura gadon Maheer zuwa Tiater Room, nan da nan suka shiga duba Ifyar idanun nasa, basu sha wahalaba cikin ikon Allah kuwa suka gano bakin zaran matsalar, harma da abinda yake hanashi maganar seda suka ganoshi,  wani daskararren jini ne ya tare masa a mahad'ar bututun fitar sautinsa, dan hka suka tura masa wata na'ura ta bakinsa cikin mintuna kad'an suka samu nasarar kwarfe jinin batareda sunyi masa wata allura ba,  sosai yake fargabar bude idanun nasa sabida yawan hasken dake d'akin, don haka Dr. Viru ya bada umarnin a maidashi d'akin da aka d'akko shi kasancewar babu haske sosai a d'akin ze bashi damar bud'e idanunsa batareda wata matsala ba,

Seda ta idar da sallar sannan ta koma d'akin, da sallama ta tura k'ofar ta kunna kai cikin d'akin, ledar Fresh Milk d'in data ajiye a gefan gadon ta d'akko sannan ta koma kan wata lallausar kujerar dake d'akin ta zauna, a hankali ta fara sha tana wani lumshe ido sabida yanda Fresh Milk d'in yake mata dad'i.

A hankali ya fara bud'e idanunsa harya gama bud'e su Ras akan silin d'in d'akin, a nitse ya fara bin d'akin da kallo tamkar wanda yake neman wani abun harya maida kallonsa kan  kujerar datake zaune a kai,  tundaga kan cute zarazaran neils d'inta na k'arfa ya fara kallonta har zuwa kan fuskarta wadda kofin hannunta ya hanashi ganin fuskarta, sedata shanye tass sannan ta sauke cup d'in tana lasar baki, karaf idanunsa suka sark'e cikin na juna, nanda nan k'irjin Maheer ya buga da k'arfi sabida tsabar kad'uwar dayayi, da k'yar ya iya tattaro kalaman bakinsa yace " Qu..ee..n of tears??!!!  wani irin kallo yake jifanta dashi wanda  har seda taji k'irjinta ya amsa itama...!   Sabida irin kallon da yake binta dashi yana d'aukene da wasu manyan sirrika masu wuyar fassarawa ga zuciyar data kasance bak'uwa a cikin al'amari na shak'uwa da kuma mayen soyayya me matik'ar zafi da tasiri.....
_*🎀KIYARDA DANI...!🎀*_
🎀🐾🎀

*♝IᗪTᘿlllGᘿᗪT WrITᘿr'ی ASSໂ📚✍️*

*💫DEDICATED: to Sis naja'art*

_*WRITING BY: Zm (CHuBaDo)*_

*✨Special Gift for Hafsat Hafnan (my jika),.*

*_BANYI EDITING BA🙅_*

_Page:23_

___________📖 sosai k'irjinsa yake bugawa haka itama a b'angaren ta, a hankali ta mik'e cikeda k'arfin gwiwa gamida farin cikin bud'ewar idanun nasa duk a lokaci guda, sedai yanayin irin kallon dayake binta dashi ne yasa duk taji babu dad'i amma kuma seta dake harta samu nasarar k'arasawa jikin gadon, murmushinta me kyau ta sakar masa, don haka ya kauda kansa da sauri zuwa wani gefen daban, dafari ya zata gizo take masa kamar yanda ta saba tun daga ranar daya fara d'ora idanunsa a kanta, dan haka zuciyarsa ta cika da Rud'ani me girman gaske, wanda ya kasa warwarewa kansa balle ya fahimci tayanda ze siffanta shi, addu'a kawai yakeyi Allah yasa ba wannan yarinyar bace yarinyar danake bege da marmarin kasancewa a tareda ita ba!! Nanda nan wani b'angare na zuciyarsa yace dashi "to idan itace yarinyar da zuciyarka da kunnuwanka sukai sabo da ita shin dawani idanun zaka kalleta Maheer? Duba da irin hallaccin da tayi maka a Rayuwarka?

Dafe kansa yayi da sauri sabida wani irin sara masa da yayi, da sauri ta dafa kafad'arsa tace " Eyyah sorry kabi a hankali kada ka fama ciwon dake jikinka dik da cewar saura kad'an ma a sallameka zuwa gida.

D'aure fiska yayi tamau tareda bin hannunta wanda ta d'ora bisa kafad'unsa, da sauri ta janye hannunta daga jikinsa, sabida mugun kallon dayake binta dashi, matsawa tayi daga jikin gadon jikin ta a matik'ar sanyaye, a hankali ta koma kan kujerar data tashi ta zauna, juyarda kansa yayi gefe guda ba tareda ya sake kallon inda take ba, itama bata kaleshi ba illa kawai abinda take sak'awa a ranta gameda halaiyar sa, gaba d'ayansa idan yayi wani abin sekace me Aljanu, muryarsa ta tsinkaya cikin Husky voice d'insa yace "keeee wai meyasa kiketa bibiyar Rayuwata ne haka? Tunda na had'u dake kijeta kawo min tsoko a cikin Rayuwata, ko ina naje sekin bini sekace wata aljanah, ok koda yake be kamata nayi mamaki ba sabida dama ku mata haka kuke, gabad'ayanku 'yanbin zak'i ne, haka kuma muddin kuka k'yalla idon ku akan mutum to kun dinga bibiyarsa kenan harse kunga bayansa sannan zaku barshi, har sonawa kike so na fad'a miki cewar kifita a Rayuwata ne iyeee?

Tunda ya fara magana take kallonsa tamkar wadda aka dasa sabida mamakin irin maganganun da suke fitowa daga bakinsa, banda hawaye babu abinda ke zuba daga fararan idanunta, babu abunda takeji a zuciyarta face wani irin tuk'uk'in bak'in ciki akan kalaman sa, da k'yar ta iya bud'e bakinta wanda yayi mata nauyi sannan ta tace" hak'ik'a duniya a cike take da mutane kala-kala, haka kuma komai na duniya yanada sakamakonsa, bazanyi mamaki ba danka jefeni da kalaman da duk suka fito daga bakin ka ba, sabida kai d'in namiji ne, dama ba duk maza bane suka san alkhairi ballentana harsu mayarda martaninsa, nagode da sakamakon dana samu daga gareka, sedai inaso ka sani ko wacce mace tanada halaiyarta hakama d'abi'unta. Tana kaiwa nan ta juya da gudu tabar d'akin tana wani irin kuka me cin Rai,

Tunda take a Rayuwata bata tab'a jin bakin ciki irin na yau ba don haka ta koma masallaci ta had'a kai da gwiwa ta dinga rusar kuka kamar wadda aka aiko mata da mutuwar wani nata.

Tunda ta fita daga d'akin ya kasa d'auke idanunsa daga kan k'ofar, lokaci guda yaji wata irin Nadama gamida haushin kansa sunyi masa dirar mikiya a zuciyarsa, shin meyasa ya fad'a mata

maganar datayi sanadiyar zubar hawayen ta? Kansa ya dafe sabida yanda k'irjinsa yayi masa nauyi, idanunsa ya mayar ya lumshe yana me dana sanin abinda yayi mata,

Seda tayi kuka me isarta sannan ta nufi office din ya Khabeer, a hankali ta k'ofar tareda yin sallama, kallo d'aya yayi mata ya fahimci tayi kuka, sabida yanda idanunta suka kumbura fuskarta kuma tayi ja, abinka da farar mace, mik'ewa yayi da sauyi lokaci guda kuma ya rikice yana tambayarta abinda ya sameta!

Wani sabon kukan ta sake fashemai dashi, tareda k'ok'arin fad'a masa a jiki, dakatar da ita yayi ta hanyar zaunar da ita akan d'aya daga cikin kujerun dake perlourn, seda yayi mata da gaske sannan ta nutsu ta dena kukan datakeyi, sannan ya fara tambayarta dalilin kukan, bata da wani zab'i don haka ta shirga masa k'aryar cikinta ne yake mata ciwo, kallonta kawai yakeyi sannan yace" tashi muje kisha magani sena maidake gida, ba musu ta mik'e kamar jira take ya ambata mata kalmar tafiya gidan,

Da ido kawai ya bita a ransa yana mamakin hali irin na k'anwar tasa, sam bata raina abin kuka sekace wta k'aramar yarinya, seda ya biya ta pharmacy din cikin asbitin ya siya mata magani sannan suka nufi hanyar gida, har suka k'arasa gida fuskarta bata koma normal ba, a hankali ta bud'e murfin motar ta fita, a babban perlourn gidn ta samu Baba tana kallon wani indian film na fad'a, ita kad'ai se faman magana take ita kad'ai tana fadin "bazaka rama ba kana kallosa ze kasheka?

Rumana dage tsaye a k'ofar khitchine ta rik'e k'ugu tana kallon Baba banda dariya babu abinda takeyi, a haka umaisa ta wuceta ko sannu batace mata ba, tab'e baki Baba tayi sannan tace " shegiya me kamada Bararo😂

Ita dai Ruman batace komaiba ta koma khitchine taci gaba da taya mamie had'a abinci.

Ahka Khabeer ya shigo perlourn da sallamah, kallon tsaf Baba tayi masa sannan ta kyauda kai, da sakin fuska ya nufi kusada ita ya zauna a k'asan kafent din dake shimfed'e a perlourn, hanunta ya kamo yace " ohhh my sweetheart yaushe kika zo ne babu ko labari? Aida na sani wllh dana kawo muki cefane na musamman, ya K'are maganar yana fad'ad'a murmushinsa, bige masa hannu tayi tareda fadin dalla sakarmin hannu, aini wllh babu abinda zakuce min kaida Faruku, in banda bakuda mutunci ace harna kwan uku a garinan bakuzo kun gaidani ba sabida baku d'aukeni a bakin komai ba, to wllh bari Mamudan ya dawo senaji idan shiyace karku dinga mutunta ni.

Tab'e baki yayi yana kallonta, seda yaga tana shirin jik'a masa aiki sannan ya fara lallab'ata yana bata baki, seda yaga ta ware sannan ya haura zuwa d'akin Ummie, nan ma kaca-kaca Ummie tayi masa sannan ta k'yaleshi, har d'aki yaje ya gaida Mamah sannan ya kicin ya gaida mamie itama, sannan ya samu zarafin tafiya side d'insa danya watsa ruwa ka kwanta kuma ya huta.

B'angaren Umaisa kuwa wani sabon kukan ta sake fashewa dashi a saman madaidaicin gadonta, nan zuciyarta ta fara aiyana mata maganganun Maheer, shin metayiwa bawan Allahn nan ne a Rayuwarta haka dayasa ya tsaneta? Shin meye laifinta donta temakeshi a Rayuwa? Dama wannan shine sakamakon alkhairin daya kamata ya saka mata dashi kenan?

Wani sabon kukan ta cigaba dayi har wani nannauyan bacci ya samu nasarar daukar ta.

*KADUNA, UNGUWAR BADIKKO.*
Binta 'yar kwabo ce zaune bisa wani k'ayataccen perlour wanda ya kasance mallakin Hajiya sa'a, kallon Hajiya sa'ar tayi sannan tace "hmmm ni wllh yanzuma kin fara bani haushi, in banda jaraba irin taki meyasa bazaki iya hak'ura da Abdul ba, wllh ni'a ganina indai ba aiki akai miki akan yaronnan ba wllh ko kallon arzik'i baki isa yayi miki ba, idan ma tak'amarki kud'in da kike dashine kema kinsan ubansa ba k'aramin mutum bane, dan haka kwai ki fito da kud'i malama ayi miki aiki akansa seyanda kikaga dama zakiyi dashi a tafin hannunki,

Murmushin jin dad'i Hajiya sa'a ta saki, sannan tace " wllh Binta indai shawarar mugunta ake nema to da anzo gurinki an gama, tafawa sukayi tareda shek'ewa da dariya irin ta cikakkun 'yan bariki, har yamma suna yare suna hirar ta yanda zasu b'illowa lamarin Abdul d'in, daga k'arshe suka mik'e Rungume da juna sukai nufi Bedroom d'in Hajiya sa'ar. Niko ina ganin sun shige d'akin zan bisu, da sauri Momyn Fadyl ta dank'o bayan rigata, tareda fisge biron daga hannuna 😂

B'angaren Dadyn su Abdul kuwa, sosai yke rashin lafya a tsatsaye, wasu lokutan ma idan abin yayi tsanani har fad'uwa yakeyi sedai a d'agashi, wasu lokutan ma seyafi sati besan inda kansa yake ba, wannan al'amarin shine babban tashin hankalin Abdul a yanzu, dan haka ya fara fafutukar fitar da mahaifin nasa zuwa k'asar Cairo, don haka da sassafe Abdul ya shirya tafiya zuwa Yola batareda sani kowa ba, sabida ya k'udurtawa zuciyarsa cewar seyayi duk me yuwuwa ya daidai ta tsakanin mahaifinsa da kuma 'yan uwansa, wannan shine abinda yake so ya cimmawa a halin yanzu, car keys dinsa ya dauka da kuma wayoyinsa, system dinsa ya bude tareda shiga Email dinsa ya fara k'ok'arin turawa Maheer saqo akan Rashin lafiyar Mahaifin nasu, yana gama rubutawa ya tura masa, sannan ya rufe system din ya fice tareda kulle k'ofar part din gaba d'aya,

Motar ya shiga tareda duba agogon Rolex din dake daure a tsintsiyar hannunsa, zaro manyan idanunsa yayi tareda kunna motar da sauri sabida ganin time din tashin lokacin jirgin nasu ya kusayi, kafin ya fita seda ya tsaya yayi magana da Baba mai gadi, sannan ya kira sulaiman wnda yake kulada harkokin shige da fice na gidan gaba d'aya, kashedi sosai yayi masa kan cewar karyabar kowa ya shiga b'angaren Dady koda kuwa Hajiya Murja ce dakanta, sabida a halin yanzu sam beyarda da ita ba,

Keys din b'angaren Dadyn ya bashi sannan yace masa shima baze dad'e ba ze dawo yau insha Allah, Addu'ar alkhairi suka dinga yi masa tareda fatan samun Abinda akaje nema. Godiya yayi musu sannan ya gigi motar zuwa Air port, yana zuwa ko minti biyar beyi ba jirginsu ya d'aga

zuwa Birnin na yolah,  se'ince Malam Abdul Allah ya bada nasara akan abinda akaje nema.

*ABUJA*
tun daga Ranar Umaisa bata sake zuwa Hospital d'in ba, sabida ta k'udurtawa kanta cewar bazata sake shiga sabgar Maheer ba koda wasa sabida hankaka ne shi besan na gida ba, dan haka ko ya khabeer yaje d'aukarta a schl sedai ta gudu idan aka gajida neman ta ba'a ganta ba sedai ya tafi abinsa, wannan dalilin ne yasa gaba d'aya khabeer din shima be sake bita kanta ba,

B'angaren Maheer kuwa tuni zuciyarsa ta dinga addabarsa ta hanashi sak'at, sabida yanda take a cike taf da kewar yarinyar daya kasa tantance matsayinta a zuciyarsa, sosai yakejin haushin kansa sabida koma meye ya faru dashi shine silar jefa kansa a cikin halin da yake ciki a yanzu,

Bayan sati d'aya aka sallami Maheer sabida yanda yaji sauk'i sosai ya koma normal yanda yake, khabeer ne da kansa ya d'aukeshi ya kaishi har gidan Maheer din dake Unguwar Garki, sosai Maheer din yaji dadin abinda khabeer din yayi masa, harta lawan mai gadi seda ya nuna farin cikin dawowar shugaban nasa, dukda cewar yayi zaton Maheer din gida yaje shiyasa tsawon lokaci be dawo ba se yau din,  Khabeer be wani dade ba ya mik'e yayiwa Maheer sallama, har bakin motarsa ya Rakoshi, a nan ne khabeer yake shaida masa batun motarsa, murmushi Maheer yayi sannan yace "ba damuwa ze kira Asp din da kansa, wayoyinsa khabeer ya bashi sannan yayi masa sallama ya tafi.  Tunda Maheer ya dawo gida ya d'aura da tunanin Queen of tears d'in sa, sosai zuciyarsa keyi masa zafi idan ya tuna sanda take kuka sabida maganar daya fad'a mata, wasu lokutan har tambayar kansa yake shin meyasa ma ya fad'a mata abinda ya zama silar zubar hawayenta?

Tsaki ya sauke tareda jawo wayarsa ya jona ta a chaji, sabida tun fitowarsa daga Hospital be kunna ta ba, system dinsa ya jawo ya ya kunna, haka kawai yaji yana so ya duba Email d'insa, kodan ya turawa Abdul dinsa sak'o.

Yana bud'ewa yayta cin karo da sak'annin mutane kala-kala, ciki kuwa harda na Mujaheed da kuma na Abdul, na Mujaheed ya fara bud'ewa  ya fara dubawa kamar haka:    _" hyyyy Dude, wai meye matsalarka ne inata faman kiran wayarka Amma kullum a kashe, hope kana Ify._

Murmushinsa me kyau yayi sannan ya bashi amsar yana nan Ify, kan sak'on Abdul ya koma tareda bud'ewa ya fara karantawa kamar haka;     *_Assalm my one and only ya Maheer, a duk ida ka kasance k'aninka Yanayi maka fatan Alkhairi tareda farin ciki me dorewa na har abada, sedai ina me bakin cikin sanar dakai cewar Dadyn mu yana fama da jarrabawa ta rashin Ify, wanda a halin yanzu bema san wanda yake kansa, insha Allah nan da kwan Uku zamu fita dashi zuwa Egypt!!!!_*

Wani irin bugawa k'irjin Maheer yayi da k'arfin gaske, mik'ewa yayi da sauri tareda nufar drower dinsa, wani mukullin mota ya d'auko ya fito da sauri, parking space ya nufa inda na hangi wata zabgegiyar Reng Roba baka wuluk, se faman d'aukar idanu takeyi, a hanzarce ya shiga ciki ya

zauna tareda d'aura sit belt a jikinsa, yana kunna motar maganar Dady  ta fara yi masa yawo a cikin kwanyar kansa, musamman ma sanda yake gaya masa cewar "ka fice ka barmin gidana Maheer, wllh na sallamawa duniya kai, haka kuma muddin ka sake waiwayar inda nake wllh senayi maka baki Rayuwarka tafi hka lalacewa!!!!!

Wasu siraran hawaye ne masu zafi suka dinga bin kyakkyawar fuskarsa, a hankali ya shiga firta " innanillahiwa'inna'ilaihirraji'un, wannan wace irin Rayuwace haka?

_*🎀KIYARDA DANI...!🎀*_
🎀🐾🎀

*♝ ɪᗪƬɛℓℓɪɢɛᗪƬ ᗯяɪƬɛя'ی ΑЅЅѡ📚✍️*

*💫DEDICATED: to Sis naja'art*

_*WRITING BY: Zm (CHuBaDo)*_

*✨Special Gift for Hafsat Hafnan (my jika),.*

_Page:24_

___________📖 jikinsa ne yay masifar sanyi daya tuna da kalaman mahaifin nasa akansa, wasu zafafan hawayene suka shiga zubo masa, cikeda sarewa ya mik'a hannunsa ya zare mukullin motar tareda kasheta, sit belt din ya cire daga jikinsa tareda bude murfin motar ya fice gaba d'aya zuwa cikin gida,  direct Re-fregerator din dake perlourn ya nufa, tareda b'alle murfinsa da k'arfin tsiya,  lokaci guda ya janyo kwalbar Brandyn dake ciki, murfin ya b'alle tareda k'ok'arin kafawa a bakinsa,  tsayawa yayi cak, lokacin daya tuna da maganar da masoyinsa Abdul yake gaya masa a lokacin dayakeyi masa tuni akan haramcin shan giya, nan da nan wani b'an gare na zuciyarsa ya fara aiyana masa cewar, "a'a maheer kada ka sake aikata wani babban kuskuren a Rayuwarka, sabida babu wata mafita dazaka samu a tareda abinda Allah yayi haramci akansa, a yanzu babu abinda kake buk'ata face ka gyara alak'arka da ubangijin ka, sabida babu wani mutum wanda ze d'auki sab'on Allah ya zama abin aikatawarsa kuma ya zauna lfy!  Dole ne Rayuwa ta juya masa baya,

Shin baka zaton cewar dalilin shan giyar da kakeyi ne Allah yake jarrabaka ta wannan b'angaren?  A halin yanzu babu abinda kake buk'ata kamar yafiyar ubangi Maheer, tabbas idan ka lazimci istig fari Allah ze duba dukkan lamarinku daga kai har mahaifin naku, dan gwarar da kwalbar yayi, still idanunsa suna zubar da hawaye, mik'ewa yayi da sauri ya koma khitchine ya d'akko wani madaidaicin kwando ya fara zuba kwalaban giyar a ciki, seda ya kwashesu tass sannan ya fita ta k'ofar baya ya watsasu a kwandon shara,  tundaga wannan Ranar Maheer ya lazimci istig fari don ya gyara alak'arsa da Ubangijin sa tareda  addu'ar yiwa Mahaifin sa addu'ar

samun Ify,  sosai Maheer ya fita daga haiyacinsa sabida yawan tunanin da yake matsawa kansa dashi gefe da'aya ga damuwar ciwon Dadyn sa, inda d'aya b'angaren kuma tunanin Umaisa ya hanashi sakat,  wasu lokutan har har unguwarsu yake zuwa amma baya samun ganinta, yauma kamar kullum sanye yake cikin k'ananan kaya wanda sukai matik'ar karb'ar jikinsa, daga d'an nesa da gidansu ya parker motar, jifa-jifa yake ganin masu irin Uniform d'in daya tab'a ganinta dashi suna nufar wani babban masallacin dake unguwar, hakanne ya bashi tabbacin cewar a cikin masallacin islamiyar take, a hankali ya koma cikin motar tareda k'udurtawa kansa cewar yau baze tab'a barin unguwar ba har seya sanyata a idanunsa,

Daga nesa kad'an da masallacin ya tsaya batareda ya fito ba, tun yana sa ran ganinta harya fitar da Rai, dan hka ya juya kan motar ya fara tafiya, kamar ance masa ya juya ya ganta ta tsaya a gurin wani dattijo tana siyan a gwaluma, tsaida motar yayi tareda zuba mata manyan idanunsa yana kallonta,  a nitse ya bud'e murfin motar tareda nufar gurin cikin takunsa na k'asaita,  harya k'arasa gurin bata lura dashi ba, sabida yanda duk tabi ta maida hankalinta akan agwalumar,  ledar agwalumar da mutumin ya mik'a mata ta karba tareda mik'a masa kudin sa, ledar Maheer ya rik'e da sauri, hakanne ya  bata damar d'ago manyan idanunta don ganin waye, ja da baya tayi tareda sakin ledar agwalumar a k'asa, nan da nan idanunta suka ciko da k'walla, juyawa tayi zatabar wajen, dan haka da sauri ya tareta tareda zuba mata tsimammun idanunsa,

Tsayawa tayi chak tana kallonsa lokaci guda hawayen suka samu nasarar zubo mota, da k'yar ta iya bud'e baki tace "meyasa kake bibiyata ne?

"Abinda kayi min kwanakin baya isheka ba shine yanzuma ka sake biyo ni har nan?  Wai meyasa kake bibiyar Rayuwata ne don Allah?  da sauri ya matso kusada ita yace" ni kaina bansan dalilin dayasa nake bibiyarki ba a Rayuwata, illa kawai abinda nakeji a tareda ke wanda har yanzu ni kaina na kasa fahimtar ma'anarsa, wllh tun ranar dana fara ganinki kika kasance a tunanina , ada nayi tunanin cewar abinda kikayimin a had'uwata dake na farko ne yasa bakejin haushinki, sedaga baya na fahimci cewar ina matik'ar Sonki Umaisa, nikaina ban tab'a zaton zan tsinci kaina a soyayyar wata 'ya mace ba, amma se gashi Qaddarah ta Riga fata!!!.

Tunda ya fara magana take kalonsa sabida tsabar firgitar datayi da kalamansa, lokaci guda zuciyarta da jikiyoyin jinin dake gudana a sassan jikinta suka tsaya cak da aiki, sabida tunda take a Rayuwarta namiji betab'a zaiyana mata kalamai masu tasiri irin haka ba, hawayen idanunta ne suka tsananta zubowa sabida bazata iya jure hakan ba, dak'yar ta iya bud'e bakinta wanda yayi mata nauyi tace "wllh duk abinda ka fad'a ba gaskiya bane, sabida duk duniyar nan banida mak'iyin da baya k'aunata sama dakai, har yanzu k'iyayya nake gani a k'wayar idanunka ba soyayyah ba!!  Inda ace kana sona bazaka tab'a zama silar zubar hawayena ba,  don girman Allah na rok'eka ka fita a Rayuwata ka dena bibiyata.!!!    Tana kaiwa nan ta juya da sauri tabar gurin

Kasa motsawa yayi daga gurin tamkar gunkin da aka dasashi a gurin, kallo d'aya zakayi masa ka fahimci tsantsar tashin hankalin dayake ciki sanadin kalamanta,  ganin da yayi cewar wankin

hula ze kaishi ga dare ne yasa ya fad'a motarsa yabar unguwar zuciyarsa nayi masa wani irin zafi.

*_ADAMAWA (YOLA STATE)_*

Cikin ikon Allah Abdul ya sauka Yolah Ify,  yana sauka be b'ata lokaci ba ya nufi Family hause dinsu dake cikin yola,  sosai sukai farin ciki da ganin Abdul d'in  har hakan ya gagara b'oyuwa a fuskokinsu,  seda suka sha hira da matan baffaninsa sannan ya nufi d'akin Baba Ma'u wadda ta kasance yayar mahaifinsa wadda suke kiranta da (DADAJI).

Sosai Dadaji taji dad'in zuwan Abdul, nan ta shiga tambayarsa Maheer, Abdul be boye mata komaiba akan abinda ya faru tsakanin Maheer din da Dady, sosai hankalinta ya tashi akan al'amarin  don haka tace "Amma  Nasiru ya tabka babban kuskure a rayuwarsa daya biyewa son zuciyarsa, dukda cewar idan akai duba da irin labarin daka bani za'a fahimci cewar ba laifin Nasiru bane harda sa hannu a cikin lamarin, don haka karka damu insha Allahu zamu dage wajen gayawa Allah.

Wayarta ta d'akko sannan ta shiga kiran wayar Baffah iyah, yana d'auka ta sanar dashi cewar duk abinda yake faruwa da d'an uwan nasu, sannan tace dashi " ka kira Baffa Umaru shima ka sanar dashi halin da ake ciki a gameda Rashin lafiyar Nasirun.

Kan kace me tuni zancen ya karad'e kunnuwan mazan dake familyn, suna idar da sallar Azarahar aka shiga meeting akan matsalar Dadyn, a nan Baffa gidad'o yake sanar dasu cewar "yaje kaduna kwanaki amma  Dady yasa mai gadi ya hanashi shiga gidan, tun daga lokacin ya fahimci a kwai abinda ke damun d'an uwan nasu, sabida kaf cikinsu Dady yafisu son zumuci.

A nan suka yanke shawarar zasuje su taho dashi nan yola  domin a nema masa Ify, haka kuwa akayi  a Ranar sukayi boking flight da Abdul da kuma Baffa gid'ad'o da Baffa Umaru suka nufi garin na Kaduna.

Cikin ikon Allah da yardarsa suka sauka Ify, nan Abdul ya kwashesu zuwa gidansu dake unguwar Rimi,  cikin mintuna kad'an suka iso k'ofar makeken gidan nasu me cikeda tarin mata'ul Hayat na duniya, horne yayi sannan mai gadi ya wangale musu k'ofa suka kunna kai zuwa ciki, a nitse yayi perking motar sannan suka fito cikin shigarsu ta alfarma, kallo d'aya zakayi musu ka fahimci daga tsatson fulanin asali suka fito,

Direct part din Dady suka nufa, a hankali ya zaro mukullin dake aljihunsa kasancewar yanada wani extra bayan wanda yabawa Sulaiman ya fara k'ok'arin bud'e kofar, tunkafin ya murd'a keyn k'ofar ta bud'e dan hka gabansa yay wata irin fad'uwa!!!!!      A rude ya tura k'ofar ya shiga da sauri, Direct bedroom din Dadyn ya nufa, nan ma k'ofar a bud'e take,  a tsorace ya maida kallonsa kan makeken gadon dake d'akin,  babu kowa akai sema yamutsa gadon da akayi, wanda ya bashi tabbacin cewar seda akayi kokawa da Dady kafin a d'aukeshi, zubewa yayi a k'asan kafet din dake shimfid'e a tsakiyar d'akin, a nan yaga drip din da aka sakawa Dadyn kafin

ya tafi yolah an jefar dashi a Qasa da alama ma fisge masa shi a kai da k'arfin tsiya duba da rin jinin dake jikin allurar da kuma kafet d'in, wata Razananniyar k'ara ya saki tareda kiran suna Allah..! Se'a lokacin su Baffa Gid'ad'o suka iso cikin  d'aki.

_*🎀KIYARDA DANI...!🎀*_
🎀🐾🎀

*♟ IŊTɇlllƓɇŊT WɍITɇr'ی  ASSѻ📚✍*

*💫DEDICATED: to Sis naja'art*

_*WRITING BY: Zm (CHuBaDo)*_

*✨Special Gift for Hafsat Hafnan (my jika),.*

*_This page is 4 you my sweetheart Shahidah Isah Abdu🥰, Qanwata ta kainah, Allah yayiwa rayuwarki albarka_*

_Page:25_

____________📖 cikeda tashin hankali Abdul yake nuna musu gadon yana fad'in "shikenan suna tafi da Dadyn mu baffah gid'ad'o!  Gaba d'ayansu kallo d'aya zakayi musu ka fahimci irin zallar tashin hankalin da suke ciki, babu abinda suke fad'a se innanillahi'wa'inna'ilaihirraji'un!!!

Baffa ummaru  ne yayi k'arfin halin cewa " gaskiya be kamata muzana muna  b'ata lokaci ba, ya kamata mu sanar da jami'an tsaro halinda ake ciki sabida a tari abin da wuri.

Wata zabgegiyar Toyoya benza bak'a wuluk na hanga bisa babban titin garin na kaduna, gaba d'aya ilahirin glasan motar a lullub'e suke da tintake, gudu kawai suke zubawa na fitar hankali har suka samu nasarar d'auke  hanyar birnin taraiya, seda sukai tafiya me nisan gaske sannan suka yi perking a wani k'aramin k'auye wanda yake dab da garin TAFA, cikin mintunan da bazasu gaza 15 ba sega hajiya murjah ta fito daga cikin wata hatsabibiyar 4matic C350, wadda ta kasance fara tass da ita, sanye take cikin wani dakakken leshi milk colour, se wani uban glass data kafa a fuskarta wanda ya cinye ilahirin rabin fuskarta sabida girmansa, a hankali take takawa cikin takun isa da kuma tak'ama, inda aminiyarta Binta 'yar kwabo ke take mata baya.

A gaggauce Mutanan dake cikin bak'ar motar suka firfito gaba d'ayansu sanye da wasu manyan riguna bak'ak'e wa'yanda suka k'arawa jikinsu cika da kuma girma, fuskarsu a lullub'e suke ciki bak'ak'en  macks, baka ganin komai face idanunsu wanda ya kasance abin tsoro ga

duk wanda ya kallesu,  suna isowa inda take suka sanarda ita sun gama aikin data basu.

Wata uwar dariya Murja ta saki sannan ta basu umarni da su saka matashi a cikin motar ta, haka kuwa akayi, nanda nan suka kinkimi Dady wanda ya sume tun bayan satonshin da sukayi suka jefa matashi a mota, seda tayi musu gargad'i sosai kan cewar karsu yarda su koma Kaduna, sabida tanada tabbacin cewar muddin suka koma tofa jami'an tsaro zasuyi ram dasu, murmushi Ogansu yayi sannan yace "kinga Hajiya kawai ki sallamemu da kud'ad'en da mukai alk'awari dake, ba wai ki tsaya kina b'ata mana lokaci ba.

Dariya tayi sannan ta tura Binta 'yar kwabo ta d'akko mata wata jaka wadda ke shak'e da kud'i ta mik'a musu, suna karb'a suka fad'a cikin motarsu sannan suka figeta da wani mahaukacin gudu,  nan suma su Murja suka fad'a tasu motar suka d'auki hanyar birnin taraiya Abuja,  cikeda kwanciyar hankali gamida nutsuwar zuciya Hajiya Murja take tuk'a motar, inda wani  b'angare na zuciyarta yake a cike taf da farin ciki,  wayarta tasa Binta ta d'akko sannan tace " maza ki kira min lambar Abdul.  Zaro ido Binta tayi sannan tace "meyasa zamu kirashi kuma Murja? Shin waike bakya tsoron abinda ze biyo baya ne?

Tab'e baki Murja tayi sannan tace " kedai anyi sakarya wllh Binta, nima ai ba  bisa Radin kaina nasa aka satomin Alhaji ba,  kawai nayi hakan ne bisa shawarar da sabon Manajan companyn B.N.M.A   ya bani, sabida na sanardashi cewar mijina babban mutum ne wanda ya mallaki millions of Naira's, amma sedai ban haihu dashi ba, duk wasu tarin kadarorin daya mallaka gab'a d'yara yaransa ya d'ora akan komai, shiyasa duk wasu mahimman abubuwansa baya sanar dani se 'ya'yansa, to shine ya bani shawarar cewa in tura a sato min Alhaji inyaso daga baya senayiwa iyalansa barazana aka indai sunaso mahaifinsu yaci gaba da rayuwa to ya zama dole su kawo min takardun compaynsa na takalma dake garin Abuja, tareda takardun hannun jarin dasuke dashi a k'asar Tokey.

Yanzu haka zancen  danake miki na zuba kud'ad'ena kimanin million 60 a wannan companyn na B.N.M.A  kuma an juyasu harna samu ribar million Ashirin tareda uwar kud'ina, ajiyar zuciya Binta ta saki sannan tace "yanzu kam na gane kuma nima insha Allah da zarar min  k'arasa inda xamu zan saka nawa hannun jarin a wannan companyn na B.N.M.A. sannan ta fara kiran wayar Abdul wanda ke zub'e a kan kafet d'in d'akin Dady, se faman rarrashinsa Baffa gidad'o keyi tareda kwantar masa da hankali.  K'arar wayarsa ce tasa perlourn yayi tsit, Baffa gidad'o ne yayi masa inkiya da hannunsa Alamar ya amsa wayar, dan haka hnnunsa na rawa ya d'aga wayar tareda sanyata a ansakuwa,

Wata uwar dariya Murja ta saki sannan tace" d'ana ya kake ya mutanan yola?  Angaya maka Murja shashasha ce kamar yanda tunaninka ya baka?
Murmushi ta saki sannan taci gaba da cewa "ina ai salon ya dade da canzawa, da alama kuka kakeyi sabida b'atan mahaifinka ko?   Dariya ta kumayi sannan tace " kiranka nayi in sanar dakai cewar na rantse da Allah idan kukai yunk'urin sanar da jami'an tsaro kokuma kace zakabi diddigina wllh kaji na rantse to abakin ran mahaifinka.

Jikinsa ne ya d'au rawa tamkar mazari, dukda irin tafasar da zuciyarsa takeyi hakan be hanashi bata haquri ba, yana kuka yake fadin "don girman Allah karki cutar da mahaifina, wllh bashida Ify, a halin yanzu babu abinda yake buk'ata face kulawar likita!      Kinga kome kike so ki fad'a wllh xan baki amma don Allah karki cutar mana da Dadyn mu na   rok'e ki plsssss,  ya wani ja pls din kamar ze  shid'e.

Kashe wayar tayi tareda sakin wani shaid'anin murmushi,

Kuka Abdul yakeyi bilhaqqi da gaskiya sekace wani k'aramin yaro, dan haka baffan nin nasa suka shiga aikin rarrashinsa, sosai suma lamarin hajiya Murja ya girgizasu, musamman ma kashedin datayi  kan cewar muddin suka sanar da jami'an tsaro to a bakin Ran Dadyn, shiru sukayi aka rasa wanda zece k'ala, dukkansu mamakin Rashin imaninta kawai sukeyi, Baffa Ummaru ne yayi azancin cewa " tunda kunji abinda tace sam be kamata mu shigo da hukuma cikin wannan babban al'amarin ba, tunda dukanmu muji abinda ta fad'a da kunnuwan mu ba gaya mana akayi ba, a Rashin imaninta wllh zata iya aikata abinda tace d'in, don haka babu abinda ya kamata muyi a yanzu face addu'a,  sabida babu abinda yafi k'arfin ubangiji.

Haka kuwa akayi dole suka karb'i shawarar da  Baffa Ummarun ya kawo sabida itakadai ce mafita a garesu,

A nitse take tuk'inta zuciyarta fess, dan haka Binta 'yar kwabo ta kalleta tace, Murja, wai a gidan wa ma zamu sauka ne da wannan mutumin wanda bashida maraba da gawa?  Tab'e baki Murja tayi sannan tace "ni wllh dad'ina dake gaggawa Binta, idan kinyi haquri ai zan sanar dake a inda zamu sauka,  dan haka ki dena damun kanki a gidan manager zamu sauka.

Se wajen bayan sallar ishsha sannan suka isa masaukin su, babu lefi gidan yanada kyau sosai dukda cewar bashida girma sosai amma hakan baze hanaka ganin kyansa na,  nanda nan aka cika musu daining da abinci kala-kala masu rai da lafiya, seda sukaci suka k'oshi sannan hajiya Murja ta fara neman layin manager, nan yake sanar mata da cewar baya nan amma da safe ze dawo, wani kasuwanci companyn su ze gunar na kimanin naira Billion  d'aya, kuma za'a samu riba sosai, nan da nan hajiya Murja tace don Allah itama tanaso ta zuba nata hannun jarin, da farko da manager yaso yaqi Amincewa, sabida bayason harka da k'ananan kud'i amma ta nace, don haka yace to shikenan setayi masa transifar din iya dadadin kud'in dazata zuba a cikin account din companyn, sannan ya shaida mata cewar ze turo motar Asibiti don akai Dady Hospital  sabida idan wani abu ya sameshi tofa duk wani shirinsu ya lalace.

Murmushi tayi sannan tace " karfa ka manta shifa sannan mutum ne, be kamata mukaishi Asibitin gwamnati ba,   shiru manaja yayi tareda nazari akan maganar ta, don haka yace "shikenan zan kira *SUSHMER INTERNATIONAL HOSPITAL* dake centeral Aria Inyaso semu kaishi can tunda babban Asibitin kud'i ne ba lallai hankalin mutane yakai kansa ba, sedai ina me gargad'inki kan cewar da zarar sun tambayeki me yake damunsa ki  gaya musu cewar firgita yayi shine ya suma, daga haka karki k'ara komai, a haka sukayi sallama dashi kan cewar gobe zata tura masa da  kud'in.

Bayan sun kammala wayar da manager, nan ta sanar da Binta duk yanda sukayi dashi. A nan itama ta tubure kan cewar sedai su tura masa da kudin tare, don wllh bazataci ribar mak'udan kudi itakad'ai ba, dariya hajiya Murja tayi, sannan tace " kai Binta kedai Allah yayi miki shege son kud'in tsiya wllh, dariya tayi sannan tace "wazek'i kud'i k'awata?

A haka har motar Asbitin *SHUSMER INTERNATIONAL HOSPITAL* ta iso, cikin mintunan da bazasu gaza shabiyarba suka kinkimi Dady suka sakashi a motar, kafin su tafi dashi seda suka tabbatar sun Auna Bp dinsa, a nan suka tabbatar da jininsa ne ya hau nan suka shiga bashi taimakon gaggawa, cikin mintuna kad'an suka sak'ala masa Drip a hannunsa.

Kukan munafinci Hajiya Murja suka dingayi, hartana kama hannun wata nurse tana cewa " don Allah sister ki taimaka min, wllh bana so in rasa mijina don Allah!!

Murmushi nurse din tayi mata sannan tace "ki kwnatar da hankalinki Hajiya insha Allahu komai zeyi daidai, yanzu dai ki koma cikin gida kuyita masa addu'a ze samu sauk'i da yardan Allah, dak'ar nurse din ta lallab'a Hajiya Murja suka koma cikin gida sannan suka tafi dashi, kasancewar ba'a buk'atar wani mejinya a asbitin shiyasa basu tafi da kowa ba.

Duk wani taimako da Dady yake buk'ata seda suka bashi shi, a k'ark'ashin kulawar Dr. Abdullah, sosai ya tsananta binkice akan rashin lafiyar Dadyn, a nan ya tabbatar da cewr a kwai wata k'waya wadda mara lfiyan yake yawan amfani da ita, hakanne yasa jijiyar dake kai sak'o zuwa ga k'wak'walwarsa ta samu matsala, wanda hakan yay sanadiyar taruwar jini a cikin k'ok'on kansa, hakanne yasa Dr. Abdullah ya kira Dr. Khabeer Mahmoud ya sanar dashi halin da ake ciki, a wannan lokacin khabeer yana zaune a Daining sunayin Deener, gefe guda kuma Farouq ne se tsokanar Baba yake suna kwasar dariya dashi da Usman, seda Abba yaci ubansu sannan suka shiga taitayinsu, mik'ewa khabeer yayi da sauri, sannan ya kalli Abba yace " Abba zan wuce Asitlbitin mu yanzu aikin gaggawa ne ya taso mana, wani mara lfy aka kawo wanda yake buk'atar surgery cikin gaggawa.

Fatan alkhairi iyayen nasa sukayi masa sannan ya karbi mukullin motar Farouq ya nufi k'ofar fita daga perlourn, harya kai k'ofar fita Umaisa tace "all d best yaya Golden.

Dak'uwa yayi mata yana murmushi sannan ya fice, a daren ranar aka shiga da Dady tiater, k'ark'ashin jagorancin Dr. Khabeer Mahmoud Muhammad, cikin ikon Allah da hikimarsa suka samu nasarar kammala tiatern ba tareda wata matsala ba. Sannan aka turoshi zuwa wani d'aki na musamman.

Washe gari tun safe su hajiya Murja suka nufi Banki don turawa manager kud'in da sukayi alk'awari dashi, nan ma batasha wahalaba tatura masa kaf kud'in dake cikin Account d'inta Million 100, inda Binta kuma ta tura masa million 60, a haka sukabar Bankin zuciyarsu fess, bayan sun koma gida ne hajiya Murja ta shiga kiran wayar manager, amma kuma bata shiga, seda ta kirashi sau 6 amma bata sameshi ba, a nan hankalinta ya fara tashi!! k'irjinta ya fara

dukan tara-tara.........
_*🎀KIYARDA DANI...!🎀*_
🎀🐾🎀

*♝ IᗪTᏋʟʟIᎶᏋᗪT WrITᏋr'ی ASSѡ📚✍️*

*💫DEDICATED: to Sis naja'art*

_*WRITING BY: Zm (CHuBaDo)*_

*✨Special Gift for Hafsat Hafnan (my jika),.*

_Page:26_

___________📖Wani uban ashar ta zunduma tareda tuge d'ankwalin leshin dake kanta, nan da nan wani irin gumi ya fara keto mata cikeda tashin hankali, kallon tsaf Binta 'yar kwabo keyi mata sannan tace "ke wai lafiyarki kuwa, naga duk kinbi kin zare kamar wata me tab'in hankali?

Zufar dake goshinta ta goge sannan ta samu zarafin magana cikeda tashin hankali tace " Binta shikenan Binta mun shiga uku mun fad'a komar 'yan damfar.... Zabura Binta tayi tareda shak'o wuyan hajiya Murja cikin karaji tace "kutumar bura'uba wllh Murja baki isa kici Amanar Binta ki zauna lfy ba, ni zaki Rainawa hankali? "Dalla malama sakarmun wuyan Rigata tun kafin in miki Rashin mutunci. Murja ta katseta cikin karaji, harke kin isa ki Rik'emin wuyan rigata Binta?

Tafa hannun Binta tayi sannan tace " k'warai kuwa harma nayi yawa, ke na Rantse miki da girman Allah idan baki dawomin da kud'ad'ena ba wllh sena tona miki Asiri a idon duniya,

A harzuk'e Hajiya Murja tayo kanta, hakanne yayi daidai da tashin k'arar wayar Hajiya Murjan, a hanzarce ta nufi inda wayar take tareda zubawa Screen din wayar idanu, murza idanunta tayi sabida ta tabbatar da abinda idanunta suka gane mata, Sunan *MANAGER* ta gani yana yawo a Screen din wayar, a hanzarce ta answer wayar zuciyarta na dukan tara-tara, murmushi manager yayi sannan yace "im sorry Hajiya, karkiga ban kiraki a waya d'azuba, wata 'yar tafiyace ta kamani daga nan Abuja zuwa legos shiyasa, amma yanzu na dawo dan hka zamu d'ora daga inda muka tsaya akan abinda muke gudanarwa, hka kuma gobe zanzo mugaisa daku sabida muga juna dani dake sabida in tabbatar miki da wani babban al'amari wanda ze jefaki a duniyar Rud'ani gameda kasuwancin da nake shirin k'ullawa.

Wata uwar ajiyar zuciya Hajiya Murja ta saki tamkar wadda aka k'wace daga bakin ingarman zaki, murmushi tayi sannan tace " hak'ik'a Manager kana da abin mamaki wllh, ni gaba d'aya da harna shiga Rud'ani dana kira wayarka ban sameka ba!

Dariya Manager yayi sannan yace "haba madam ai wasa farin girki tukunna, bayanzu ya kamata kifara wannan tunanin ba senan gaba tukunna!

Shiri tayi tana nazarin kalaman Managern, katseta yayi ta hanyar cewa " keda zaki samu ribar kudal'ad'e masu yawa meye naki na fargaba a akai?

Murmushin jin dadi ta saki sannan tace "oh hakane fa Manager na, yanzu dai inanan ina jiran zuwanka goben insha Allah, a haka sukai sallama da Manager zuciyarta fess. se'a lokacin ta juya ta kalli Binta " yar kwabo wadda ta zuba mata idanu tana sauraron duk tattaunawar da sukeyi tace " hmmm Binta kenan na godewa Allah daya nuna min ainihin kalarki a fili na gani, don haka zan dawo miki da Million 60 dinki, inyaso daga ranar dana baki kud'in ki babuni babuke har Abada!! Tunda ke bakisan mutunci ba.

Jikin Binta ne yayi masifar sanyi, musamman ma dataji kalmar aminiyar tata na k'arshe, tabbas idan har tabari suka Rabu da Hajiya Murja to wllh kashinta ya gama bushewa, nan da nan ta shiga bata hak'uri kamar zata ari baki, dak'ar ta samu Murja ta hak'ura harta sakko suka d'an tab'a hira, sannan suka mik'e suka fad'a d'aki mak'ale da juna.

B'angaren Maheer kuwa sosai yaci gaba da bibiyar Rayuwar Umaisa da lamuranta,   amma dukda hakan bata canza zaniba, sosai take garashi son ranta, idan taso iskanci ma ko kallon arzik'i batayi masa idan suka had'u,  amma sam hakan besa Maheer ya rabu da ita ba sema k'ara nane mata dayakeyi, kullum yana hanyar mkarantar islamiyarsu duk dan ya ganta yaji dad'i a zuciyarsa.

Yau ta kama laraba ne don haka Maheer ya k'udurtawa kansa da zuciyarsa cewar yau za'ayita ta k'are a tsakaninsa da Umaisa, dolenta yau ta tsaya ta saurareshi koda ace baxata karb'i soyayyarsa ba.

A nitse take takowa cikin takunta me jan hankali, tun daga nesa ta hangi motarsa wadda ko'a mafarki ta ganta zata shaida mamallakinta,

A hanzarce ya fito daga motar cikin takunsa na isa da k'asaita, jingina yayi da motar tareda sark'e hannayensa a k'irjinsa tareda zuba mata tsimammun idanunsa,  d'auke idanunta tayi da sauri daga kansa, sannan ta maida hankalinta zuwa ga hanyar tafiyarta, harta iso dab dashi ta fara k'ok'arin wuce shi, da sauri yasha gabanta yace "pls Queen don Allah ki tsaya ki saurareni mana wllh dukkan abinda bakina ya furta akanki gaskiya ne, ni kaina bantab'a zaton zan fad'a a tarkon son wata 'ya mace ba Queen, a lokaci gani kawai nake duk mata halinsu d'aya ne, ashe sam abin ba haka yake ba, tabbas malaman kimiyar soyayyah sinyi gaskiya da sukace  so a zuciya yake ba'a idanu ba, haka kuma yayin da guguwar soyayyah zata d'ebi mutum bata shawara dashi balle ta nemi izininsa, Nasoki a lokacin da idanuna basusan kamanninki ba Queen, I love you Queen I really love you with all my heart,  pls Queen say the samething to me honestly kamar yanda na fad'a miki don Allah!  Idan har kika amshi soyayya ta da dukkan zuciyarki  I promise  to be yours forever and Ever Queen!!!!

*KIYARDA DANI* dukkan abinda zan fad'a miki babu komai a cikinsa face tsantsar gaskiya da da zallar Aminci a cikinsa.

shiru tayi ta kasa magana, tabbas idan tace batajinsa a ranta tayi k'arya, sabida duk inda masoyin gaskiya yake Maheer yakai ayi kwatance dashi, inda ace soyayyarsa bata gaskiya bace wllh baze tab'a jure irin abubuwan datake yi masa ba, a lokacin dayake expresing mata irin sonda yake mata ta tsinci wani babban abu a  kalamansa da kuma idanunsa, babu komai a cikinsu face tsantsar tsagwaron gaskiya.

Kasa magana tayi lokaci guda kuma ta maida kallonta ga kyakkyawar fuskarsa ma'abociya kwarjini da kuma haiba, kasa jure kallon k'wayar idanunsa tayi dan haka da sauri ta juya ta fara tafiya, binta yayi da sauri sannan ya sake tsayarda ita yace " Queen ki gayamin dukkan abibda yake Ranki a gameda ni, duk abinda zuciyarki ta fad'a miki Akan Maheer Lamid'o kawai ki fad'eshi, koda ace zezama  barazana ga Rayuwata nayi miki alqawarin cewar zan fahimceki, kuma zanyi miki uziri akansa Queen! Idan ma bakya sona ne wllh ki sanar dani nikuma nayi miki alk'awarin cewar bazan k'ara bibiyarki ba har abada!!

Juyowa tayi a firgice tana kallonsa sabida yanda kalamansa na k'arshe suka firgita duk wata nutsuwa dake tareda ita. Girgiza masa kai tayi hawaye na bin kumatunta wanda yake baiyana tsantsar tsagwaron soyayyar datakeyi masa, a raunane tace " taya Queen of tears zata iya Rayuwa batareda Maheer Lamid'o ba?  Idan har soyayyar dakakemin gaskiyace meyasa zuciyar Umaisa zata kasayin Uziri gareka Maheer?  Wllh banajin a kwai Ranar dazatazo zuciyar Umaisa ta buga batareda d'ingon amon soyayyarka a ciki ba Maheer!!!! *KA YARDA DANI* ina sonka with all my heart!    Se'a lokacin kukan datake dannewa ya samu nasarar k'wace mata.

Kasak'e yayi yana kallonta zuciyarsa na k'ara ruruwa da wutar k'aunar ta, tareda jinjinawa jarumtar yarinyar, tunda harta iya b'oye abinda ke ranta harta kasa fitar dashi se'a yanzu, wani irin farin ciki ne ta ziyarci zuciyarsa lokaci guda ya juya wajen motarsa se faman murmushi yake mata,  motar ya fad'a tareda barin unguwar zuciyarsa fesss sabida ya samu cikar burin Rayuwarsa.

Motar tabi da idanunta harta dena ganinta sannan ta juya ta nufi islamiya zuciyar ta a cikeda farin ciki.

Washe gari da safe kamar yanda Manager yayiwa hajiya Murja alk'awarin zezo  don suga juna Akan maganar plan dinsu na gaba da zasu gudanar kuwa haka akayi,  wajen misalin k'arfe biyar na yammacin alhamis Manager ya dira a cikin gidan,  sanye yake cikin K'ananan kaya wa'yanda suka baiyana cikar zatinsa da kuma haibarsa,  inda kansa ke sanye cikin bak'ar hular p cap, idanunsa sanye suke  cikin wani bak'in glass k'irar Companyn prada, k'afafunsa kuma a sulke suke cikin wani bakin takalmi k'irar Companyn Batozy, a nitse yake takawa harya tura k'ofar perlorn ya kunna kai ciki,  Babu kowa a perlourn se binta 'yar kwabo dake kallon wani

Hausa film, a k'asaice ya shigo perlourn ya zauna tareda hard'e k'afafunsa, a dake ya kalli Binta 'yar kwabo yace " kiramin Hajiya kice mata Manager ne yazo, washe baki tayi da sauri ta mik'e tace "0h to bari na sanar da ita, jikinta har rawa yakeyi sabida tasan maganar kudi ce ta kawo shi, tana shiga ta sanar da Hajiya Murja, kusan a tare suka fito perlourn,

da sakin fuska Hajiya Murja tace " maraba da Manager gidan kud'i yau dai gani gaka Allah ya yarda, ta fad'a tana dariya harta zauna.

Kallon tsaf Manager yayi musu cikin bak'in  gilashin dake manne a idanunsa, murmushi yayi me sauti sannan yace "kamar yanda na fad'a miki a baya Hajiya yanzuma zan sake maimaita miki cewar duk d'an daya haifu  cikin Uwarsa da kuma ubansa tofa dole ne ya kasa  manta kamannin mahaifiyarsa, musamman ma idan wani ko wata ya zama silar zubar  hawayen wannan  mahaifiyar tasa kokuma silar rushewar Ahalinsa, azoton ki kokuma tunaninki ya zafin wutar fansar dakeci a zuciyarsa zata kasance yayin da yayi arba da abin harinsa agabansa???

Zaro idanu tayi cikeda tsantsar tsagwaron tashin Hankali take nunashi, lokaci guda miyan bakinta ya k'afe k'af sabida tsabar tashin hankalin datake ciki, dak'yar ta iya tattaro kalaman dake bakinta tace " mmmm... ..Mah...eer!!!

_*🎀KIYARDA DANI...!🎀*_
🎀🐾🎀

*♝IDTɵ||IG'ɵDT WrITɵr'ى  ASSɷ📚✍️*

*💫DEDICATED: to Sis naja'art*

_*WRITING BY: Zm (CHuBaDo)*_

*✨Special Gift for Hafsat Hafnan (my jika),.*

_Page:27_

____________📖 wani killer murmushi ya saki sannan ya sake maida kallonsa garesu a karo na biyu, tab'e baki yayi sannan ya zare p cap din dak e kansa, a wannan lokacin babu abinda ke ci a zuciyarsa face wutar fansa, glass d'in idonsa ya zare tareda d'ago dara-daran idanunsa wa'yanda suka fara canza launi sabida fishi, nan da nan jijiyoyin kansa da wuyansa suka mimmik'e, a nitse ya fara takawa har zuwa gabanta, wuyan ta ya dank'a da dika hannayensa sannan ya wani shak'eta yace "shin zaki iya tuna ranar *28/12/1997 k'arfe 9:30pm* na dare?  To idan kin manta bari tafin hannuna ya tuna muki!  Ya fad'a tareda d'auketa da wani mahaukacin mari, wanda yasa taga wasu jajayen taurari sunayi mata shawagi a tsakiyar kanta.

Kwarfeta yayi tafad'i tim a k'asa har seda kanta ya bugu da K'aramin table din glass din dake perlourn ya fashe, wata razananniyar k'ara ta saki lokaci guda tareda fashewa da wani irin kuka, dariya Maheer ya saki wadda iyakacinta lips dinsa, lokaci guda kuma hawaye suka fara zubo masa tamkar bazasu tsayaba, sunkuyawa yayi dab da ita sannan yace "meyasa kika saka momyna kuka? Me tayi miki a rayuwa wanda yasa kikazama silar rusawar Rayuwarta?

"Shin meye laifin Mu da kika zama silar Rabamu da mahaifiyarmu? A sanadin abinda kika aikatawa Momy yau gashi an wanyi gari mun rasata, tatafi tafiya ta har abada kuma duk *KECE SANADI!!* dan haka na rantse da wanda raina yake hannunsa sena d'and'anawa Rayuwarki irin kwatankwacin bak'in cikin da kika d'and'anawa tamu Rayuwar damu da mahaifiyar mu! haka kuma sena sauyawa miki rayuwarki ta hanyar k'ask'antar dake mafi munin k'ask'anci, tayanda sekin gwammaci mutuwarki akan komai, bazan tab'a barinki ki zauna lfy muddin ina raye sena tabbatar da cewa na dasa miki bak'in cikin da zaki rayu dashi a cikin zuciyarki har zuwa ranar da ajali ze riskeki riskeki!!

Mik'ewa yayi tareda k'arasawa gaban Binta 'yar kwabo wadda ta takure a guri d'aya sabida tsoro da kuma tashin hankali, murmushin gefan baki yayi tareda wurga mata wani matsiyacin kallo wanda yasa duk taji ta muzanta a gabansa sannan yace "saurin me kikeyi haka? Aike banzo kankiba tukunna sabida ban fara nazari akan irin azabar dazan yi miki ba, don haka seki zauna cikin shiri kafin na juyo kanki!

Ficewa yayi daga perlourn zuwa waje, a farfajiyar gidan ya tsaya tareda k'wallawa Lawan mai gadi kira kamar ze fasa gidan sabida b'acin Rai, a hanzarce Lawan ya k'araso gurin tareda sunkuyawa cikeda ladabi yace " ayi hak'uri Ranka ya dad'e Uziri ne ya kamani shine na kewaya,

A tak'aice Maheer yace " ina ma'aikatan danace ka samomin?

Cikeda girmamawa Lawan yace yallab'ai suna d'akin dake baya a can na saukesu kamar yanda kabada Umarni, murmushi Maheer yayi sannan yace " dakayu, maza kaje ka kira min su kuzo tare, da Hanzari Lawan ya mik'e don cika umarnin da aka bashi, cikin minti kad'an se gashi ya dawo tareda wasu manyan halittun 'ya'yan arna a bayansa,

Sanye suke cikin wasu riguna wayanda suka tsaya musu iya gwiwarsu sabida girmansu, hakanne ya bani damar k'arewa damatsan k'afar su kalo, a murd'e suke sosai ga tsayi ga kuma kauri, kaida ka gansu zaka fahimci sunji noma, sabida tsoron da suka bani har seda alk'alamina ya fad'i k'asa, itakuwa *JANAF* suna had'a ido da ita ta zura da gudu ta cika wandonta da iska😂😂

A haka suka k'araso gurin suka tsaya, cikeda girmamawa suka fara gaida maheer wanda ya shagala da kallon irin girman halittarsu Victoria da kuma Yukeria,

Tab'e baki yayi sannan yace "kubiyoni, babu musu suka mara masa baya, se faman sauke

numfashi suke sabida tsabar k'ibar da suke dashi, a haka suka kunna kai cikin perlourn, cikeda k'asaita ya zauna akan d'aya daga cikin kujerun perlourn yana k'arewa su murja kalo cikeda tsana,  Binta 'yar kwabo kuwa tunda tayi ido hud'u dasu Victoria ta saki futsari a wandonta sabida yanda ta tsorata dasu.

Cikin harshen turanci Maheer ya kallisu Victoria yace " aikinku a gidannan shine, kullum idan kuka tashi da safe ku tabbatar kun fitar da wa'yannan matan waje kun zanesu duka me lafiya, sannan ku sakasu su goge duk wani lingu da sak'on dake cikin gidannan,  haka kuma kafin su kwanta ma ku tabbatar jikinsu ya gaya musu sannan ku  maidasu d'akin da aka sauke ku a ciki su dinga kwana,  se kuma abu na k'arshe banyarda kubasu abincin daya wuce garin kwaki ba.

Cikeda ladabi suka amsa da "yesss sair, shin zamu iya fara aikinmu daga yanzu?      Tab'e baki yayi sannan yace " why not.

Tun kafin ya rufe baki Victoria ta sab'i hajiya murja a kafad'a tayi waje da ita, hakama Yukeria itama ta cakumi Binta 'yar kwabo sukayi waje dasu, duk irin ihun da sukeyi hakan besa sun k'yalesu ba seda sukayi musu lilis sannan suka k'yalesu.

_*🎀KIYARDA DANI...!🎀*_
           🎀🐾🎀

*♟IᗪTҽ||IƓҽᗪT WɾITҽɾ'ى  ASSⲱ📚✍*

*💫DEDICATED: to Sis naja'art*


_*WRITING BY: Zm (CHuBaDo)*_

 *✨Special Gift for Hafsat Hafnan (my jika),.*


_Page:28_

___________📖 tun kafin a rufa sati su Hajiya Murja suka fita haiyacinsu, duk sunbi sun kod'e sun jeme tamkar basu ba, sabida yanda rayuwa ta juya musu, tun ba'aci litinin da talata ba tuni suka sare da lamarin maheer, Binta 'yar kwabo kuwa ta tsinewa Maheer yafi cikin kwando dubu,

*SUSMER INTERNATIONAL HOSPITAL ABUJA*  sosai Dady yake samun kulawa a k'ark'ashin jagorancin Dr.khabeer mahmoud, sosai khabeer yakejin tausayin Dady tareda nuna duk wata tausayawarsa gareshi, don haka sabo na musamman ya shiga tsakaninsu dashi, har wasu lokutan Dady yakanji wani irin bak'on yanayi a tareda khabeer d'in,  b'angaren Maheer shima yanayin iya bakin k'ok'arinsa wajen kulawa da mahaifin nasa dukda baya zuwa Asbitin se sanda Dadyn yake bacci sannan yake zuwa, sosai yakejin kewar  mahaifin nasa, amma kuma babu

yadda ya iya dole ne yaci gaba da hak'uri har zuwa ranar da komai ze daidai ta.

Yau ta kama monday ne, don haka tun safe Umaisa ta shirya cikin uniform dinta don zuwa makaranta,  d'akin Baba ta shiga da sallamarta, a bakin gado ta samu Baba ta rafka uban tagumi, dariya Umaisa tayi sannan tace "ke fitinanniyar tsohuwa meye matsalarki ne haka? Cire tagumin Baba tayi sannan ta fashe da kuka harda sharar hawaye,  zuru Umaisa tayi tana kallonta sannan tace" ikon Allah yau naga abinda ya isheni ni Fatimah! Me nayi miki zaki sani a gaba kinamin kuka?

Bakin zaninta ta kama tana goge hawayen fuskarta tareda fad'in "Na shiga Uku ni Binta da lamarin Mamuda gabad'aya  gidannan a cike yakeda yahudanci kala-kala,  yanzu fisabilillahi ki kalli yarannan su Khabeeru da Faruku gaba d'ayansu sun zama magidanta amma babu Aure nikam wllh inajiyewa kaina tsoron abinda zeje yazo,  nan kuma gaki ga Rumana dukkan ku Nono ya gama cika muku k'irji amma kuma babu mijin Aure, ta k'are maganar tana sharar k'wallah.

Tinda ta fara magana Umaisa ta had'e rai tanayi mata wani kallo, tab'e baki tayi sannan ta mik'e tace" lallai ma tsohuwar nan kin zak'e dayawa, to ai seki samomana mazajen da zamu aura d'in tunda akanki muke zaune, ni wllh nazata ma wani abin arzik'in ne yake damun ki shiyasa ma na tsaya ina b'atawa kaina lokacin sauraronki. Ta fad'a tana k'unk'uni,   wata uwar harara Baba ta zabga mata, sannan tace "yau naji tsigalalliyar yarinya, waiyyo Allah na  binta! To kinga  Uwar ki Badi'atou kikayiwa da ubanki Mamuda, shegiya kod'ad'd'iya me zubin sadakar yallah.

Banza tayi mata ta nufi hanya tana murgud'a mata mazaunai harta fice daga d'akin, Abbah ta gani kawai a daining se kuma Ruman da ya Khabeer suna Breakfast, kusa da Abba taje ta zauna tareda fad'ad'a fara'arta tace "My Abie ina kwana?

Shafa gefan fuskarta Abba yayi sannan yace " lafiya lau sweetheart,  fatan Babyn Abba ta tashi lfy?        Washe baki tayi sannan tace "na tashi lfy mah Abie.

Se'a lokacin ta kalli ya khabeer tace "morning ya Golden .

D'ago manyan tsimammun Golden Eyes d'insa yayi ya zuba matasu har tsahon  3minute yana nazarinta, sannan ya maida hankalinsa kan chips din dayake ci,  haka kawai idan ya kalleta yanzu seya kasa gane ma'anar canjin dayake tareda ita, musamman idan tana gudanar da wasu abubuwan seyaga ita kad'ai tana murmushi, gashi sam batason zama a perlour kamar yanda ta saba kullum tana d'aki sekace wata Amarya.  Tsaki yayi tareda mik'ewa ya kalli Abba yace " Abba ni zan wuce Office. Da sakin fuska Abba yace "to Allah ya bada sa'a son.

Kwab'e fuska Ruman tayi sannan tace " ya Golden yune fa Birthdayn Aunty Beebah, don Allah ya khabeer kaje damu idan zaka, d'azu naji Tana gayawa Ummie.   Wata uwar harara ya wuga mata sannan yace" ba inda zakije magulmaciya, wato lab'e ma kikeyiwa mutane shiyasa ma har kikaji maganar birthday d'in ko?

Turo baki tayi sannan tace "a'a wllh ya khabeer ba lab'e nakeyi ba, ummien ce da kanta ta fad'a min d'azu danaje d'akinta gaida ita. Ta k'are maganar tana kallonsa,

Kallonta Umaisa tayi sannan tace " kema maganin ki, ni wllh Abba bana ma son shiga sabgar Wannan Aunty Beebahn, sabida gabad'ayanta bata da mutunci sosai kamar Aunty Maryam, wllh Abba dama ka hana Auren yaya Golden da i........ "Keep quete mara kunya kawai! khabeer ya katseta ta hanyar daka mata wata shegiyar tsawa me firgita zuciya, ni sa'anki ne da zaki dinga magana a kaina kamar wani tsaranki?
_*🎀KIYARDA DANI...!🎀*_
🎀🐾🎀

*♝ IᑎTɵ||IǤɵᑎT WгITɵг'ی ASSɷ📚✍️*

*💫DEDICATED: to Sis naja'art*

_*WRITING BY: Zm (CHuBaDo)*_

*✨Special Gift for Hafsat Hafnan (my jika),.*

*_Jama'a Assalamu'alaikum🙏. Ina makaranta litattafan hausa da kuma nazarinsa?_*
*_ina me sanar daku cewar, Shahararriyar marubuciyar nan wadda tayi fice a cikin duniyar marubuta wato Sis NAJA'ART, tazo muku da sabon salon da ba'a tab'a zuwar muku da kamarsa ba a duniyar marubuta ba, a cikin littafinta me taken FANSAR RAI.!!! littafin daya tara tsagwaron sark'ak'iya a cikinsa mai wahalar warwarewa, maza ku garzaya ku nemu naku akan farashi naira 200 kacal😁_*

_Page:28_

___________📖 Tun kafin a rufa sati su Hajiya Murja suka fita haiyacinsu, duk sunbi sun kod'e sun jeme tamkar basu ba, sabida yanda rayuwa ta juya musu, tun ba'aci litinin da talata ba tuni suka sare da Al'amarin maheer d'in, sabida duk yanda suke zaton sa ya zarce tunaninsu, Binta 'yar kwabo kuwa ta tsinewa Hajiya Murja yafi cikin kwando dubu, sabida a cewarta wai duk itace ta jefasu a cikin halinda suke ciki,

Wata Ranar Asabar d'in k'arshen mako ne Hajiya Murja tana goge kujerun k'arfen dake farfajiyar Garding din gidan, wanda aka tanada domin hutawa ta musamman, akan hanyarta na komawa ne ta cake da wani dogon k'arfe wanda Babu komai a jikinsa face tsatsa, nan ta durk'ushe a gurin tana kurukuwar neman d'auki, Victoria ce ta nufota da sauri fuskarnan Babu annuri balle a samu tausayawa a cikinta tace "ubanka ka tsayayi a nen? Tun kafin tayi magana

taji saukar bulala a gadon bayanta, seda tayi mata lilis sannan ta kwasheta ta jefa a d'aki ta Rufeta da mukulli.

*SUSHMER INTERNATIONAL HOSPITAL ABUJA* sosai Dady yake samun kulawa a k'ark'ashin jagorancin Dr.khabeer mahmoud Muhammad, sosai khabeer yakejin Dady a Ransa tareda nuna duk wata tausayawarsa gareshi, don haka wata irin shaguwa gamida sabo na musamman ya shiga tsakanin Dady da khabeer, wasu lokutan idan Dady yana tareda Khabeer yakanji wani irin bak'on yanayi a tareda khabeer d'in wanda shi kansa yakan gaza gane ma'anar hakan,

b'angaren Maheer shima ba'a barshi a bayaba yanayin iya bakin k'ok'arinsa wajen kulawa da mahaifin nasa, dukda cewar baya iya zuwa Asbitin da Rana har se sanda Dadyn yake bacci sannan yake zuwa, sosai yakejin kewar mahaifin nasa, amma kuma babu yadda ya iya dole ne yaci gaba da hak'uri har zuwa ranar da komai ze daidai ta.

Yau ta kama monday ne, don haka tun safe Umaisa ta shirya cikin uniform dinta don zuwa makaranta, d'akin Baba ta shiga da sallamarta, a bakin gado ta samu Baba ta rafka uban tagumi, dariya Umaisa tayi sannan tace "ke fitinanniyar tsohuwa meye matsalarki ne haka? Cire tagumin Baba tayi sannan ta fashe da kuka harda sharar hawaye, zuru Umaisa tayi tana kallonta sannan tace" ikon Allah yau naga abinda ya isheni ni Fatimah! Me nayi miki zaki sani a gaba kinamin kuka?

Bakin zaninta ta kama tana aikin sharar hawayen dake fuskarta tareda fad'in "Ya naga abinda yafi Qarfina ni Binta!! Wllh gabad'aya lamarin Mamuda ya gama tsayamin a rai, yo hakane mana 'yar nan, ace gaba d'aya lamarin gidan mutum an gama cikashi da yahudanci kala-kala? yanzu fisabilillahi ki kalli yarannan su Khabeeru da Faruku gaba d'ayansu sun zama magidanta amma babu Aure kuma duk yabi ya zuba musu ido sekace wani sakare? nikam wllh inajiyewa kaina tsoron abinda zeje yazo, nan kuma gaki ga Rumana dukkan ku Nono ya gama yi muku sammako a k'irjin ku, Babu mijin Aure kuma dukda hakan ya zuba muku ido yana kallonku wai ku karatu. ta k'are maganar tana sharar k'wallah.

Tinda ta fara magana Umaisa ta had'e rai tanayi mata wani kallo, tab'e baki tayi sannan ta mik'e tace" lallai ma tsohuwar nan kin zak'e dayawa, to ai seki samomana mazajen da zamu aura d'in tunda akanki muke zaune, ni wllh nazata ma wani abin arzik'in ne yake damun ki shiyasa ma na tsaya ina b'atawa kaina lokacin saurarонki. Ta fad'a tana k'unk'uni, wata uwar harara Baba ta zabga mata, sannan tace "yau naji tsigalalliyar yarinya, waiyyo Allah na binta! To kinga Uwar ki Badi'atou kikayiwa da ubanki Mamuda, shegiya kod'ad'd'iya me zubin sadakar yallah.

Murgud'a mata baki Umaisa tayi sannan tace " oho dai naji d'in, ai wllh garama ni inada kyan fasali, kekuwa daza'a kasaki a faranti ma wllh Babu me d'aukarki sadaka ma ballantana da kud'insa, ta fad'a tana juyi a gaban Baba.

Tab'e baki Baba tayi sannan tace "ai duk tsiyarku dole ne kuyi aure yau da kaina ba aikeba zan

samu Mamudan inyaso se'inga ta tsiya, washe baki Umaisa tayi sannan tace " oho dai nidai ba yanzu zanyi Aure ba har sekin mutu sannan zanyi Aure don haka duk bala'inki sekin mutu zamuyi shagalin Bikin gidannan, ta fad'a tana dariyar tsokana tareda murgud'a mata mazaunai harta fice daga d'akin, Abbah ta gani kawai a daining se kuma Ruman da ya Khabeer suna Breakfast, kusa da Abba taje ta zauna tareda fad'ad'a fara'arta tace "My Abie ina kwana?

Shafa gefan fuskarta Abba yayi sannan yace " lafiya lau sweetheart, fatan Babyn Abba ta tashi lfy? Washe baki tayi sannan tace "na tashi lfy mah Abie.

Se'a lokacin ta kalli ya khabeer tace "morning ya Golden .

D'ago manyan tsimammun Golden Eyes d'insa yayi ya zuba matasu har tsahon 3minute yana nazarinta, sannan ya maida hankalinsa kan chips din dayake ci, haka kawai idan ya kalleta yanzu seya kasa gane ma'anar canjin dayake tareda ita, musamman idan tana gudanar da wasu abubuwan seyaga ita kad'ai tana murmushi, gashi sam batason zama a perlour kamar yanda ta saba kullum tana d'aki sekace wata Amarya. Tsaki yayi tareda mik'ewa ya kalli Abba yace " Abba ni zan wuce Office. Da sakin fuska Abba yace "to Allah ya bada sa'a son.

Kwab'e fuska Ruman tayi sannan tace " ya Golden yune fa Birthdayn Aunty Beebah, don Allah ya khabeer kaje damu idan zaka, d'azu naji Tana gayawa Ummie. Wata uwar harara ya wuga mata sannan yace" ba inda zakije magulmaciya, wato lab'e ma kikeyiwa mutane shiyasa ma har kikaji maganar birthday d'in ko?

Turo baki tayi sannan tace "a'a wllh ya khabeer ba lab'e nakeyi ba, ummien ce da kanta ta fad'a min d'azu danaje d'akinta gaida ita. Ta k'are maganar tana kallonsa,

Kallonta Umaisa tayi sannan tace " kema maganin ki, ni wllh Abba bana ma son shiga sabgar Wannan Aunty Beebahn, sabida gabad'ayanta bata da mutunci sosai kamar Aunty Maryam, wllh Abba dama ka hana Auren yaya Golden da i........ "Keep quete mara kunya kawai! khabeer ya katseta ta hanyar daka mata wata shegiyar tsawa me firgita zuciyar wanda akayiwa. ni sa'anki ne da zaki dinga magana a kaina kamar wani tsaranki?

Shiru tayi tareda k'ank'ame Abba kamar zata shige masa masa ciki, kasa d'agowa tayi sabida yanda ta gama tsorata dashi, tsaki yayi sannan ya fice daga gidan zuciyarsa a dagule, koda yaje office ma be wani zagaya wrds d'in kamar yanda ya saba ba, sabida gaba d'aya baya cikin yanayi mai dad'i key ya murzawa office d'in sabida baya soma wani yazo ya takura masa.

Se wajen 4 daidai sannan ya bud'e k'ofar sabida zuwa masallaci, a hanyarsa ta komawa office d'in sukai kacib'us da Dr. Abdullah, wanda ke sanye cikin riga da wandon farin boyal wanda sabida haskensa har farar singlet d'in jikinsa ana gani, tab'e baki khabeer yayi sannan ya rab'a ta gefansa ze wuce, tareshi Dr. Abdullah yayi sannan yace " ohhh khabeer wai har zuwa wani lokaci zaka canza hali ne malam?

Tureshi khabeer yayi sannan yace "kaga malam i need to rest don Allah bana son wani dongon surutun ka don Allah! Kasak'e Dr. Abdullah yayi yana kallonsa, dan haka ya matsa ya bashi hanya ya wuce, Direct d'akin da aka kwantar da Dady ya nufa don ya sake duba yanayin jikin nasa, da sallama ya tura k'ofar glass din dake d'akin tareda kunna kai zuwa ciki, a xaune ya sameshi yana yana kallon News, da sakin fuska Khabeer ya k'arasa gareshi tareda zama a gefansa, murmushi dady yayi irin na Dattijawa sannan yace " sannu da zuwa Dr.

B'ata fuska Khabeer yayi sannan yace "har sonawa zan cigaba da tuna maka cewar nima tamkar d'a nake a gareka Alhaji? Murmushi Dady yayi sannan yace " ai sanin hakanne ma yasa nake kiranka da Dr. Sab'anin kai dakake kirana da Alhaji.

Shafa lallausar sumar dake kansa Khabeer yayi sannan yayi murmushi yace " ai hakan ma tamkar manuniya ce dazata nuna maka tabbacin cewar Dr. Khabeer Mahmoud d'ane a gareka Dady.

Hannunsa Dady ya mik'a tareda shafa kan khabeer d'in , nan da nan kewar gudan jininsa suka cika zuciyar sa, se'a yanzu yakejin cewar tabbas ya tabka babban kuskuren da baze tab'a iya gyarashi ba, yanzu ta ina ze fara neman gudan jininsa? Wasu zafafan hawaye ne masu zafi suka shiga yi masa zarya a kan fuskarsa zuciyarsa nayi masa zafi bisa abinda ya aikatawa gudan jininsa haka kuma jajirtaccen d'ansa maheer!

Dafa kafad'unsa khabeer yayi tareda fad'in "ya salam! Haba Alhaji don Allah, meyasa kake zubarda hawaye irin haka bayan kuma kasan condition d'in da kake ciki? Murmushi Dady yayi wanda yafi kuka ciwo sannan yace " hak'ik'a idan wani babban al'amari ya sark'e zuciyar d'an Adam yakan zama mai wuyar warwarewa, musamman idan abubuwa biyu sukaci karo da juna sekaga an gagara shawo kan matsalar balle akaiga warwareta Docter. A halin danake ciki a yanzu babu wani magani wanda ze iya zama maganin damuwata face Yawan ambaton Allah da kuma neman agajinsa! Ya fad'a tareda fashewa da wani irin kuka mai tab'a rai.

Shiru Khabeer yayi yana nazarin maganganun Dady, wanda ya kasa warwaresu balle ya fahimci ma'anarsu, mik'ewa yayi zuciyarsa babu dad'i, a matsayinsa na likita dole ne yayi dik me yuwuwa yaga ya datatar da zubar hawayen wannan adalin dattijon kobabu komai a k'alla ze samu nutsuwar zuciya, hugging d'insa khabeer yayi a ransa yana mai tausayawa Masa.

Maheer ne zaune bisa dank'areriyar Royal chir d'in dake perlourn. Inda Hannunsa ke sanye cikin system d'in sa yana typing, seda na matso dabdashi sannan na fahimci sak'o yake k'ok'arin turawa, seda ya kammala rubuta sak'on sannan ya turawa Baffa Gid'ad'o ta Email d'in sa.

*KADUNA STATE*

Sosai hankalin Abdul a gama tashi, lokaci guda kuma dik yabi ya rame sabida Rashin kwanciyar hankali da nutsuwar zuciya, Dukda irin kulawar dayake samu agurin baffannin nasa,

sosai suke kwamtar masa da hankali inda wani b'angaren kuma suka sa aka tsananta addu'a akan b'atan Dadyn.

Wayar Baffa gid'ad'o ce tayi k'ara alamar shigowar sak'o, sharewa yayi batareda ya dubaba, sabida tashin hankalin dayake ciki ya wuce munzalin tsayawa duba massage, Baffa Umaru ne yace "zuwa yanzu kam gaskiya ya kamata ace mun d'auki mataki akan b'atan Lamid'o, sabida sam be kamata muzubawa al'amarin idanu ba. " tabbas kam maganarka gaskiya ce Baffa Iyah ya fad'a cikin harshen fulatanci, sannan yaci gaba da cewa "taya zamu zuba ido muna kallon mace tana juyamu sekace wasu sakarkaru? Gaskiya we have to take some action akan wannan babban al'amarin dake shirin tinkaro mu.

Qarar wani sak'on ce ta sake shigowa wayar Baffa gidad'on, tsaki ya d'anyi sannan ya maida hankalinsa zuwaga wayar don ganin sak'on menene haka aketa faman turo masa dashi ne haka???
_*🎀KIYARDA DANI...!🎀*_
🎀🐾🎀

*♝IᗪTᏋ꒒꒒IᏀᏋᗪT WᏒITᏋᏒ'Ꮥ ASSᏇ📚✍*

*💫DEDICATED: to Sis naja'art*

_*WRITING BY: Zm (CHuBaDo)*_

*✨Special Gift for Hafsat Hafnan (my jika),.*

*_Yau page d'in naki ne me gaiya me aiki our Boss (REAL MOMYN AFRAH). Na mallaka miki shi halak malak kiyi duk yanda kikaga dama dashi mallakinki ne, kome Intelligent writers suka zama a Duniya kece sanadin faruwar hakan, don haka muna alfahari dake Aunty maryma Allah kuma ya Qaramiki Ify our boss❤_*

_Page:29_

Banyi Editing ba🙅‍♀️

___________📖 Yana duba sak'on da aka turo masa yay zumbur ya mik'e tsaye, lokaci guda kuma ya xube akan gwiwoyinsa tareda kai goshin sa k'asa don yin godiya ga Allah (S.W.T), sarkin da jinsa da ganinsa basa shud'ewa. Nan Baffa Gidad'o ya shiga yiwa Allah kirari tareda ambaton Ubangiji da sunayen dayafiso kuma yafi son a rok'eshi dasu *(Al-Haiyyu Al-Qaiyyum)* sannan ya d'ago yana mai fad'ad'a murmushinsa a garesu,

Kallon mamaki dukansu su Ukun suke bin Baffa Gidad'on dashi, Baffa Umaru ne yayi k'arfin halin cewa "Gidad'o wai meyake faruwa ne haka? Ya kamata ka sanar damu abinda ke faruwa

ko muma masamu hankalin mu ya kwanta,  murmushi Baffa Gidad'o ya sakeyi a karo na biyu sannan ya fara magana kamar haka "hak'ik'a masu iya magana sunyi gaskiya da sukace kyan d'a ya gaji Ubansa, sannan kuma dukkan abinda bawa ya gaza yiwa kansa muddin ya mik'a al'amarinsa ga Allah to Babu shakka Ubangiji ze isar masa.!     Kallonsa kawai su Baffa Umaru sukeyi  ba tareda kowannensu yace dashi k'ala ba.

Ajiyar zuciya ya sauke sannan yace " Lamid'o dai yanzu  baya tareda Hajiya Murja, a yanzu haka yana nan a k'ark'ashin kulawar Maheer.  Zabura Abdul yayi ya mik'e tsaye tareda zubawa Baffa Gidad'o manyan idanunsa wayanda ke cikeda k'walla yace "dnt say that Baffa Gidad'o pls, how is that possible ace Dady yana tareda ya Maheer bayan dukan mu musan cewar ya Maheer ya dad'e da barin cikin ahalinsa? Idan ma kunayin hakan ne don ku kwantarmin da Hankali don Allah ku dena na rok'e ku, karku mantafa nima musulmi ne mai imani kamar kowa, don haka na yarda da k'addara maikyau ko mara kyau kuma na shirya karb'arta a duk yanda tazo min!

Takowa Baffa Gidad'o yayi har zuwa gaban Abdul d'in sannan ya dafa kafad'unsa yace "tabbas dukann mutum mai imani dole ne ya yarda da dukkan k'addarar da Allah ya aiko masa da ita Abdul, kamar yanda kaji na fad'a to haka maganar take *KAYARDA DANI* cewar mahaifinka yana tareda d'an uwanka Maheer, don haka yanzu base anjima ba zamu kama hanyar Abuja don muje mu duba lafiyar Lamid'o.

Haka kuwa akayi kamar yanda Baffa Gidad'o ya fad'a hakanne ya kasance, Inda Baffa Umaru ya kwashesu a cikin d'aya daga cikin motocin gidan suka kama hanyar Abuja. tofa  sedai muce a sauka lfy mutanan yola zasu Abuja😂

*LEGISLATIVE  QUATER APO ZONE E ABUJA*, Umaisa ce kwance bisa madaidaicin gadon dake d'akinta, sanye take cikin wata doguwar rigar atamfa wadda aka k'awata d'inki da fararan stons da kuma adon ja a jiki, kasancewar launin atamfar a kwai launin ja a jikinta,  sosai ta karb'i jikinta tareda futo da ainihin hasken fatarta,  kunnenta a manne yake da wayar tallphone din dake ajiye bisa Bedside drower din dake manne a jikin gadon, kallo d'aya zakayi mata ka fahimci tana cikin duniyar nishad'i gamida mayen soyayyah,  murmushi naga tayi wanda yay silar baiyanar fararan hak'oranta, lokaci guda kuma ta shagwab'e fuska cikin sigar shagwab'a tace "uhmm nidai ban yarda ba, wllh yau nakeso na ganka kuma ba'a hanyar islamiya ba!

Ajiyar zuciya Maheer ya sauke sannan yace " Queen wai meyasa abin kuka baya miki wahala be? To shikenan naji  zanzo amma da sharad'i.  Washe baki tayi sannan tace " na yarda da dukkan sharad'inka My Jan!   Wani irin sanyi ne gamida nutsuwar xuciya sukayi masa dirar mikiya a ilahirin jijiyoyin jikinsa, sabida jin irin sunan da Queen d'insa ta kirashi dashi,  komai nata burgeshi yakeyi musamman ma yanda take nuna masa kulawa da tattalinsa, "baka fad'amin sharad'in naka ba My jaan, Umaisa ta katseshi cikin sanyin muryarta wadda ke d'auke da wani sirri  a cikin ta.

Ajiyar zuciya ya sauke sannan yace " zan fad'a miki idan nazo anjima, shagwab'e masa tayi

sannan tace " to what time zakazo?   A tak'aice yace " nan da 4  insha Allah.

Ajiyar zuciya ta sauke a ranta tace "yauwa nasan haryazo ya tafi su ya Usman basu dawo ba, balle hakan ya zame mata matsala, tabbas tasan duk ranar da tayi sake  suka ganta tana hira da Maheer Ranar ta gama kad'ewa har ganyenta!  Amma kuma a fili setayi murmushi tace " to Allah ya kawoka lf..... "I cnt explaine how much i love you Queen, i really love you with all my heart  Umy. Don Allah karki zama silar kassara zuciyar da take a cikeda mayen k'aunarki Queen,  Maheer ya katseta cikin wata irin murya me d'aukeda tsantsar soyayyar gaskiya da kuma mayen ta.

Shiru tayi ta kasa cewa komai, sabida har ga Allah batajin zata iya yaudarar wani ma ballanta wanda takejin an halicceta ne domin shi, ita kanta batajin zata iya Rayuwa batareda shiba ballantana harta samu zarafin yaudararsa, wasu siraran hawayene suka fara yi mata zarya akan kuncinta, don haka ta kasa cewa komai ila wani irin bugawa da zuciyarta takeyi da k'arfi!!

Da wata irin murya Maheer ya kirata sunanta yace " Queen!!  *KIYARDA DANI* bazan tab'a cutarda zuciyarki ba, nayi alk'awarin cewar zan kula da dukkan damuwarki sannan zan soki a ko wani irin hali kika samu kanki, *KIYARDA DANI* ni Maheer zan zame miki bango da zaki jingina dashi har k'arshen Rayuwata!

Kasa jure sauraron irin kalaman dayake gaya mata tayi don haka ta ajiye kan wayar da sauri, lokaci guda kuma wani irin tausayin sa ya wanzu a birnin zuciyarta, fashewa tayi da wani irin kuka wanda babu komai a cikinsa face tsananin tsagwaron soyayyarta gareshi!

Shiru yayi yanabin wayar da kallo, ya jima a zaune sannan ya mik'e ya fad'a toilet, shower ya sakarwa kansa, ya jima ruwan yana zuba a tsakiyar kansa  sannan yayi wankan ya fito d'aure da babban towel a k'ugunsa hannunsa kuma bisa kansa yana goge lallausar sumarsa da wani k'aramin towel fari tass. Direct wajen dressing miror dinsa ya nufa, tsadadden man shafawarsa na *Companyn  OLAY* na maza, ya d'auka ya fara bin tattausar fatarsa da shi, seda ya shafe duk jikinsa sannan ya d'auki cumb ya fara gyara sumar dake kansa.

A hankali ya fara takawa cikin takunsa na isa da k'asaita harya kai bakin makekiyar Drowar dake manne a bangon d'akin, wata dakakkiyar giznah skey blue ya jawo se faman yarari take tana maiko, kaillo d'aya zakayi mata ka fahimci me tsada ce,  ma'ajiyar agogunan Rolex d'insa ya nufa ya bud'e ya zaro wanda yafi ko wanne tsada da kyau ya ajiyeshi gefen kayan daya fito dashi,

A gaggauce ya sanya kayan a jikinsa, sannan ya bud'e drower da yake sanya hulunansa  a ciki ya d'akko wata Royal blue din zanna bukar wadda aka tsaya sakarta se faman baza k'yali da walwali takeyi, a lokacin daya sanya hular a kansa seda na sake kallonsa tareda yaba tsarin halittar Maheer Nasir Lamid'o,   wani dakakken takalmi me d'anyatsa ya sanyawa a k'afarsa shima Royal blue, sosai yayiasifar kyau sekace wani ango, nanfa ya shiga fesa tsadaddun turarukansa masu masifar k'amshi sannan ya ajiye ya kwashi car keys d'insa da kuma

wayoyinsa ya fice daga d'akin.

A farfajiyar gidan ya hangi binta 'yar kwabo tana goge masa mota, inda Hajiya murja keta fama fa bawa filawa ruwa dukda irin kumburar da k'arfata tayi hakan beda su Victoria sun tausaya mata ba.  Tsaki yayi sannan ya shige cikin bak'ar Range Rover d'insa ya murza mata key ya nufi *Sushmer Hospital*, koda yaje Asbitin seda ya fara yin sallar la'asar sannan ya shiga ciki,  daga d'an nesa da d'akin Maheer ya tsaya yana kallon Dady wanda ke sanye cikin pink d'in uniform d'in Asbitin yana kallon, kallo d'aya zakayi masa ka fahimci baya cikin kwanciyar hankali da nutsuwar zuciya.

Ya jima a tsaye yana kallon mahaifin nasa zuciyarsa na harbawa sabida kewarsa, cikeda karayar zuciya ya juya yabar Asibitin sabida baze juri kallon Dadynsa a cikin Rashin kwanciyar Hankali ba!

Be dire a ko ina ba se *zone E Legislative Quaters,*  a bakin katafaren get din  gidansu ya tsaya tareda yin horne, cikin mintuna kad'an aka wangale masa get ya kunna kai zuwa cikin gidan, wajen da aka tanada don perking d'in motoci ya nufa ya parker sannan ya zaro wayarsa ya shiga kiranta don ya sanar da Uwar gaiyar zuwansa,  seda ya kirata kusan sau biyu sannan ta answer ya sanar da ita zuwansa, katse wayar tayi sannan tace"ganinan zuwa.

Bata wani jimaba ta fito, sanye take cikin wata bak'ar jallabiya k'irar *Companyn shahriyal Abaya* tayi Rolin da mayafi Royal bue wanda aka k'awatashi da stones masu haske daga k'asansa, sosai kayan suka karb'i jikinta sekace balarabiyar k'asar Misrah, a nitse take takowa cikin takunta me jan hankali wanda hakan yasa gabad'aya Maheer ya shagala da kallonta harta k'araso gabansa besani ba.

Zarazaran hannayenta tasaka ta rufe kyakkyawar fuskarta dasu, sannan Maheer ya samu nasarar dawowa daga duniyar begenta, nuni tayi masa da wasu kujerun Roba wanda aka sanya a ta bayan parking space d'in  kad'an,  zama yayi sannan ya kalleta yace "masha Allah, komai Queen d'ina ta saka kyau yake mata, da ace inada tukuicin dazan bayar gareki wllh dana baki a matsayin kyauta ta ta farko a gareki!

Kallonsa kawai takeyi sannan tace " ai tun a had'uwata dakai ta farko ka baki babbar kyautar da har duniya ta tashi bazan tab'a mantawa ba, don haka *KA YARDA DANI,* kai kanka kyautace ga Umaisa Mahmoud muham........ Kasa k'arasawa tayi sabida ganin irin kallonda Ya khabeer yake binta dashi, nanda nan k'irjinta ya buga da k'arfi sabida tsabar tashin hankalin datake ciki! Da k'yar ta iya had'a kallmomin da suka Rage mata tace " ya kha..kha..kah...khabeer!!!
_*🎀KIYARDA DANI...!🎀*_
🎀🐾🎀

*♝ IᗪTᏋllIǤᏋᗪT WrITᏋr'ی ASSω📚✍️*

*💫DEDICATED: to Sis naja'art*

_*WRITING BY: Zm (CHuBaDo)*_

*✨Special Gift for Hafsat Hafnan (my jika),.*

_Page:30_

___________📖Wata  irin mummunar fad'uwar gabace ta ziyarci zuciyar Umaisa, lokaci guda kuma ta mik'e tsaye tana k'ok'arin komawa bayan Maheer sabida yanda duk tabi ta Rud'e da ganin sa!

Kallon ta kawai khabeer yakeyi amma sabida tsabar tashin hankali yama kasa motsa koda yatsan hannunsa ballantana na k'afarsa, wani irin nauyi k'irjinsa yayi masa tamkar an d'ora masa  k'aton katafaren dutse a saman zuciyarsa, gabad'aya kansa ya gama kullewa sabida tsantsar tsagwaron tashin hankalin dayake ciki!  Yanzu yarinyar dayake kalo a matsayin duniyarsa gamida nutsuwar zuciyarsa itace yau take *_Exchanging Romantic love words_* da wani d'a namiji bashi ba?  Indai kuwa har Umaisa son Maheer takeyi Tabbas yana cikin gagarumin tashin hankalin da harshensa baze taba iya tattaro kalaman dazasu iya baiyanawa mekaratu shiba. Da k'yar ya iya d'aga k'afarsa ya nufi k'ofar shiga maine perlour d'in gidan,

Babu kowa a perlourn se Ummie wadda ke zaune tana kallon tashar Arewa24, ko sallama kasawa yayi sabida yanda jinsa da kuma ganinsa suke barazanar d'aukewa, had'a hanya kawai yakeyi inda ya d'ora hannunsa na dama a saitin zuciyarsa,  zuba Masa idanu Ummie tayi tana me karantar yanayinsa, sosai ta fahimci zallar tashin Hankalin dayake kan fuskarsa amma kuma ta dake batareda tace dashi k'alaba haryabar perlourn.

mik'ewa tayi kawai tabi bayansa don kawai ta tabbatar da abinda idanunta suka gane mata a tareda shi,  yana shiga part d'insa ko k'ofar be rufeba ya fad'a kan makeken Royal bed d'insa tareda zubawa saman d'akin idanu, k'ara danne saitin Zuciyarsa yayi, sabida wani irin harbawa dayaji tanayi masa, Rintse manyan Golden Eye d'insa yayi wa'yanda suka canza launi sabida Rad'ad'in da yakeji a zuciyar sa, a haka Ummie ta shigo ta sameshi,  sosai tashiga damuwa sabida tabbas tasan gudan jinin sa yana cikin tashin hankali dukda be gaya mata ba, haka kuma ba k'aramin abubane ze d'agawa Khabeer hankali harya bari wanima ya fahimci hakan,

*_hak'ik'a duk duniyar nan babu halittar data san ma'anar kalmar d'a sama da mahaifiya! haka kuma ita kad'aice take iya fahimtar damuwar d'anta koda ace be sanar da ita damuwar tasa ba!!_* , hannu tasa ta shafa gefan fuskarsa tareda zama a bakin Gadon, kasa magana tayi illah kallonsa kawai da takeyi, saukar hannunta dayaji akan fuskarsa ne yasa ya bud'e idanunsa ya saukesu akanta,  lokaci guda kuma ya mik'e ya Rungumeta k'am a k'irjinsa!  Kasa motsin kirki Ummie tayi sabida yanda take  juyo irin bugun da zuciyarsa keyi, lokaci guda jikinta yay masifar sanyi gamida fargabar abinda ke shirin faruwa dashi,  tabbas tasan halin khabeer yanada

masifar zurfin ciki shiyasa abune mayuyaci kasan damuwarsa.

Bubbuga bayansa ta dingayi alamar Rarrashi, lokaci guda kuma taji dumin saukar hawayensa a Gadon bayanta, cikeda tashin Hankali ta zaroshi daga jikinta tana kallon fuskarsa, tun kafin tayi magana yace "wllh ina sonta Ummie na!! I love her with all my heart, Ummie tun bansan meye so ba nake d'awainiya da dakon soyayyarta, tun tana k'arama Allah ya jarabceni da k'aunarta, hakanne ma yasa bantab'a sakewa da ko wace mace ba ballantana ma har naji ina sonta, Ummie hatta Beebah danak'i amincewa da Aurenta duk sabida itane nak'ita sabida banajin cewar zan iya had'a son danake mata da wata mace daban!

Amma Se gashi lokacinda takai minzalin daya kamata ta fahimci irin yanda nakeji akanta seta gaza yin hakan Ummie! Shikenan na Rasata a lokacin danafi kowa son kasancewa da ita!!!!!!

K'uri Ummie tayi masa tana kallonsa har ya rufe bakinsa, dafa kafad'unsa tayi sannan ta fara magana kamar haka " Khabeer dukda cewar bansan wace yarinya kakeso ba Amma hakan yasa naji a raina cewar bazaka Rasata ba, na tabbata Allah be d'ora maka sonta don ya hanaka ita ba, sabida ni kaina na yarda dacewar ba k'aramin so kake mata ba!

"Kasota tun tana 'yar k'arama batareda ka tab'a sanarda ko wani mahaluki ba kamar yanda kake sanar dani a yanzu, kaine ka fara sonta tun batasan kanta ba, haka kuma bazance maka kaine zaka Aureta ba, sabida al'amari na Aure wannan hurimi ne na Ubanji (S.w.t) a matsayina na mahaifiyarka ina me baka shawarar cewa ka mik'a dukkan lamarinka ga Allah Khabeer, na tabbata bazaka tab'a yin danasani ba insha Allahu, sannan nima kaina zan tayaka da addu'a idan yarinyar alkhairi ce a gareka Allah ya baka ita, idan kuma ba Alkhairi bace a gareka Allah ya baka wadda tafita Alkhairi!

Rungume Ummie ya sakeyi yana me zubda hawaye, tabbas abinda ta gaya masa gaskiya ne, haka kuma babu abinda ya gagari Ubangiji, sedai bayajin cewar ze iya cire soyayyar dayakeyi mata a ransa koda ace be sameta ba sedai ya mutu da soyayyarta a zuciyasa! Sabida sonda yake mata a jininsa yake, yariga ya gama ratsa duk wata gab'a da jijiyar jikinsa!

Dak'yar Ummie ta samu ya d'an Rage damuwarsa sannan ta fice daga d'akin, a ranta tana mamakin wace yarinyace haka wadda ta samu nasarar samun tsagwaron soyayyar gaskiyar Miskilin d'anta haka? koma wacece wannan yarinyar tabbas tayi babban dace data samu gwarzon namiji irin khabeer, wanda ya had'a duk wasu Qualites daya kamata d'a namiji ya kasance dasu. Tabbas bazata gusheba wajen rok'a masa Allah, har seya samu cikar burinsa da ikon Allah.

Bangaren Umaisa kuwa kuka ta fashe masa dashi wanda gaba d'aya ta kasa sanin dalilinsa, se'a yanzu take ganin wautarta da har ta bari zuciyarta ta rinjayeta ta gaiyato *_ZAB'IN RANTA_* cikin gidansu, da ace ta bari sun had'u a inda suka saba had'uwa wllh da duk hakan bata faru ba, shikenan yau ta shiga uku a hannun Ya Golden!

Shiru Maheer yayi yana kallonta batareda yace da ita k'ala ba, a tak'aice yace "Dr. Yayanki ne dama?   Yarfe hannu kawai takeyi tana kuka,  don hka Maheer ya gimtse fuska lokaci guda ya rikid'e mata ya koma mata ainihin Maheer Lamid'on data sani a baya, wanda murmushima aiki yake zame masa ballantana kuma magana, sannan ya kalleta yace " meye dangantakar datake tsakaninki da Dr. Khabeer mahmoud?

Da mamaki ta d'ago tana kallonsa tareda tsayarda zubar hawayen datake  sannan tace "he's my Brother, shine babban yayan mu ya Khabeer din danake yawan baka Ibrinsa.

Shiru yayi zuciyarsa na wani irin harbawa tareda tariyo masa irin kallon dayaga Khabeer din yana binta dashi d'azu,  kallo d'aya ya samu nasarar yiwa Khabeer d'in ya fahimci zallar soyayyar gaskiyar dake kwance a idanun Khabeer d'in gamida kishin ta, a nan ya fara kokonto akan maganar data dinga gaya masa kwanaki akan Khabeer d'in, cewar Khabeer yayanta ne amma kuma sam baya sake mata sosai, sedai dukda hakan baya iya jurar zubar hawayenta ballantana kuma damuwarta, koda ace baze rarrasheta ba sedai kawai ya tashi yabar mata gurin kokuma ya daka mata tsawa. Sedai dukda hakan tanason shi sosai haka kuma tana jidashi, bama shi lad'aiba kaf ahalinta zata iya sadaukar da komai sabida farin cikinsu.  Shin me hakan yake nufi *?*

Mik'ewa Maheer yayi sannan yace " its ok dear kukan ya isa haka, maza tashi ki shiga gida se munyi waya anjima ko?

D'aga masa kai kawai tayi sannan ta mik'e ta nufi hanyar dazata kaita kaita cikin gida,  shikuma maheer ya bita da kallo zuciyarsa na harbawa.

Tana shiga perlourn kasa tafiya d'akinta tayi sabida zarginta da zuciyarta takeyi, lokaci guda ta nufi hanyar side d'in ya Khabeer k'irjinta na dukan tara-tara dak'yar ta iya murd'a handile d'in k'ofar ta shiga da sallama, amma kuma babu kowa a perlourn don haka ta nufi k'ofar bedroom dinsa tana karanta duk addu'ar datazo bakinta,

Tana tura k'ofar ta bud'e don haka ta kunna kai zuwa ciki dukda irin bugun da zuciyar ta keyi mata,  a zaune ta sameshi ya dafe kansa da dukkan hannayensa tareda zubawa kapet din dake d'akin idanu, k'arar k'ofar ne yasa ya d'ago tsumammun Golden Eyes dinsa ya zuba mata yana kallonta!  Tun kafin yayi magana ta taho da gudu ta zube a gabansa, lokaci guda kuma ta fashe masa da kuka tace "don girman Allah ya Khabeer kayi hak'uri karka dake ni don Allah, wllh bazan sake ba, ni kaina bansan meyasa na gaiyatoshi ba!

K'uri Khabeer yayi mata yana kallonta, musamman ma yanda take magana cikeda k'uruciya a ciki gamida k'arfin gwiwa, kallo d'aya zakayi mata ka fahimci zallar gaskiyar abinda ke Ranta take fad'a. kamar daga sama taji ya cillo mata tambaya kamar haka " Kina sonshi kuma zaki iya Aurensa?

Zuba masa manyan fararan idanunta tayi cikeda zallar mamakin tambayar daya jefo mata

gamida nazarinta, tabbas tanajin Maheer a zuciyarta, haka kuma batajin zata iya b'oyewa kowa irin son da takeyi masa, don haka bakinta yana rawa tace "Ina sonshi yaya!  Kuma zan iya zama dashi a k'ark'ashin inuwa d'aya, badan komaiba se don irin sonda yakemin gamida nagartarsa, Pls kada kak'i fahimta ta, wllh har raina nakejin inayi masa wani irin so wanda ni kaina bansan adaddinsa ba balle na kwatantashi.

Wani irin bugawa k'irjin Khabeer yayi, lokaci guda kuma ya saki wani irin murmushi  wanda yafi kuka ciwo  sannan ya kalleta cikin ido yace " karki damu k'anwa ta, insha Allahu yayanki ze kasance a tare dake har zuwa ranar da zaki samu cikar burinki na auren wanda kike so kinji?

Wani irin tsalle ta daka ta fad'a jikinsa tareda k'ank'ameshi tana dariyar farin ciki,  zareta yayi daga jikinsa sannan yace "so nawa zan gargad'eki akan ki dena hugging dina kin girma?

Washe baki tayi sannan tace " im sorry yayana bazan k'ara ba, sannan ta fice daga d'akin zuciyarta fessss,

Ido ya zuba mata harta fice daga d'akin lokaci guda kuma ya dafe saitin zuciyarsa tareda lumshe tsimammun idanunsa tareda k'udurtawa kansa cewar " indai har sonda yake mata gaskiya ne dolene ya haqura da farin cikinsa don tabbatuwar nata farin cikin, haka kuma so tari a rayuwa abinda mukeso bashi yake zama alkhairi ga rayuwarmu ba, don Haka zeci gaba da addu'a akan Allah ya zab'amasa abinda yafi alkhairi a rayuwarsa, sedai abune mawuyaci ya ira raba zuciyarsa da soyayyar Umaisah!!!!
_*🎀KIYARDA DANI...!🎀*_
🎀🐾🎀

*♝IÐŦɇ[[IǤɇÐŦ WɍIŦɇɍ'ى  ASSɷ📚✍️*

*💫DEDICATED: to Sis naja'art*

_*WRITING BY: Zm (CHuBaDo)*_

*✨Special Gift for Hafsat Hafnan (my jika),.*

_Page:31_

*_Dis page is 4 you dear sis, Aisha musa Isah (Chubad'o)😁, kome Zm chubad'o  ta zama a sanadin potolo ne, domin kuwa itace silar kasancewa ta marubuciyar yanar Gizo, i really proud of you my darling❤_*

___________📖 8:30pm zaune suke bisa makeken daining table dinsu kamar yanda Ahalin gidan suka saba kasancewa kullum domin yin Diner, sedai wannan lokacin ya banbanta da sauran lokutan sab'anin na kullum,

Usman ne ya kalli Farouq yace "heyy lafiya kuwa banga Golden ba? Tab'e baki Farouq yayi sannan yace " nima tunda na dawo office nake nemansa na kira wayansa har kusan  2 times amma beyi piking ba,

Da mamaki Abba yake kallonsu sannan yace "amma kaidai Farouq anyi sakarai wllh, ace ka kira d'an uwanka har so biyu baka sameshi ba amma bakayi tunanin kace part dinsa ka duba lfyarsa ba?  Sosai kai Farouq yayi cikeda jin kunyar abinda yayi.

Ajiye cokalin hannunsa Abba yayi sannan ya mik'e ya nufi part d'in Khabeer, da sallama ya murd'a handile d'in k'ofar, yana kwance akan doguwar kujerar dake perlourn hannunsa a nad'e bisa k'irjinsa,  sanye yake da milk colour d'in jallabiya ta *COMPANYN EMRATY* sosai ta karb'i jikinsa dukda cewar bashida hasken Fata sosai kamar ta 'yan Uwansa, amma kallo d'aya zakayi masa ka fahimci fatar jikinsa a goge take irinta maza 'yan k'walisa kuma masujida kansu, har Abba ya zauna daga gefansa Amma sam Khabeer bema lura dashi ba ballantana  ma ya yaji motsinsa.

A nitse Abba ya maida kallonsa ga fuskar Khabeer d'in yana nazarinsa, sosai yaga fuskarsa tayi masa fayau duk yabi ya fad'a,  nan da nan hankalin Abba ya tashi lokaci guda kuma yakai hannunsa kan goshin Khabeer d'in,  sosai yaji jikin nasa da zafi sosai, don haka Abba ya shiga tashin sa, a hankali ya bud'e lumsassun idanunsa wa'yanda sukayi masa nauyi sabida tashin hankalin dayake ciki, hatta Abba seda ya tsorata da irin sauyin da idanun Khabeer d'in sukayi, cikeda damuwa Abba ya kalli Khabeer yace " ya salam!  Son meyake damunka haka?

Shiru Khabeer yayi yana kallon Abba wanda shima kallonsa yakeyi, ido cikin ido suke kallon juna lokaci guda kuma Khabeer ya maida idanunsa ya lumshesu,  jikin Abba ne ya k'ara sanyi don haka ya jawo Khabeer din zuwa jikinsa, lokaci guda kuma ya Rungumeshi  yana tambayarsa damuwarsa.

Shiru Khabeer yayi sabida harga Allah yana jin tsoron sanar daahaifin nasu damuwarsa, sabida harga Allah bemasan ta ina ze farayin hakan ba, sedai bashida wani zab'i wanda ya wuce ya sanar dashi gaskiyar abinda ke damun nasa!

Zare jikinsa yayi daga na Abba, sannan ya kama hannunsa ya rik'e cikin nasa wata nannauyar ajiyar zuciya ya sauke muryarsa na rawa ya kalli Abba yace " Abbana!! Bansan ta ina zan fara sanar dakai damuwata ba, amma zanyi k'ok'arin gaya maka  matsalata ta hanyar da zatafi min sauk'i wajen fahimtar dakai Abbah!

Sabida a duniyar nan gaba d'ayanta mutane biyu ne kad'ai suke iya samun kusanci da zuciyar mutum, sune iyayensa, Duk duniyar nan Kaikad'aine wanda ya kamata ya fahimci damuwata

Abbah Sabida banida wanda yafika a duniyarnan,  Abba ina sonta haka kuma banajin zan iya rayuwa da wata mace bayan ita,  Abba! Ya fad'a yana me dafe saitin zuciyarsa da hannunsa guda.

Murmushi Abba yayi sannan ya kalli Khabeer yace " Son   gaba d'aya maganar daka fad'a duka naji kuma na fahimta, kuma insha Allahu ni mahaifinka nayi maka alk'awarin cewar zanje har gidansu iyayen yarinyar innema maka Aurenta ko 'yar wacece ita, don haka ka sanar dani wacece yariyace wannan kuma 'yar waye a cikin garin nan?

Ido Khabeer ya bud'e yana kallon Abba sannan ya mayarda kallonsa ga k'asa yace " Abba Ba kowace yarinya bace illah *_UMAISA_*  wllh Abba ina son..... "Ka rufemin baki Khabeer!!!!! Abba ya katseshi cikin karaji da kuma tsantsar fishi gamida b'acin Rai yace " Ada inayi maka kallon mara hankali Ashema ka wuce hakan!

Ban tab'a zaton haka a tareda kai na khabeer, da alama notinan dake cikin kanka sun kwance, shiyasa harka iya kallon idanuna kake gayamin duk maganar datazo bakinka!!!  Wannan wace irin masiface haka? k'anwar taka kake gayamin kanaso Khabeer?  To wllh ka godewa Allah dayasa bana d'aya daga cikin iyayen da suke saurin yiwa yaransu baki, in badan hakan ba wllh dasena  na'ance ka khabeer!!!!! A fisace Abba ya fice daga perlourn yana huci.

A bakin k'ofar perlourn sukai kacibus da Mamie wadda ke tsaye tana sauraron duk maganar da suka tattaunawa, ko kallonta Abba beyi ba ya wuce yabarta tsaye a gurin.

Da k'yar ta iya d'aga k'afarta ta shiga d'akin, kallo d'aya tayi masa ta fahimci irin gagarumin tashin hankalin dayake ciki,  zama tayi akan kujerar dake kallon tasa, sannan tace " Babana kayi kuskure guda d'aya a raywarka, wanda zan iya fassarashi a matsayin wauta kokuma shirme, ita soyayya a kowani lokaci baiyanata akeyi ba b'oyeta ba, sabida zurfin ciki baya haifar da komai face cutuwa da kuma danasani kokuma ma ince zalintar kai. Wanda na tabbata da ace idonka be gane maka Umaisa da wani ba da bazaka tab'a fitoda abinda ke Ranka ba!  Don haka a matsayina na Uwa a gareka khabeer ina me baka tabbacin cewar insha Allah zanyi iya bakin k'ok'arin don ganin ka samu cikar burin ka.

A'a Mamie banaso ki tilasta mata ta soni, sabida kona aureta bazatayi min kallon masoyi ba sedai ta kalleni a matsayin mak'iyinta! wanda nikuma bazan tab'a iya jurar hakan ba! Har gara ajalina ya riskeni akan Qanwata tayi min kallon wanda ya rushe mata farin cikin Rayuwarta!!! Mamie idan har masoyi ya cika masoyin Qawarai to ze iya sadaukar da farin cikinsa domin farin cikin abin Qaunarsa, haka kuma Sadaukarwa tana d'aya daga ciki jigon soyayyar gaskiyah!!!!

Amma khabeer idan har zamuyi maka adalci ya kamata mu samamaka farin cikin Rayuwarka a matsayinmu na iyayenka "haka itama ya kamata kuyi mata adalci Mamie!. Khabeer ya katseta ta hanyar fad'ar hakan.

Murmushin k'arfin hali khabeer yayi sannan yace " Zan iya fassara son da nake mata a

matsayin jarrabawane ta ubangiji a gareni Mamie, Amma kuma banajin zan iya jurar gani zubar hawayenta komai QanQantarsu, ballantana kuma ace nine silar zubar su, nafiso Abarta ta Auri wanda takeso kuma ta rayu dashi cikin aminci, ta hakane kawai zan cika adalin masoyi a gareta idan har na sadaukar danawa farin cikin don tabbatuwar nata farin cikin.!!!!

Shiru Mamie tayi tana kallonsa a ranta tace "lallai khabeer yacika adalin Namiji, lallai masu iya magana sunyi gaskiya da sukace kyan d'a ya gaji Ubansa, tabbas a wannan rayuwar abune mawuyaci kasamu adalin masoyi kuma nagartacce a yanda son zuciyar mutane ya yawaita a wannan zamanin, kowa kansa kawai ya sani, baya tunanin kowa.

Hak'ik'a a Matsayin ta na mahaifiyar Umaisa tajiyewa d'iyarta takaicin Rasa nagartaccen mijin dayake mata sona gaskiya, mik'ewa tayi jikinta babu k'wari tabar d'akin, koda ta dawo perlourn kasa magana tayi sabida tsabar damuwar dake cinta a Ranta, kujerar data bari d'azu ta koma ta zauna, ko abincin ma kasaci tayi.

Usman ne ya kalleta yace " Mamie ya naganki haka?

Murmushin yak'e Mamie tayi tareda b'oye damuwata tace "wllh jikin Baban nawa ne danaje na gani duk senaji babu dad'i.

Zaro ido Usman yayi yace " Mamie wai kin manta Golden ne?  Nanda safiya zakiga ya ware kamar kowa, ni barima naje na dubashi,  tashi Farouq ma yayi sannan yace "Muje nima na dubosa tun kafin na sakeyin laifi a gurin Alhaji Abba. Dariya sukayi gaba d'aya sannan suka mik'e harda Rumana da Umaisa suka tafi d'akin khabeer d'in.

Duk hirar da sukeyi, Itadai Ummie kasa cewa komai tayi, haka kuma abincin ma ba wani cinsa takeyi ba sabida harga Allah ta gama tsorata da ganin yanayin Khabeer d'in.

Mamah ma tashi tayi ta marawa su  Usman baya zuwa d'akin khabeer d'in, ya kasance daga Ummie se Mamie,  kallon Mamie Ummie tayi sannan tace " wllh Badi'atou inajin tsoron ciwon nan na khabeer, kiduba fa ki ga yanda ya rame ciwon wuni da'aya sekace wanda ya shekara yana jinya, nasan khabeer sosai yanada masifar zurfin ciki, wllh da ace ya sanar dani yarinyar dayake so dani da kaina zan durk'usa har k'asa na Rok'eta ta soshi koda kad'anne!!!

K'irjin Mamie ne ya buga da k'arfi lokaci guda kuma wani irin gumi ya fara keto mata, hak'ik'a dolene tayi wani abu akan wannan babban al'amarin dayake shirin ruguza farin cikin Ahalin. Amma kuma a zahiri setace "Addu'a kawai ya kamata mu tayashi da ita, Allah ubangiji yayi musu zab'in alkhairi gaba d'aya,  a haka suka tashi zuciyar kowa a dagule.

*SUSHMER INTERNATIONAL HOSPITAL ABUJA,* su Baffa Gidad'o sun iso Abuja Ify, basu dire ko inaba se Asbitin, tun kafin su perker motar Abdul ya bud'e murfin motar, seda Baffa

umaru yayi masa jan ido sannan ya dakata, a nitse suka sakko daga motar tareda kunna kai zuwa cikin Asibitin, wata farar  Nas Abdul ya tambaya yace " don Allah inane femele sogical words din ku?

Nuna masa tayi sannan suka tafi, nan ma basu wani sha wahala ba suka samu d'akin da Dadyn yake kwance,  a nitse suka tura k'ofar glass d'in tareda sallama d'auke a bakunan su,  kamar daga sama Dady yaji muryoyin su lokaci guda kuma ya maida kallonsa garesu,

Da gudu Abdul ya k'arasa gareshi ya Ringumeshi k'am a jikinsa yana hawayen farin cikin ganin mahaifin nasa......

_*🎀KIYARDA DANI...!🎀*_
🎀🐾🎀

*♝ IDTԏƏl|lƓƏDT WrIԏƏr'ى ASSฌ📚✍️*

*💫DEDICATED: to Sis naja'art*

_*WRITING BY: Zm (CHuBaDo)*_

*✨Special Gift for Hafsat Hafnan (my jika),.*

_Page:32_

*_Dis page is 4 you My darling UMMU DILSHAD mallakinki ne kiyi yadda kikaso dashi wllh na baki shi kyauta😅, haqiqa Qimarki ta musammance a idon Chubad'o, haka kuma karamcinki gareni mai girma ne, sonso fisabilillah❤_*
___________📖 Sosai Dady yaji wani irin bak'on yanayi yana ratsa zuciyarsa wanda yafi kamada tsantsar tsagwaron  farin ciki,  hak'ik'a ada ya riga ya gama yanke k'auna da sake ganin danginsa ballantana kuma gudan jininsa,  a yanzu babu abinda yake murk'usa zuciyar Dady kamar abinda ya aikatawa gwarzon d'ansa Maheer!! Idan a kwai abinda yake d'aga masa a yanzu be wuce Rashin Maheer d'in a tareda shi ba, Tunda suka shigo d'akin Dady yake kukan farin cikin ganinsu gamida nadamar abinda ya dinga aikata musu a sanadin sakacin da yayi da addu'a, musamman ma Baffa Gidad'o wanda gabad'aya kunyar had'a ido  Dady yakeyi dashi, don haka cikin kuka Dady ya had'a gaba d'aya hannayensa guri guda yace "don girman Allah ku gafarceni ahalina! Akan abubuwan dana dinga aikata muku bisa Rashin sani, hak'ik'a na tabka kuskure mai girma na sakacin danayi wajen wasa da addu'o'in neman tsari, shiyasa ma har Murja da muk'arrabanta suka samu galaba a kaina irin haka!! Don haka ina Rok'on yafiya a gareku 'yan uwana, musamman ma kai Gidad'o...! Ya k'are maganar yana sharar hawaye

Murmushi sukayi gaba d'ayansu sannan Baffa Umaru ya kab'i maganar yace " hak'ik'a ka tafka

babban kuskure Lamid'o, wannan kuskuren daka aikata kuwa shine yin sakaci da ambaton Allah tareda wasa da addu'o'in neman tsari, da ace kayi Rik'o dasu wallahil'azeem da baka tsinci kanka a irin halinda kasamu kanka a ciki ba!  Amma babu komai dama komai muk'addarine daga Allah, haka kuma tun Ran gini Ran zane Allah ya rubuta faruwar hakan, sedai kawai a kiyayi gaba tareda Fatan Allah ya yafe mana gabad'yanmu.

Da Amin suka amsa gabad'aya, sannan Dady ya kallesu yace "Shin ya akai ma kukasan inda nake har kukazo gareni?

Shiru sukayi gabad'ayansu aka rasa wanda zece k'ala a gameda tambayar da Lamid'on yayi, Baffa Gidad'o ne ya dafa kafad'unsa sannan yace " mu kanmu mun samu labarin inda kake ba tareda zato ko tsammanin hakan ba a safiyar yau,  kuma mun samu labarin ne daga Bakin Maheer.

"Maheer!!!! Dady ya fad'a cikin karaji gamida tsantsar kad'uwa!

Ae Maheer!!!!

Wasu zafafan hawayene masu zafi suka fara zubowa Dady, lokaci guda kuma ya damk'o hannun Gidad'o yace " yanzu ina Maheer d'in yake? Don girman Allah ku kiraminshi innemi gafararsa, hak'ik'a ban cancanci yazo inda nake ba, tunda nida bakina na gaya masa cewar karya sake waiwayar inda nake a Rayuwa!!  Haka kuma na fad'amsa cewar na sallamawa duniya sh......... Numfashinsa ne yayi sama lokaci guda idanunsa sukayi sama.

K'arar na'urar dake nuna yanayin daidaituwar numfashin nasa ce ta tsaya chak,  da wani irin mugun sauri Baffa Umaru  ya danna na'urar kiran gaggawa. In a second  segasu Dr. Viru sun hallara a d'akin.

Su kansu seda suka firgida da ganin irin halinda Dady yake ciki, nan suka shiga bashi taimakon gaggawa,  sunsha wahala matik'a amma still ba wani canji da aka samu. Dole yasa suka yake shawarar kiran Dr. Khabeer.

Khabeer wanda ke kwance bisa makeken gadonsa a nan nad'e cikin  bargo Mamie tana ta fama dashi akan ya tashi yasha kunun tsamiyar data damamasa amma yak'i, a haka har Ummiensa ta shigo d'akin ta Samesu, murmushi Ummie tayi sannan ta kalli Mamie tace" hmm ai kinsaba tsayawa kina lallab'ashi akan abinci, shiyasa shikuma yake k'ara narkewa.

Dariya Mamie tayi sannan tace "ai Baban nawa d'an a lallab'a ne, don haka barni kawai dashi wannan al'amarin na Uba da 'ya ne.

Dariya Mamie tayi sannan ta zauna daga bakin gadon tana binsu da kallo,  seda Mamie tayi masa  da gaske sannan ya bud'e tsimammun idanunsa wa'yanda suka canza launi suka k'ankance sabida damuwa, yamutsa fuska yayi sannan ya karb'a ya d'an sha, yana cikin shan

kunun wayarsa dake gefan Mamie ta d'auki k'ara, inda sunan Dr. Viru ya fito Rad'a-Rad'a a kan screen din wayar, mik'a masa wayar Mamie tayi sannan ya amsa tareda kai wayar kunnensa.

Tun kafin yayi magana Dr. Viru ya sanar dashi abinda ke faruwa, da sauri khabeer ya mike ya d'auki keyn motarsa ya fara k'ok'arin fita, dakatar dashi sukayi tareda cilla masa tambayar ina zashi shida bayajin dadi?

A takaice yace " Mamie hospital zani, mara lafiyan dayake k'ark'ashin kulawata ne ciwonsa ya tashi, kuma wllh He is in cretical Conditon, shiyasa nakeso naje na taimaka masa da abinda Allah yayi min baiwa dashi, kasa magana sukayi gaba d'ayansu, a ransu suna mamakin Qarfin hali irin na khabeer din.

Yana fita yaji kansa ya fara juya masa, don haka dole ya kira Usman ya tuk'ashi zuwa Asbitin, A nan ma seda Usman d'in ya kamashi sannan ya iya takawa har zuwa cikin Asbitin,

Shi kansa Usman mamakin yayan nasa yakeyi, lallai wannan mutumin na musamman ne a gurin khabeer, tunda har ya iya tasoshi yana cikin halin jinya, a haka suka k'arasa bakin k'ofar d'akin da aka shiga da Dadyn,  tsayawa Usman yayi, don haka khabeer ya kalleshi yace "ka kaini ciki mana inyaso seka fito, haka kuwa akayi har ciki Usman ya kaishi, inda ya tarar dasu Dr. Viru sun kacame wajen ceto Rayuwar mutumin da bayama iya ma hango fuskarsa daga inda yake tsaye, haka kawai se Usman yaji cewar yana shi'awar ganin fuskar mutumin, a hankali ya dinga takawa harya samu nasarar yin arba da fuskar Dadyn, sosai yaji mutumin ya bashi tausayi haka kuma ya tsaya masa a Rai, da sauri ya juya ya fice daga d'akin a ransa kuma yana jinjinawa aikin su khabeer din. Lallai likitoci suna QoQari sosai, haka kuma babu me iya biyansu sai Allah (S.w.t).

Cikin ikon Allah kuwa khabeer ya samu nasarar shawo kan matsalar, dama ba wata babbar matsala bace bututun iskar Dadyn ne ya toshe sabida yanda ya matsawa kansa da yawan tunani da kuma damuwa, a haka suka turo gadon suka fito dashi zuwa d'aki na musamman,

Shiko Usman tunda ya fito daga d'akin yake kallonsu Baffa Gidad'o wa'yanda ke cikin tashin hankali sabida Rashin lfyar Dadyn, babban abinda yafi jan hankalin Usman zuwa garesu shine Abdul, sosai yaji tausayinsa haka kuma seya samu kansa dajin zafin hawayen da Abdul d'in yake Zubarwa, haka kawai seyaji bayason ganin kukansa ko kad'an.

A hankali ya Qarasa gareshi tareda dafa kafad'un Abdul d'in, nan Abdul ya dago idanunsu ya sark'e cikin na juna!!

Tofa babbar maganar!
_*🎀KIYARDA DANI...!🎀*_
🎀🐾🎀

*♝ IDTɵ||IƓɵDT WrITɵr'ی ASSѻ📚✍️*

*💫DEDICATED: to Sis naja'art*

_*WRITING BY: Zm (CHuBaDo)*_

*✨Special Gift for Hafsat Hafnan (my jika),.*

_Page:33_

___________📖Kallon juna sukayi kusan kimanin 5scond sannan, Abdul yace "kamar nasan fuskar nan? d'auke hannunsa Usman yayu daga kafad'ar Abdul d'in sannan  yace "a kwai yuwuwar hakan amma abune mawuyaci nafi tunanin kamace kawai, any way i'm Usman mahmoud muhammad, ni Qanin Dr. Khabeer mahmoud ne wanda ke kula da Rashin lafiyar mahaifin ka, hannu Abdul ya mik'a masa yace" nikuma Abdussalam Nasir Lamid'o, murmushi Usman yayi wanda ya baiyana fararan haqoransa yace "Nice to meet you Abdussalam, "mee too Abdul ya fad'a shima yana murmushi, se'a lokacin Usman ya gaidasu Baffa Gidad'o tareda tambayarsu ya mai jiki, da kulawa suka amsa masa a haka har wata nurse tazo ta samesu inda take sanar dasu cewar zasu iya shiga su duba mara lafiyan, na musu suka nufi d'akin inda shikuma Usman ya nufi office d'in ya khabeer donya d'aukeshi su koma gida,

A nan ya samu Dr. Abdullah se faman masifa yakewa khabeer d'in sabida yanda yake Qoqarin kashe kansa akan abinda shiyafi cancanta daya sameshi, ganin Usman ne yasa Dr. Abdullah ya rage fad'an dayake masa tareda tsira masa al'urar dake hannunsa, had'e rai khabeer yayi sosai sabida bayaso Usman ya samu damar yi masa wata tambaya, sabida be shirya amsa masa ko wace tambaya ba a halin yanzu, magunguna Dr. Ya mik'awa Usman yace " ka tabbatar kullum yasha su akan lokacinsu, sannan ya maida kallonsa ga khabeer d'in yace "duk wasu magani dazan baka da wasu dokoki dazan fad'a maka duk kasansu Golden, tunda you are a Doctor, idan har baka kwantar da hankalinka ka Rage yawan tunani ba babu abinda maganin nan ze maka, gobe da safe zanzo har gida naga jikin naka. Yana kaiwa nan ya mik'e yabar office d'in Ransa a b'ace.

Wani irin Kallo Usman kebin khabeer dashi wanda yafi kamada na tuhuma yace " amma ya Golden senake ganin kamar be kamata ka....... "Kaga malam banason yawan surutu ka gane ko?

Shiru yayi yana kallonsa sannan ya kamashi sukabar office d'in suka fita daga cikin Asbitin, a ran Usman yana mamakin Hali irin na yayan nasa, abu d'aya ya qudurtawa zuciyarsa shine seya binkito abinda  ya Golden d'in ke boyewa wanda bayaso ya sani.

B'angaren Maheer kuwa sosai ya rasa kwanciyar hankali sabida tsoron Abinda zeje ya dawo a tsakaninsa  da yarinyar dayake da tabbacin cewar tariga ta zama jini da tsokar dake yawo a

cikin gangar jikinsa, tabbas ita kad'aice mahad'in kwanciyar hankalinsa da salamar Ruhinsa, bayajin ze iya jurar Rashin ta koda na k'ank'anin lokaci ne a rayuwarsa, babban abinda ke tayar masa da hankali a yanzu guda d'aya ne shine Dr.khabeer! Tun ranar daya kalli Qwayar idanunsa yaga daskararriyar soyayyar dayakeyiwa Queen d'insa ya kasa kwanciyar hankali, dukda cewar shine  *ZAB'IN RANTA* ba khabeer din ba!

Wayarsa ya lalubo ya danna number d'inta, kwance take bisa kafet din dake d'akin tayi shiru, gaba d'aya kewarsa duk tab'i ta takura mata, dik wani bugu na zuciyarta yana bugawane da soyayyar maheer dinta!!. Qarar tellphone dince ta katseta wanda ko ba'a fad'a mata ba tasan Maheer ne, da sauri ta mik'e ta nufi gurin zuciyarta fal farin ciki ta d'auka ta kara a kunnenta tareda yin sallama, lokaci guda suka saki ajiyar zuciya ita dashi, wadda take baiyana tsantsar kewar junan da sukayi!!!.

Wani irin lumshe idanu maher yayi sabida jin muryarta da yayi, hka kawai yakejin wani irin baqon al'amari a tattareda yarinyar, musamman ma idan yana kallonta kokuma yanajin muryarta, Allah ne kad'ai yasan irin yanayin da zuciyarsa take shiga a kanta, wani irin so yake mata wanda baze iya misaltawa irinsa ba. Da wata irin kasalalliyar murya yace "i miss you Queen, dariya tayi har yana iya jiyo sautin dariyar yace " dariya ma kikemin ko? To tunda ke bakya missing d'ina barina kashe wayana kawai....... Da sauri tace "i miss you too Jan!

Dariyar shima yayi sannan suka afka Duniyar hira, sun jima suna waya sannan sukayi sallama da juna,  wasa-wasa kullum Qara shaquwa suke da juna tamkar ana Qara izamusu wutar Qaunar dake tsakaninsu. Ita kanta har mamakin kanta takeyi idan tana wani abun akan Maheer, sam bata iya b'oye irin son da takeyi masa, Ameerah ce ta shigo d'akin da sallama tareda kallon kallon yayar tata tace " ya Umaisa Mamie is calling you, she say data kuma kiyi shauli kizo. Tana kaiwa nan ta juya harda d'an gudunta tabar d'akin

A nitse ta mik'e cikin nutsuwa, sannan ta nufi d'akin Mamie, a hankali take taka step din tamkar wata k'asaitacciyar sarauniya harta kai k'ofar d'akin ta murd'a tareda kunna kai ciki had'e da sallama, a zaune ta samu Mamie bisa d'aya daga cikin luntsuma-luntsuman kujerun dake perlourn nata,

Zama tayi daga gefan Mamien tareda fad'in "Mamie gani.

Kallonta Mamie tayi kimanin daqiqu biyar sannan tace " Umaisa a matsayina na mahaifiyarki ina so ki sanar dani meye a tsakaninki da wannan matashin yaron wanda yazo gurinki shekaran jiya?

Qirjinta ne ya buga da Qarfi lokaci guda kuma wata irin zufa ta fara keto mata dukda uban sanyin Ac dake perlourn,  inda-inda ta farayi tana sosa gefan kanta sabida yanda duk tabi ta rude da tambayar da Mamie tayi mata.

Kallon tsaf Mamie tayi mata sannan tace " haryanzu ke yarinya ce Umaisa, ni uwace bazan

tab'a tauyeki ba, tunda kema kinada haqqi akaina, nayi mamaki k'warai da baquwar d'abi'ar da kika shigo da ita cikin Rayuwarki Umaisa, ada komai naki bakya iya boye min shi amma se gashi dayake al'amari ne na soyayyah bakiyi shawara da kowaba kika jefa kanki cikinsa, kinsan al'amarin d'a namiji kuwa Umaisa?

Kuka ta fashewa Mamie dashi har da shashsheqa, cikeda karayar zuciya tace " iya dnt know why i love him Mamie, ni kaina bansan meyasa harna amince dashi irin haka ba Mamie, wllh koke kika ganshi zaki yaba da halayansa da kuma d'abi'unsa, komai nasa a tsari yakeyinsa, he is very friendly and social Mamie, bayan kasancewarsa  genues bravo...... Keep Quite idiont, i'm i your mate, don ubanki zaki tsaya kina expresing how you fill akan wani wani banza can?

Tashi ki fice min daga d'aki tun kafin kija abinda zan nakaita ki akansa, in banda lalacewar zamani har ke zaki iya kallon Qwayar idona kina gayamin irin wa'yannan banzayen maganganun?

Ina kunyarki da tarbiyar da muka baki Umaisa?

Wani tuquqin baqin ciki ne ya tasowa Mamie, sabida baqin ciki jitake kamar zuciyarta zata fasa qirjinta ta fito, miqewa Umaisa tayi da mugun sauri tabar d'akin tana kuka,

Dafe kanta Mamie tayi a ranta ta qudurtawa kanta cewar koda Umaisa zata mutu seta Auri khabeer sabida shine zabinta ba wani sakarai can ba.!

_*🎀KIYARDA DANI...!🎀*_
🎀🐾🎀

*♝ IŊƬɘ||IƓɘŊƬ WɼIƬɘɼ'ی ASSωɑ📚✍️*

*💫DEDICATED: to Sis naja'art*

_*WRITING BY: Zm (CHuBaDo)*_

*✨Special Gift for Hafsat Hafnan (my jika),.*

_Page:34_

*_Al'umar musulmi muji tsoron Allah mu muƙa dukkan lamuran mu ga Allah, wannan jarrabawar da muke fama da ita na curona-virus Allah ubangiji ka kawo mana sauƙinka da agajinka, ya ubangiji Allah ka yafe mana laifukanmu badan halayenmu ba!😭🤲_*
___________📖 Fita tayi daga ɗakin tana wani irin kuka wanda yake baiyanar tsantsar damuwar datake ciki, a perlourn ƙasa sukai kaciɓus da Ruman tana ƙoƙarin hawa steps ɗin,

kallonta kawai Ruman takeyi a ranta tana jinjina dalilin kukan ƙanwar tata, wuceta Umaisa tayi da sauri tareda toshe bakinta da hannayenta.

yanda take kuka kad'ai zaka kalla kasan tana cikin tashin hankali kamar wadda ake zare ma rai, a haka ta koma d'aki tana gurzan kuka, Abinne ya d'aurewa Rumana kai, sabida ganin irin kukan da Umaisa keyi yasa tabi bayanta da sauri, tana shiga d'akin ta zube a K'asan Capet din d'akin ta sake fashewa da kuka.

A haka Rumana ta shigo ta sameta, a nitse ta dafa kafad'unta zuciyarta aatik'ar dagule sannan tace " meyake damunki ne haka? Zuwa yanzufa ya kamata ace kin dena irin wayan nan banzayen koke-koken naki, ya kamata fa ki fahimci cewar kefa ba yarinya bace Umaisa.

Dagowa tayi da jajayen idanunta wayanda suka canza launi sabida kuka tace "Rumana shin laifine dan naso mutumin daya nunamin k'auna da dukkan kulawarsa gareni? Maheer ya soni a lokacin da shi kansa besan menene so ba, haka kuma ya soni a lokacin da betab'a mafarkin hakan ba, wllh Ruman bazan tab'a iya son wani d'a namiji a rayuwata kamarsa ba, wani irin so nake masa wanda ban tab'a jin kwatankwacin irinsa a tareda kowa ba!

Amma se gashi Mamie ta kasa fahimtar hakan, batareda tunanin irin halinda zan shigaba amma Mamie take ƙoƙarin Rabani dashi, nikuma wllh indai akan rabuwa da Maheer ne sedai in rasa rayuwa........ "Anya kinada hankali kuwa Umaisa? Rumana ta katse ta cikin wani irin yanayi.

Kafeta Ruman tayi da manyan idanunta sannan taci gaba da cewa " Umaisa karki bari giyar soyayyah gamida mayentasu rufe miki idanu ki bijirewa umarnin Mahaifiyarki!!, shi namiji da kike ganinsa ba abin yarda bane balle har a saki jiki dashi, a matsayina na 'yar uwarki ina me baki shawara kan cewar ki mik'a dukkan lamarinki ga Allah sannan kuma kiyiwa Mamie biyayya akan dukkan abinda ta umarceki, sabida su iyaye da kike ganinsu wllh basuda mahadi balle aja dasu, bijire musu daidai yake da janyo fishin Allah (S.W.T).

Rungume ta Umaisa tayi tareda fashewa da wani sabon kukan, dak'yar Rumana ta samu nasarar Rarrashinta, tareda gaya mata tausasan kalaman da zasu rissinar da zuciyarta, sannan ta samu Umaisan tayi shiru,

sedai dukda hakan ita kadai tasan irin Rad'ad'in da zuciyarta take ciki, haka kuma batajin zata iya Rabuwa da Maheer ɗinta, jira kawai takeyi Abbanta ya dawo ta sanar dashi damuwarta, shikadaine wanda tasan ze goya mata baya kuma ya barta ta Auri *ZAB'IN RANTA.!*

Yau sab'anin kullum Abba be samu nasarar dawowa gida ba har wajen 9:00pm, wannan dalilin ne yasa Umaisa ta yanke shawarar taje ta sanar da ya khabeer abinda Mamie take shirin aikata mata, tun daga d'akinta take ta sharar k'walla harta kai part din Khabeer d'in, a hankali ta tura k'ofar ko sallama batayi ba sabida tashin hankalin datake ciki.

Kwance yake bisa makeken Royal bed d'insa, inda Dr. Abdullah yake k'ok'arin gyara masa

zaman igiyar drip din dake ɗaure a tsintsiyar hannanunsa, seda ya gama tsaf sannan ya koma gefe ya zauna yana kallon Khabeer din ransa a matiqar b'ace yace" wllh kaji kunya kaidai, akan yarinya Qarama kake qoqarin halaka kanka a banza, har zuwa wani lokaci zaka d'auka kana boye mata abinda yake Ranka?

Kaga malam Lokaci yayi daya kamata ka bude mata sirrin dake zuciyarka ko ka samu kwanciyar hankali da nutsuwar zuciya, kaduba fa kaga irin condition din da kake ciki Khabeer!!! A halin yanzufa Zuciyarka ta fara kumbura sabida damuwar da kake yawan addabar kanka dashi, idan har bazaka iya sanar da itaba ninan zan sanar da ita sirrin Zuciyarka, *_KAYARDA DANI  Abokina.!!!_*

Lumshe tsumammun idanunsa yayi a hankali, lokaci guda kuma ya budesu tar akan Abdullah yace "wai sonawa zan fad'a maka cewar na haqura da ita ne?

"Ka dakata da wannan maganar banzar da kakeyi malam!  Abdullah ya dakatar dashi a fisace, idan harka haqura da ita meyasa har yanzu ka kasa gogeta daga Zuciyarka?

"Sabida haka Allah ya ƙaddara min Abdullah! Khabeer ya katseshi ta hanyar fad'ar hakan.

Abdullah yanashirn yin magana Umaisa ta shigo d'akin. kai tsaye gun Khabeer ta nufa batareda ta lura da drip din dake sak'ale a hannunsa ba ta wani fad'a jikinsa tareda sakin wanu irin kuka, sabida tsabar kukan da takeyi bakinta har Rawa yakeyi, dakyar ya iya tattaro ragowar qarfin daya yage masa ya dagata daga jikinsa,  lokaci guda yaji zuciyarsa nayi masa wani irin zafi, sabida yanda yakejin kukan nata yana wani irin narka masa zuciya, Allah shikaɗai yasan irin son da yakewa yarinyar!   Daƙyar ya iya buɗe bakinsa  ya fara tambayar ta dalilin kukan nata.

bata ɓoye masa komaiba ta warware masa dukkan abinda mamie ta gaya mata, a ƙarshe ta ƙare maganar da cewa "wllh ya khabeer i love him so much, and i cnt live without him!!!

Ƙuri yayi mata tamkar wani sakarai, haka kuma ya kasa koda motsin kirki ballema ya iya cewa komai, babu abinda yafi ɗaga masa hankali kamar kalmarta na ƙarshe!!!!

wata uwar harara Dr. Abdullah ya wurga musu dagashi har ita, sabida takaicin abokin nasa ji yake kamar ya shaƙeshi koya samu sassauci a zuciyarsa.

Miƙewa khabeer yayi daƙyar Cikeds ƙarfinhali tareda kama hannunta, jajayen idanunta ta ɗago tana kallonsa cikeda son jin inda zasuje, murmushin ƙarfin hali ya sakar mata sannan yace "kiyarda dani  gurin mamie zamuje muyi magana akan wanda kikeso ɗin, i'm sure mamie zata Barki ki Auri wanda kike so dear!

miƙewa tayi da sauri shikuma yana riƙeda hannunta, suna shirin fita daga ɗakin Abdullah ya katsesu ta hanyar cewa "Stop deceiving your self khabeer!!  Harzuwa yaushe zaka kai kana

azabtar da Rayuwarka akan wannan yarinyar, you should tell her how you fill about yanda kakeji akan sonda kake mata, lokaci yayi dazaka sanar da ita cewar she's the only yarinyar da kajeji a ranka sama da kowace budurwa a duniya. Amma sabida cutarkai kaƙi ka sanar da ita , wannan abinda kakeyi ba sadaukarwa bace shirmene kawai Khabeerrr!

tunda ya fara magana Umaisa take kallon Dr. Abdullah, gaba ɗaya jinsa kawai takeyi tamkar wata zararriya, gaba ɗaya jin sautin maganarsa takeyi tamkar saukar aradu, inda wani ɓangaren na zuciyarta takeyi masa kallon taɓaɓɓe, a saluɓe ta mayar da kallonta ga khabeer wanda gabaɗaya yabi ya wani daskare tamkar an dasashi,  daga irin kallon dayake mata ta fahimci cewar maganar Dr. Abdullah gaskiya ce, wani irin bugawa ƙirjinta yayi, don haka ta fara jada baya tana  zubarda hawaye, da sauri khabeer ya fara yun ƙurin binta,  da wani irin mugun sauri ta juya tabar ɗakin su kuma duka mara mata baya.

_*🎀KIYARDA DANI...!🎀*_
🎀🐾🎀

*♝IᗪTЄ||IƓЄᗪT WrITЄr'ى  ASSѡ📚✍️*

*💫DEDICATED: to Sis naja'art*

_*WRITING BY: Zm (CHuBaƊo)*_

*✨Special Gift for Hafsat Hafnan (my jika),.*

_Page:35_

___________📖binta yakeyi da dukkan sauran ƙarfin daya rage masa, amma sam ya kasa cimmata, bata tsaya a ko ina ba se'a babban perlourn gidan sakamakon ganin Ummie datayi a daining aria ɗin, da wani mugun sauri ta faɗa jikin Ummie ta ƙanƙameta, gaba ɗaya duk tabi ta birkice sekace wata zararriya,  rikicewa Ummie tayi sabida yanda taga umaisan nayi kamar wata taɓaɓɓiya, jijjigata kawai takeyi tareda jera mata tambayoyi, a haka khabeer da Abdullah suka ƙaraso perlourn.

Fisge jikinta Umaisa tayi daga riƙon da Ummie tayi mata, lokaci guda kuma ta tawani koma bayan ummie ta tsaya tareda fashewa da kuka tace "wllh Ummie ya khabeer ya haukace, wllh ummie baya cikin hankalinsa, cewafa yakeyi wai yana sona kuma wai aurena yake sonyi!  Wllh ummie karki saurareshi kawai ki kira Abba akaishi Asibiti.

A hankali  khabeer ya far takowa zuwa inda Ummie ke tsaye,  wata uwar ƙara Umaisa ta ƙwala wadda seda gidan ya amsa gaba ɗaya, tareda ƙanƙame ummi tana faɗin "tell him karya mato inda muke wllh Ummie ya khabeer baya cikin haiyacinsa, ta faɗa tana wani irin kuka kamar

Ranta ze fita daga jikin ta,

Ihun data kurma ne yasa mutanan gidan gaba ɗaya suka hallara a perlourn, ciki kuwa harda Baban Gano, kallonta kawai mutanan dake perlourn sukeyi, haka kuma sunyi tsit bakajin komai se sautin kukan umaisa, hakanne yayi daidai da shigowar Abba perlourn tareda Usman.

Da wani irin gudu ta ƙara inda Abba ke tsaye tareda faɗawa jikinsa ta saki wani irin kuka tana nuna masa khabeer wanda ke dafe da kansa sabida tsabar tashin hankali take faɗin "Don Allah Abba ka taimakeni mukai ya khabeer Asbiti wllh abba ya haukace, bakaji irin maganganun dayake faɗamin ba Abbah, cewafa yakeyi wai ni yakeso ya aura!

Wata irin uwar zuface ta shiga ketowa Abba, lokaci guda kuma yanayinsa yay masifar sauyawa sabida ɓacin rai, a nitse ya zarota daga jikinsa yayi gefe da ita, lokaci guda kuma ya maida kallonsa ga khabeer, wani irin tuƙuƙin baƙinciki ne yake taso masa daga zuciyarsa, cikin wani irin karaji da rawar jiki ya ƙarasa inda khabeer yake tsaye, wani irin gigitaccen mari Abba ya ɗauke khabeer ɗashi, ji kake tasss!...tass!!...tasss!!!.

A kausashe ya nunashi da yatsansa yace "khabeer ada inayi maka kallon shasha-sha, Ashema kafi wuce haka, sonawa zan sanar dakai cewar wannan hanyar daka biyo bame ɓillewa bace?

Taya kake tsammanin zan iya baka Auren ɗiyata ta cikina?

Shin bakasan cewa ƙanwarka bace babu Aure a tsakaninku kai da ita ba?

"harzuwa yaushe zakaci gaba da ɓoye wannan sirrin Alhaji mahmoud.! Mamie ta katseshi cikin wani irin karaji me ɗaukeda Amo a cikinsa, lokaci guda kuma wasu irin hawaye masu masifar zafi suka shiga bin kumatunta, wanda hakan ya sanya kowani halitta dake cikin perlourn kansu yay masifar ɗaurewa, musamman ma Baba da Ummie da kuma Ummah. Farouq da Usman da Rumana kuwa kasa motsin kirki sukayi sabida tsabar mamakin irin almarar dake shirin faruwa a zuriyar tasu gabaɗaya.

"Ki rufe min baki Badi'atou, Abba ya katseta fisace cikin ɗaga murya..!

Girgiza kai Mamie tayi tana kuka Lokaci guda kuma ta zube a ƙasan capet ɗin dake perlourn tace "kayi haƙuri Alhaji amma a irin karamcin da zuriyarka dakai kanka kayimin banajin zan iya cigaba da ɓoye musu wannan sirrin, koda kuwa hakan ze zama silar mutuwar aurena dakai!!

yana shirin yin magana Baba ta katseshi ta hanyar ɗaga masa hannu tace "mamuda, idan har ka ɗaukeni a matsayin uwar data haifeka to ina me baka umarnin cewar karka kuskura ka hanata baiyana wannan sirrin da kuka ɓoye kaida ita!

wannan maganar ce tasa dole Abba ya nemi guri ya zauna a ɗaya daga cikin kujererun perlourn, wata irin zuface take keto ma Abba duk irin sanyin Ac dake tashi a perlourn, dole gaba

ɗaya ahalin suma suka nemi guri suka zauna, sannan Mamie ta maida idanunta ƙasa tana sharar hawaye ta fara magana ksmar  haka.

*_LABARIN AINIHIN ABIDA KE FARUWA SHINE_*

Asalina ni haifaffiyar garin Adamawa tantagaryar  cikin mabilwa, mahaifina malamin makarantar Alo ne, nikaɗai Allah ya bashi a tsayin ƴa, haka kuma ya bani kulawa sosai a cikin Rayuwata, ina ƴar shekara goma kacal a duniya Allah yayiwa mahaifiyata Rasuwa,  wannan mutuwar ta girgiza mahaifina sosai haka nima,  tundaga loƙacin Babana ya ninka kulawar dayake bani fiyeda wadda yake bani kafin mahaifiyata ta rasu.

bayan wani lokaci me tsaho babana ya sakeyin Aure badon radin kansa ba sabida matsin dayake samu daga mahaifiyarsa wato kakata,  tunda babana yayi Aure kwanciyar hankalina ya ragu, duk wata kulawa danake samu daga babana nazo na dena samunta, hasalima kafin mu haɗu dashi aiki ne,

tundaga lokacin rayuwata ta koma tamkar ta baiwa mara ƴanci ko tausayina mahaifina bayayi, wasu lokutan ma a gabansa Adda Dije take dukana tana azabtarwa, amma kuma baya iya hanata. Kwatsam wata ranar juma'a Babana ya shigoda ɗaurin goro da alewa, a nan yake sanar dani cewar ya bada Aurena ga wani almajirinsa, a ranar nayi kuka kamar Raina ze fita,

Adda Dije kuwa ranar kamar ta zuba ruwa a ƙasa tasha sabida murna, a ranar babana ya kaini ɗakin mijina, sannan yayi min nasiha sosai tareda gargaɗina kan cewar muddin na kashe aurena karna kuskura na dawo masa gida, a haka muka rabu da babana ya koma gida nikuma ya barni a gidana,

A lokacin danayi arba da mijin da Babana ya Auramin na girgiza sosai, sabida ganin tsarin halittar da Allah yayi masa, bugu da ƙari gashi ɗan gata a sosai,  ko kaɗan ɓe ƙyamaceni ba ya nuna min soyayya da kulawa ta yanda ma bakina baze taɓa iya misaltashi ba. A haka muka cigaba da Rayuwa dashi cikin Aminci da kuma ƙaunar juna, se'a lokacin na fahimci cewar gata mahaifina yayi min daya Aura min Bawuro.

Kwatsam Ranar
28/12/1997 a  wata Alhamis wadda bazan taɓa mantawa da ita ba a rayuwata, Bawuro yayi tafiya zuwa wani gari wanda be sanar dani ba, seda ya ƙwashe sati biyu sannan  ya dawo, ni kuma ina ɗauke da tsohon ciki, a wannan ranar  Bawuro ya sakeni saki 1 sannan ya Umarceni dana bar masa gidansa a daren baya son ganina.  A ranar kasa kuka nayi sabida tashin hankali, musamman ma dana tunada maganar mahaifina ta ƙarshe.

wannan dalilin ne yasa na yanke shawarar nayi nisa da garin Adamawa kozan samu kwanciyar hankalin da bansan ɗanɗanonsa ba.  Wannan tafiyar danayi itace ta tazama silar canzawar akalar Rayuwata harna samu damar shigowa cikin Ahalin na Alhaji Mahmoud muhammad.

Ina cikin tafiya a daren naƙuda ta kamani a kan hanyata ta zuwa jumeta, a nan ne muka haɗu da mahmoud, ganin dayayi zan iya rasa rayuwata ne yasa ya ɗaukeni yasa a motarsa, be dire ko ina dani ba se a wani babban asibiti dake cikin jumeta, ban wani sha wahalaba Allah ya saukeni Ify na haifi ɗiya mace, seda na kwashe kwana 7a Asbiti sannan aka sallameni, dukda hakan mahmoud betaɓa gazawa dani ba hakama abinda na haifa, bayan ya kaini gidansa ne ya raɗawa yarinyar suna Fatimah yakeyi mata laƙabi da Umaisa.

Duk wata ɗawainiya da gata wanda ɗa ya kamata ya samu daga gurin ubansa to umaisa ta samu a gurin Alhaji mahmoud, bayan nayi arba'in ne ya nuna yana son Aurena, batareda tunanin komai ba na amince na Aureshi,

Bayan ya kamala aikin daya kaishi yola ya ɗaukoni ɓe dire a ko ina dani ba se garin gano, a nan ya gabatar dani ga mahaifiyarsa wato Baba, a matsayin matar daya aura batareda sanita ba, Mamie ta faɗa yayin da take kallon baba da jajayen idanunta waƴanda suka rine sabida kukan data gurza, shiru baba tayi tana kallonta sannan mamie ta cigaba da cewa "bamusha wahala wajen shawo kan Baba ba musamman ma dataji anyi mata takwara, kwanan mu biyu a Gano muka dawo abuja, kuma baku nuna ƙyama a gareni ba kasancewar Alhaji yafi ƙarfin gidansa, wannan shine ainihin gaskiyar labarin da muka daɗe muna ɓoyewa nidashi, amma magana ta gaskiya itace akwai Aurataiya a tsakanin khabeer da kuma Umaisa.! Ta ƙare maganar tana wani irin kuka me ban tausayi.

_*🎀KIYARDA DANI...!🎀*_
🎀🐾🎀

*♝ IÐTɵ[[IƓɵÐT WrIТɵr'ى ASSꙍ📚✍️*

*💫DEDICATED: to Sis naja'art*

_*WRITING BY: Zm (CHuBaƊo)*_

*✨Special Gift for Hafsat Hafnan (my jika),.*

_Page:36_

___________📖 gabaɗaya ahalin babu wanda be girgiza ba dajin wannan batu, Usman da Frouq kuwa daskarewa sukai a zaune saɓanin khabeer dayasan komai, shiru perlourn ya ɗauka na ɗan wani lokaci sannan Baban Gano ta fara magana kamar haka "haƙiƙa Allah mai hikima ne akan dukkan lamarinsa, duba da irin abubuwan da suka faru a tsakanin Mahmuda da kuma Badi'atou, dukkan wani me hankali da tunani dolene ya fahimci cewar akwai abinda Allah ya ɓoye a cikin wannan babban al'amari wanda na tabbata badan soyayya ta bijiro a tsakanin

kabiru da Fatsima ba da wannan sirrin be baiyana ba.

Don haka babu abinda zamuce sedai muyi godiya ga Allah dayasa hakan ta kasance  da wuri, duk wannan abinda sukeyi Umaisa bama ta iya jin abinda Baban take faɗa tunda taji cewar ba Abba bane mahaifinta, gaba ɗaya tama kasan kukan sabida tsabar tashin hankalin datake ciki, babu abinda bakinta yake faɗa se "innanillahiwa'inna'ilaihirraji'un!!  Yanzu ina zata saka rayuwarta taji daɗi?

Taya kuma zata rayu da wani uban saɓanin Abbanta kuma abin sonta?

Tabbas ya khabeer ya cuci rayuwarta daya zama silar baiyanar wannan mummunan labarin wanda bata taɓa zatonsa ba bale tsammani a cikin rayuwarta!  Kamar daga sama taji saukar hannun Abba akan kafaɗunta, ɗago idanunta tayi waƴanda suka soye sabida tashin hankali tana kallonsa, murmushin ƙarfin hali Abba ya sakar mata sannan yasa hannu ya share mata ƙwallar dake shirin zubo mata yace " Mamana! Ki kwantar da hankalinki har yanzu nine Abbanki, haka kuma babu wanda ze rabani dake har duniya ta tashi, sabida son da nake miki ban taɓa nunawa kowa irin soyayyar danake miki ba, sabida banaso ki nemi wani abu ki rasa a cikin rawarki,  wllh kaf ƴaƴan dana haifa a cikina bantaɓa fifita soyayyar danake musu akan taki ba, hasalima kenake fifitawa akan tasu soyayyar!  Don haka ki sanyawa zuciyarki cewar duk wanda kikeso ki Aura wallahil'azeem shi zan Aura miki, don haka ki sanya a ranki cewar Abbanki har yanzu yana tareda ke Umaisa, haka kuma muddiɓ yana raye bazaki taɓa neman wani abu ki rasashi ba!

Faɗawa tayi a jikinsa ta ƙanƙameshi, lokaci guda kuma kukan datake dannewa ya samu nasarar ƙwace mata, kasa magana tayi illa ƙara ƙanƙame Abban datakeyi a jikinta, a ranta kuma wani irin zafi takeji a zuciyarta wanda bata taɓa ɗanɗanar makamacinsa ba a tarihin rayuwarta,  babban abinda yake ƙara ɗaga mata hankalima shine, shin ta ya zata rayuda wani uban wanda ba Abbanta ba??

Ji take dama ta mutu kota huta da wannan gagarumin bala'in dayake shirin kutsowa cikin Rayuwarta!!!

Ba umaisa kaɗaiba hatta Rumana seda zuciyarta ta karye, Ummie kuwa babu abibinda takeyi se kuka,  shiko khabeer ji yake kamar ya janyota ya rugumeta a ƙirjinsa ya rarrasheta, amma sedai babu damar hakan.

A fusace Abba ya maida kallonsa ga khabeer yace "tunda ka lalata komai ai hankalinka ya kwanta yanzu ko?
Be jira cewarsa ba ya kama hannunta sukabar perlourn zuciyarsa a dagule, be dire a ko ina da itaba se'a ɓangarensa, a babban perlourn dake part ɗin Abba suka zauna, kallonta Abba yayi tareda miƙa mata wayar dake hanunsa yace "Mamana sakamin number ɗin yaron da kikeso ɗin, karkiji komai har yanzu Abbanki yana taredake, haka kuma duk wanda kikeso wllh shi zan Aura miki Uwata.

Karɓar wayar tayi jikinta har wani rawa yakeyi ta sanyawa Abba number maheer ɗin, komawa Abba yayi kan ɗaya daga cikin kujerun dake perlourn ya zauna, sannan ya shiga kiran wayar,

Maheer dake kwance bisa ƙaya taccen perlourn sa, gaba ɗaya baya cikin nutsuwarsa sabida yanda tunanin duniya da kuma damuwa suka tisashi a gaba, komai na duniyar ma yanzu sam baya yi masa daɗi, yanzu babbar damuwarsa shine Rashin lafiyar mahaifinsa da kuma khabeer wanda ke shirin rabashi da abar ƙaunarsa, a haka wayar Abba ta shigo cikin wayarsa, ɗagowa dara-daran idanunsa yayi lokaci guda ya saukesu bisa kan wayarsa dake ihun neman agaji, shiru yayi yana kallon wayar tamkar baze ɗauka ba, haka kawai yaji gabansa yana faɗuwa don haka da sauri ya amsa wayar tareda yin sallama.

Amsawa Abba yayi tareda  cewa "Sunana Alhaji Mahmoud Muhammad mahaifin Umaisa.

da sauri mahir ya miƙe zaune tareda rissinawa tamkar Abban yana kallonsa ya shiga gaisheshi cikeda girmamawa,   basu wani jima suna wayarba Abba ya sanar dashi cewar ya turo magabatansa gobe idan Allah ya kaimu, sannan ya shaida masa cewar ya bashi Auren umaisa.

Waiyo Allah zando me karatu yaga irin farin cikin da maheer yake ciki, tamkar wanda akayiwa bushara da gidan Aljanna, haka itama Umaisan dukda irin tashin hankalin datake ciki hakan be hanata jin daɗin hakan ba.

nasiha sosai Abba ya dingayi mata kan cewar ta daure ta saki ranta, haka kuma ta danne zuciyarta ta yarda da ƙaddarar da Allah ya aiko mata,  babu yadda ta iya tunda haka Allah ya ƙaddaro mata, amma kuma meyasa Mamie bata sanar da ba tun farko cewar ba Abbane ya haifeta ba?

Wannan dalilin ne yasa taji a ranta cewar Mamie bata kyautawa rayuwarta ba, haka kuma batayi mata adalci ba, Tabbas mamie ta cutar da zuciyarta  amma babu komai haka Allah ya ƙaddaro mata, haka kuma ta karɓu ƙaddarar hannu bibbiyu.

Washe garida safe maheer ya shirya tsaf cikin wani dakakken boyal fari tass, wanda ya baiyana ainihin cikar halittarsa gamida haibarsa, haka kawai yakejin kansa cikin wani iriɓ farin ciki mara misaltuwa, a da ya ƙudurawa zuciyarsa cewar bazetaɓa zuwa Asibitin ba, amma haka kawai yau seya samu kansa da son ganin mahaifin nasa da kuma ƙaninsa Abdul da kuma baffaninsa, dukda cewar suma suna matiƙar son du haɗu dashi ɗin amma kuma yaƙi yarda su haɗun.

motarsa ya faɗa tareda murza mata key yabar harabar gidan, cikin mintunan da bazasu gaza 30 ba ya iso harabar Asibitin, tun kafin ya ida perker motar ya hangi motar gidansu hakanne ya tabbatar masa da cewar su baffa Giɗaɗo suna cikin Asibitin,  wani irin farin cikine ya sake sarƙe zuciyarsa, a nitse ya fito daga motar cikin takunsa na isa da ƙasaita,  a haka harya isa word ɗin da Dadyn yake,  ya jima a tsaye a bakin ƙofar glass ɗin dake ɗakin, seda ya ɗauki lokaci me tsaho yana kallon Ahalin nasa sannan ya tura ƙofar tareda sallama.

_*🎀KIYARDA DANI...!🎀*_
🎀🐾🎀

*♝ IÐŦɇƚƚIƓɇÐŦ WɍIŦɇɍ'ی ASSѻ📚✍️*

*💫DEDICATED: to Sis naja'art*

_*WRITING BY: Zm (CHuBaƊo)*_

*✨Special Gift for Hafsat Hafnan (my jika),.*

_Page:37_

___________📖Kuri Dady yayi masa yana kallonsa, hakama su baffa Giɗaɗo dake zaune a ɗakin, shiko Abdul kasa motsin kirki yayi sabida ganin yayan nasa, babban abida yafi komai ɗaure masa kai shine yanda yaga maheer ɗin yayi masa duhu kuma ya rame, buɗe masa hannayensa maheer yayi alamar Abdul ɗin yazo gareshi, Da sauri Abdul yazo yay hugging nashi harda hawayensa, a haka suka ƙarasa ɗakin hannunsu a sarƙe dana juna.

Tun kafin su ƙaraso Dady yaketa faman miƙawa maheer hannu cike da tsantsar soyayya, kansa a duƙe ya ƙarasa inda Dadyn yake tareda kama hannunsa da duka hannayensa biyu, wani irin sanyi ne yake ratsa zuciyar maheer tareda tsantsar ƙaunar mahaifin nasu, haƙiƙa yayi kewarsa ba ƴar kaɗan ɓa, tayanda bakinsa da laɓɓansa sunyi kaɗan wajen misaltawa me karatu yanda yakeji a wannan halin.

Ada yayi tunanin cewar ze iya Rayuwa batareda dady ba, Ashe abinda be sani ba shine yayiwa kansa ƙarya, jawoshi dady yayi zuwa jikinsa, lokaci guda kuma ya Rumgumrshi ƙam a ƙirjinsa, wasu irin zafafan hawayene suka shigayiwa ɗan da kuma uban zarya, a wannan lokacin duk wanda ya kallesu ze fahimci hawayen dake zuba a idanunsu ba hawaye bane kawai, isharace wadda ke sauka a bisa ɗanba ta soyayyar ɗa da mahaifi.

Sun jima a haka sannan Dady ya zare jikinsa daga na maheer, lokaci guda kuma ya ƙanƙame hannayensa yace "haƙiƙa na cutar dakai ɗana, hakakuma na zalunceka, banyi tunani ba ko kaɗan akan hukuncin dana zartar a gareka ba ko kaɗan, yau gani a gabanka ina me roƙonka slfarma a karona biyu don girman Allah ka yafewa mahaifinka kaji yarona !! Don Allah ka yafemin !!! Ya faɗa yana wani irin kuka kamar wani ƙaramin yaro.

Da sauri maheer ya rungumeshi yace "a'a Dady, har kullum kaine sama dani, haka kuma dukkan abinda zakayimin a matsayina ɗanka ɗolene nayi haƙuri dashi kuma nayi maka biyayya, amma kash se gashi na gazayin hakan, kabani Umarni amma na bijire maka sabida zafin raina na banza da wofi, a ƙarshe nazama nine silar rushewar ahalinmu, don haka nine ya dace na

baka haƙuri Dadyna don girman Allah ka yafemin kozan samu nutsuwar zuciya Dadyna!

Shafa kansa kawai Dady keyi yana hawaye, lokaci guda kuma ya saki murmushin farin ciki yace "kaƙika tayi gaskiya datace  a kwai ranar dazata zo maheer zeyi magana me cikeda tarin farsafa gamida ilimi a cikinta, Allah sarki! Da ace tana raye da idanunta sun gane mata wannan rana da mafaɗacin ɗana yayi magana cikin tattausan lafazi gamida soyayyah.

Kunyace ta kama maheer lokaci guda kuma ya sinkuyar da kansa ƙasa yana murmushi, se'a lokacin ya ɗago ya gaida su baffa Umaru, dariya sukayi gaba ɗayansu sannan sukace  seyanzu ka ganmu kenan.

A nan baffa Giɗaɗo yayita musu nasiha akan sakaci da addu'ah, a haka Dr. Abdullah ya shigo ya samesu, bayan sun gaisa ne ya fara duba jikin Dadyn, bayan ƴan rubuce-rubucen dayayi ne ya rubuta musu takardan sallamah,  a nan ne Dady yake tambayarsa ina Dr. Khabeer?

Murmushi Abdullah yayi sannan ya sanar dashi cewar khabeer bashida lfy, amma yace ya sanar dashi cewar dazarar ya ji sauƙin jikinsa zezo har gida ya sake duba jikin nasa,  sosai Dady yaji dadin hakan tareda yi masa addu'ar samun sauƙi. A haka suka tattara suka bar asibitin suka ɗauki hanyar Garki inda gidan Maheer yake,

Tun kan su shiga farfajiyar gidan Abdul yake yaba yanayin tsarin gidan, cikeda tsokana ya kalli maheer yace "yaya gaskiya gidannan yamin kyau sosai wllh, da ace na isa Aure wllh da a nan zan zauna da matana inyaso kai ka nemi wani,  wata uwar harara maheer ya sakin mai dole tasa Abdul ya tsuke bakinsa, horn suka zuba me lafiya, da sauri lawan mai gadi ya wangale musu get ɗin suka kunna kai zuwa cikin gidan, a nitse suka nufi perking lot ɗin da aka tanada don ajiye motoci suka perker motocin, dannan suka fito cikin Aminci gaba ɗayansu, cikin takunsa na isa yayi musu jagora zuwa cikin gidan, a daidai ƙofar shiga maine perlour ɗin gidan yay kaciɓus da victoria, cikeda gimamawa ta kalleshi tace "barka da dawowa sir, dama wancan matan da muke horarwa ne ciwon dake ƙafarta yayi tasanani,  a halin yanzuma banda wari da tsutsa babu abinda yakeyi,  shima ɗayar matan  bashida lfy amma sedai ciwon nasu ba iri ɗaya bane.

Hararарta maheer yayi sannan yace "toni ina ruwana me zan musu?  Kedai kawai kuci gaba da horar dasu   shine kawai aikinku, ya juya da sauri ze shige Dady  ya jawoshi, cikin tattausan lafazi yace "boy  suwaye waƴannan yaran?  nd kuma wasu matane kake cewa a horar dasu?

murmushi yayi  sannan ya waske yace " Dad muje don Allah banaso kai stresing kanka akan waƴanda basuda wani amfani, all you want yanzu is to rest muje kawai,

wani irin kallo Dady yayi masa dole tasa ya fara shafa kai, baffa Umaru ne ya kalli Victoria yace "ke muje ki kaimu muga wasu matane wannan haka. Kallon Maheer Abdul yayi sabida tabbas yasan a kwai Lauje cikin naɗi, dole a kwai abinda maheer ɗin yake ɓoye musu wanda bayaso a sani, aiko suna haɗa ido da maheer ya kashe masa ido ɗaya, da sauri sukabi bayansu baffa

Umaru zuwa ɗakin da Hajiya murja suke, tun kafin su ƙarasa ɗakin wani irin wari da ƙarni ya gauraye musu hanci, dole hakan yasa suka tsaya daga ɗan nesa da ɗakin, wani irin kallo dukansu sukebin maheer ɗin dashi wanda yafi kamada na zallar tuhuma. Turo baki yayi sekace wani ƙaramin yaro, cikin wani irin salon irin na sangartattun yaran masu kuɗin nan yace "uhmn Dady nifa banyi komai ba kawai nayi abinda ya dace ne"  ya ƙare maganar yana wani male baki.

murmushi dady yayi sannan yace " nasani bakayi komaiba yarona, amma zo nan kaji wani magana, maƙe kafaɗa yayi sannan yace "naƙi wayon wllh idan nazo murɗemin kunne zakayi. Dariya suka kwashe habaɗayansu dashi , sannan Baffa Umaru yace "Maheer kenan dama me hali ai baya fasa halinsa. Victoria yayiwa inkiya data fito dasu Hajiya murja da kuma Aminiyar tata.

cikin mintuna kaɗan victoria da Yukeria suka fito dasu waje tamkar wasu kayan wanki suka wurgosu gabansu Dady,  nan da nan warin ƙafar ya gauraye gurin, da sauri suka toshe bakinsu da hancindu da hannayensu,  gaba ɗaya duk sun jeme sun koɗe tamkar basu ba , sabida yanda rayuwa ta juya musu baya.

Lokacin da Hajiya murja ta ɗago idanunta ta kalli Dady wani irin mugun sanyi jikinta yayi, lokaci guda kuma ta fashe da wani irin kuka tareda ƙoƙarin kamo gefan rigar Dadyn, da sauri Abdul bige mata hannu tareda jifanta da wani ɗan iskan kallo wanda yasa gabaɗaya taji ta muzanta a gabansu,  kasa magana Dady yayi illa kallonta kawai dayakeyi, daƙar ya iya buɗe baki yace "tabbas bahaushe yayi gaskiya daya kirayi duniya da sunan makaranta! Zuwa yanzu na tabbata ta koya muku karatun da baku taɓa jin kamarsa ba balle kuyi hadda, dama ita duniya haka take, a yayin data shimfiɗawa mutum tabarmar isa da iko  ya hau kai yayi kane-kane sekiga gaba ɗaya ya manta da mutuwarsa ko makomarsa, na tabbata baki taɓa zaton duniya zata juya muku baya  irin haka ba, amma se gashi tun ba'ayi nisan kiwoba kin fara girbar abinda kika shuka wanda na tabbata da cewar wannan ciwon dake ƙafarki shikaɗai ma ya isa yayi ajalinki, don haka ku tattara dake da abokiyar cin mushen naki kuyi gaba, haka kuma na sakeki saki uku..!!!

wani irin kuka ta fashe dashi me matiƙar taɓa zuciyar duk wani me sauraronta,  jiki a saluɓe su dady sukabar gurin, nan akabar su maheer da abdul a gurin, kuɗi maheer ya zaro daga aljihun wandonsa rafar ƴan dubu ɗaiɗaya guda biyu ya miƙawa Victoria yace "gashi wannan kuɗin aikinku ne keda sister ɗinki, daga yau aikinku ya ƙare a gidannan. Cikeda farin ciki suka karɓi kuɗin tareda surfa masa godiya, seda suka dingurewa su hajiya murja kai sannan suka bar gurin suna masu ƙara godewa maheer ɗin, sabida tunda uwarsu ta haifesu basu taɓa riƙe kuɗi masu yawan haka ba.

Daga ɗan nesa da ita Abdul ya tsaya yace "ke murja kike ko wane?  Shin kinyarda da maganar da muka faɗa miki cewar se munga ƙarshenki nida ya maheer?

"ada na tabbata baki taɓa zaton hakan zata kasance ba ko?" hhhhhhhhhh wannan kaɗai ya isa ki gane cewar aikida hankali yafi aiki da agogo, ya ƙare maganar tareda zabga mata wani

azababben mari me Ifiya.

da sauri ta dafe fuskarta tana hawaye, murmushi ya sakin mata sannan yace "kinsan meyasa na mari wannan ƙazamar fuskar taki?

"na mareki ne sabida ki dinga tunawa dani a rayuwarki, ke kuma me kamada jinjirin biri ya nuna Binta ƴar kwabo yace "kije basena dakeki ba ciwon dayake jikinki ma kaɗai ya isheki ishara.

Murmushi maheer yayi mai ƙayatarwa sannan  yace "Muje  yaron momy manta da waƴan nan matan, har sun fara tafi maheer ya juyo yace dasu "yanzun kam zaku iya tafi duk inda kukeso, sabida bana buƙatarku a cikin gidana, aiko kamar jira suke suka miƙe daƙyar harda ɗan gudunsu suka fice daga gidan suna wani irin kuka gwanin ban tausayi,

a haka su maheer suka ƙarasa perlourn zuciyarsu feessss

cikin mintuna kaɗan order ɗin da maheer yayi musu na abinci ta iso, da kansa ya jera komai a daining aria ɗin sannan ya koma bedroom ɗinsa ya fesa wanka ya fito sanye da jallabiya maroon colour,  suma su Dady ba'a barsu abaya ba seda suka Ashshaka wankansu sannan suka hallara a daining sukaci suka sha, bayan sun kammala ne  aka shiga hirar yaushe gamo, nan baffa iya ya kira Dadaji a waya ya haɗata da dady sukaita hira tamkar bazasu dena ba, nan Dady ya sanar da ita cewar insha Allah jibi zasu wuce kaduna, inyaso daga nan zezo gida ya ganta tareda sauran ƴan uwa da abokan arziƙi.

Karɓar wayar maheer yayi shima suka gaisa da ita,  sosai Dadaji ta jajanta masa abinda ya faru tareda nuna alhininta akan hakan, dariya maheer yayi batareda yace komai ba sukai sallama.

Bayan sun gama hirar ne maheer yake sanar dasu dady batun soyayyarsa da Umaisa tareda shaida masu yanda  sukai da Abbanta a daran jiya.

Sosai suka nuna farin cikinsu akan hakan, nan Baffa Giɗaɗo yake tambayarsa cewar ya sunan mahaifin yarinyar?  A nan take maheer yace "sunansa Alhaji Mahmoud Muhammad kuma yana aiki ne a Works of Housing  fake nan abuja.

wani ƙaya taccen murmushi Baffa Giɗaɗo ya saki sannan yace "indai wannan ne ai baɗuwa tazo daidai da zama Maheer, indai Mahmoud ne ai nasanshi tare mukai makaranta dashi a KSUT dake wudil, asalinsa bakano ne a wani ƙauye dake maƙotaka da wudil ɗin, mutumin kirkine sosai, don haka karkaji komai goɓe idan Allah ya kaimu zamuje mu nema maka Aurenta da yardan Allah.

_*🎀KIYARDA DANI...!🎀*_
🎀🐾🎀

*♝ IᗪT ҽ ɭɭIƓҽᗪT WrIT ҽr'ی ASSɷ📚✍️*

*💫DEDICATED: to Sis naja'art*

_*WRITING BY: Zm (CHuBaƊo)*_

*✨Special Gift for Hafsat Hafnan (my jika),.*

_Page:38_

*KUKAN KURCIYA.....👇*

*_Ya ilahi! Haqiqa duniya a cike take da ababan mamaki kala-kala, haka kuma al'amarinta mai girmane, tabbas bahaushe yayi gaskiya dayace inda ranka kasha kallo a duniya, duniya ta zarce mahangin kowa shiyasa ma ta ishi kowa riga da wando, haka kuma duk shirinka da tarin guzirinka wata rana seka barta, don haka yi maza ka tattala lokacinka wajen gudanar da abinda ze fissheka a duniyarka da kuma lahirarka, yi qoqari ka iya furicinka komai qanqantarsa idan ba haka ba seya jefaka cikin zargin jama'a, Yi qoqari kamaida komai ba komai ba a gaba seka tadda rabo mafi girma da alfanu.😊_*

___________📖washe gari kamar yanda baffa Giɗaɗo ya faɗa haka kuwa akayi, don haka maheer ya kira Umaisa ya shaida mata zuwan magabatan nasa, duda cewar bata cikin yanayi me daɗi hakan be hanata baiyana masa farin cikinta ba, seda suka ɗan taɓa hira kaɗan sannan sukai sallama da juna cikeda zallar soyayya.

Tana kashe wayar wazu zafafan hawaye suka shiga sakki mata, yanzu inazata saka rayuwata taji daɗi sabida Allah?

Shin ta ina zata fara neman mahaifinta da kuma danginta?

Ashe dama duk abubuwan datakeyiwa Abba yana haƙuri da ita ɗama bashine mahaifinta ba?

Rashin sanin amsoshin wannan tarin tambayoyin nata sunfi komai ɗaka mata hankali a rayuwarta, musannan idan ta tuna wasu lokutan da suka gabata a shekarun baya, komai ƙanƙantar ciwo idan ya sameta Abba baya taɓa samun kwanciyar hankali har seta warke sannan hankalinsa yake kwanciya, a kwai lokacin datayi wani mugun zazzaɓi me zafu kamar zata mutu a ranar Abba kasa bacci yayi, washe garin ranar ko karyawa beyiba ya tafi Asbitin ya zauna da ita, tun daga ranar ya hana kowa zuwa yace a barshi shine zeyi jinyarta, amma wai duk irin soyayyar daya nuna mata ace wai bashine ya haifeta ba?

"innanillahiwa'inna ilaihirraji'un waiyo ni Umaisa ina zansa rayuwata naji daɗi ne?

Ya Rabbi ka yaye min wannan ƙuncin rayuwar baƙin cikin danake cik.....!!!    Wani irin kuka ne yaci ƙarfinta dole ta kasa ƙarasa maganar dake kan harshenta.

Meyasa mamie zatamin haka a rayuwata ne?

Mamie  dake tsaye a bakin ƙofar ɗakin duk jikinta ya gama sanyi sabida ganin Halinda Umaisan ke ciki, a hankali take takowa har zuwa tsakiyar ɗakin, jiki babu ƙwari ta miƙa hannunta zuwaga kafaɗun Umaisa, aiko hakan yayi daidai da juyowarta fuskar nan duk tayi ja sabida kuka tace "A'a Mamie! Don girman Allah karki taɓani, a halin yanxu sam bana buƙatarki a taredani, mutumin daya raineni batareda alaƙa ta jini ta shiga tsakanina dashi ba ya riga ya gama cikemin gurbin duka dangina da maihaifana gaba ɗaya, don haka na roƙeki sabida girman Allah mamie ki ficemin daga ɗaki ko zan samu hankalina ya kwant.......

Wani gigitaccen mari Mamie ta ɗauke umaisa dashi, wanda yasa jinta da kuma ganinta suka ɗauke na wucin gadi, sannan mamie ta nunata da yatsa tace "haƙiƙa idan kika hukuntani akan ƙaddarar da Allah ya aiko miki a cikin rayuwarki zaki tabka babban kuskure a Rayuwarki Umaisa!!  Nifa mahaifiyarki ce, wani adalci kike nema nayi miki wanda ya wuce na haifeki ta hanyar Aure?"

"don kawai nayi miki laifi ban sanar dake waye mahaifinki ba se hakan ya baki damar dazaki jefeni da maganganu masu zafi irin haka?"

"Kadafa ki mata cewar a kwai tarin ƴaƴa a duniyar nan waƴanda iyayensu suka haifesu batareda aure ba, sukuma waƴannan yaran mezasuce da iyayen su kenan ?"

"Seni dana haifeki ta hanyar Aure wanda Al'uma dadama suka shaida hakan ne zan fuskanci irin wannan hukuncin daga gareki Umaisa?

"yau koda kece a matsayina umaisa abinda nayi shi zakiyi, bafa ninace mahaifinki ya sakeniba, shine dakansa ya yanke wannan hukunci batareda yayi la'akari da cikinki danake ɗauke dashi ba, shin a matsayinki na ƴa mace zaki sake waiwayar wannan mutumin a iya rayuwarki?"

Zubewa mamie tayi a gurin tareda sakin kukan data daɗe tana dannewa,  da sauri Umaisa ta matso jikinta ta rungumeta tana kuka tana bawa Mamie haƙuri akan bisa rashin kyautawar datayi mata, bayanta mamie ta dinga shafawa sannan tace "ki gafarceni ƴata, haƙiƙi ban kyauta miki ba sam, kawai dai babu yanda na iya ne umarnin mahaifina nakebi."

a haka wani wahalallen bacci ya ɗauketa, babu abinda take saukewa sama da ajiyar zuciyar kukna data gurza, sosai fuskarta da bakinta sukai jajir sabida kuka abinka da farar mace, kwantar da ita Mamie tayi a saman gadon tareda gyara mata kwanciya ta lulluɓeta da lallausan bargon dake saman gadon, kallonta kawai Mamie takeyi a ranta tana mejin wani irin tsusayin

ɗiyar tata,  yanzu ta ina zata fara neman Bawuro a Rayuwarta balle harta danƙa masa ɗiyarsa ta huta?

Wasu siraran hawayene suka shiga zubo mata sabida rashin sanin cikakkiyar amsar tambayan datayiwa kanta,  share ruwan hawayen tayi da bayan hannunta sannan ta miƙe tabar ɗakin, bayan fitarta babu jimawa Khaber ya shigo ɗakin, sanye yake cikin wata milk ɗin jallabiya wadda tai matiƙar karɓar jikinsa, kallo ɗaya zakayi mai ka fahimci ramar dake  fuskarsa, a hankali ya dinga takawa cikin takunsa irinna ƙasaitattun maza masu jida kansu haryakai bakin Gadon ya zauna,  ƙurawa fuskarta manyan Golden Eyes ɗinsa yayi yana kalonta cikeda ƙauna, wata sassanyar ajiyar zuciya ya saki wadda ke baiyana tsantsar kewarta dayayi, wani irin so yakeyi mata wanda Yakejin baze iya musltawa ko wani mahaluki shiba a duniya, a hankali ya miƙa hannunsa zuwa kan kyakkyawar fuskarta ya shafa, tsuke baki tayi kamar wadda ke shirin magana amma kuna still idanunta a rufe suke tana ta kwasar baccinta, wani cute smile ne yayi escaping lips nashi sannan ya zaro wayarsa dake aljihun gaban jallabiyarsa ya shiga snaping ɗinta, ya jima a ɗakin yana aikin ɗaukanta hotunan sannan ya miƙe yabar ɗakin, kamar daga sama taji anata kiraye-kirayen sallan Azuhur, da sauri ta miƙe ta shiga toilet tayi wanka tareda ɗauro Alwala, a gaggauce ta shirya sannan ta tada sallah, cikin mintuna da bazasu gaza 7 ba ta idar, a nan ma seda taci kuka sosai tana ronƙon Allah kan yayaye mata damuwarta sannan kuma yayiwa rayuwarta zaɓin dayafi zama alkhairi a gareta.

wayar gefan gadonta ta ɗauka ta shiga kiran Abba, nan ta sanar masa batun zuwan iyayen maheer ɗin, murmushi Abba yayi me sauti sannan yace "mamana ai ya kirani ya sanar dani zuwansu a yau ɗin, haka kuna nayi farin ciki da hakan, sannan ban Amince ki sanarda kowa wannan batunba na zuwan nasu, daga nan zan shirya dukkan abinda ya dace, a ƙarshe kuma ina me sanar dake cewar muddin ina raye wallahil'azeem wanda kikeso shi zan baki ki aura, ta hakane kawai zan Sauke nauyin da Allah ya ɗoramin a kanki, karki taɓa yarda ki Auri khabeer Da sunan zakiyi min kara, sabida bana cikin iyayen da suke matiƙar son kansu, ni ubane me adalci ga Ahalinsa!

kasa magana tayi illah hawayen dake zubo mata kamar an kunna fanfo, muryarta na rawa tace "i love you my bravo Dady!!

murmushi yayi sannan yace " love you too sweetheart."

A haka suka gama maganar ya kashe wayar, duk wani abu daza'a buƙata Abba ya shirya komai batareda su Mamie sun sani ba,   ƙarfe 5:00pm su baffa Giɗaɗo suka hallara a unguwar Zone E Apo legislative Quarters  manyan motocine na alfarma, wanda kallo ɗaya zakayi musu kasan masu matiƙar tsadane, a haka me gadi ya wangale musu ƙofar gidan duka danna hancin motar zuwa cikin gidan,  inda aka tanada don perker motoci sukaje sukayi parking sannan suka firfito, ciki kuwa harda Dady wanda ke sanye cikin wata dakakkiyar shadda giznah wadda keta uban sheƙi tana yararin tsada,

A nitse suka ƙaraso harabar gidan fuskokinsu duk a ɗaukeda murmushi,  da usman suka fara

cin karo sabida Abba ya sanar dashi zuwansu kan cewar idan sun iso ya kaisu ɗakin baƙi na musamman,  haka kuwa akayi cikin mintuna kaɗan Usman yayi mudu jagora zuwa cikin perlourn, nan da nan ya cika gabansu da kayan motsa baki iri-iri,  sannan Abba ya fito shima fuskarsa ɗauke da murmushin farin cikin ganinsu.

da sakin fuska ya ƙaraso perlourn tareda tarbar babban Abokinsa wato  Giɗaɗo Abubakar lamiɗo tareda ƴan uwansa, sosai Abba yaji daɗin ganin  Aminin nasa, nan suka shiga hirar yaushe gamo, bayan lafawar komai ne suka gabatar da bukatarsu ta nemawa Ɗansu Auren ɗiyarsa, ba musu Abba ya Amince kuma ya basu, nan ya buƙaci da su fito da sadaki ayi komai a wuce gurin inyaso daga Baya semu gudanar da sauran shagulgulan,  sosai sukai na'am da batun Abban, nan baffa Umaru ya zaro dubu hamsin Ya miƙawa Abba, a nan take mutanan dake perlourn suka shaida Ɗaurin Auren Maheer Nasir Lamiɗo da Umaisa Mahmoud muhammad, akan sadaki dubu hamsin,

Shiru Usman yayi zuciyarsa duk a dagule lokaci guda kuma wani irin tausayin yaya Golden ya shiga kwaranya a zuciyarsa, yanzu shikenan ya Golden ya rasa Umaisa kenan?

Amma meyasa Abba zeyiwa khabeer haka?   Indai kuwa har hakane Abba beyiwa khabeer adalci ba, a haka taron ya tashi kowa yana san barka da karamci irin na Alhaji mahmoud, mota baffa Giɗaɗo ya koma ya ɗakko daurin goro guda hudu mayanya da kuna katan na alawa ya koma perlourn ya kai ya danƙarawa Abba kan cewar a rabawa mutane don su shaida.

se dabda marib sukayiwa Abba sallama suka wuce gida,  a nan Abba ya kalli Usman yace "son maza ka ɗauki goron nan da alawan ka shiga musu dashi gida, ba musu Usman ya kwasa yakai maine perlour ɗin gidan, seda Abba yayi sallan magrib sannan ya shiga gidan, yakoyi sa'a duk suna perlorn saɓanin Umaisa data ɗaura da zaman ɗaki tun lokacin dataji matsayinta a gidan, da sallama ya shigo perlourn tareda zama a ɗaya daga cikin kujerun dake perlourn, seda suka gaisa da Baba sannan ya miƙa mata goro da Alawar dake gabansa yace "Baba ga goro nan da alawar ɗaurin Auren ƴata Umaisa da Maherr, seku rabawa sauran jama'a don suji kuma su shaida,  wata muguwar faɗuwar gaba Ummie yayi lokaci guda kuma ta zube a ƙasan gwiwoyinta tana wani irin kuka.

Hakanne ayi dadai da shigowar yaya Golden perlourn!!!!!!

_*🎀KIYARDA DANI...!🎀*_
🎀🐾🎀

*♝ IᗪTↄ€lIGↄ€ᗪT WrITↄ€r'ی ASSω📚✍*

*💫DEDICATED: to Sis naja'art*

_*WRITING BY: Zm (CHuBaƊo)*_

*✨Special Gift for Hafsat Hafnan (my jika),.*

_Page:39_

*KUKAN KURCIYA👇*

*_Haqiqa ilimi baiwane, Rayuwa kuma hikayace, Jahilci ba uziri bane balle yazama katangar jingina ga kowa, Yi qoqari ka hangi abinda yake kusa dakai ba wanda yake nesa dakai ba, yawan walwala yafi yawan Qunci,  yi qoqari kaso kowa idan kayi hakan dame zaka ragu.🤷‍♀️_*

____________📖 kasa motsin kirki khabeer yayi, daƙyar yake iya ɗaga ƙafafunsa har zuwa inda Abba ke zaune,  murmushin ƙarfin hali ya saki tareda kama hannun Abba yace" Na tayaka murna sosai Abba, da har kasamu nasaran sauke nauyin da Allah ya ɗora maka a matsayinka na Uba me adalci ga Ahalinka."   yana kaiwa nan a maganarsa ya miƙe yabar perlourn zuciyarsa na masa wani irin zafi,

Wani irin kallo Baba ta dinga bin Abba dashi, amma sedai babu yanda ta iya tunda ya riga yayi gamon kansa wajen bada Auren Umaisa ga wani can daban, ƙaddara kenan tariga fata.

Mamie kuwa kasa magana tayi sabida yanda taji maganar kamar saukar aradu a tsakiyar kanta, amma meyasa Abba zeyi haka bayareda neman shawaranta ba? Yanzu meye ma'anar abinda ya aikata kenan?

Zubewa tayi a gurin  tana mai firta "hasbunallahuwani'imal wakeel, yanzu dawani ido duniya zata kalleni ni Badi'atou?

Kukan Ummie ne kawai yake tashi a tsakiyar perlourn, Usman ne yayi ƙarfin halin ƙarasawa inda Ummien ke zaune ya riƙeta tareda faɗin "don girman Allah ummie kiyi haƙuri kidena kukan nan, idan kema kina kuka taya zamu samu ƙarfin gwiwan Rarrashin ya Golden?"

"Ummie kefa Uwace kuma me bamu ƙarfin gwiwa akan komai, don haka don Allah ki dena damuwa ki manta da komai mubarshi a matsayin ƙaddaran da Allah ya aiko mana gaba ɗaya,

Miƙewa Abba yayi yabar perlourn sabida baze iya juran ganin zubar hawayen Ahalin nasa ba, shi kansa babu yanda zeyi ne shiyasa, haka kuma bayaso ya tauye umaisa ko kaɗan, tunda har yayi alƙawarin ze cike mata gurbin mahaifinta dole ne ya bata abinda takeso muddin beci karoda koyarwan addini ba, musamman ma yanzu dayake a kwai ciwo a rayuwarta wanda yasa take keɓance kanta ita kaɗai, wannan kawai ya isa yasa ya bata abinda takeso badan komai ba kodan sabida farin cikinta.

Dafa kafaɗun Mamie baba tayi, sabida yanda ta lura da irin tashin hankalin data ke ciki, sabida kalaman na Abba, a hankali Baba ta buɗe baki tace "Kiyi haƙuri Badi'atou ki karɓi Abinda ƙaddara tazo dashi, tun ran gini ran zane Allah ya rubuta cewar ba Khabeeru bane mijin Fatsima, shiyasa kukaga har hakan tafaru, a halin yanzu babu yanda muka iya wanda ya wuce mu sanyawa ƙamarin albarka tareda yi mata fatan zama lfiya a gidan Aurenta.

Wata doguwar ajiyar zuciya Mama ta sauke, lokaci guda kuma ta shiga share zufar dake yanko mata tace "tabbas abinda Baba ta faɗa gaskiyane, haka kuma babu wanda ya isa yaja da yin Allah, dama kama nakane Allah yana nashi, duk musulmin ƙwarai dolene yayi imani da dukkan Abinda Allah ya ƙaddaro masa a rayuwa, don haka munayiwa Umaisa Fatan Alkhairi a gidan Aurenta, shikuma khaberr Allah yayi musu zaɓin alkhairi.

Da amin suka amsa gabaɗayansu Amma banda Mamie wadda gaba ɗaya ta koma kamar wata sakarya sabida yanda abin ya girgizata ainun.

A haka ahalin suka kasance cikin ƙunci  a wannan rana.

A ɓangaren su maheer kuwa ba ƙaramin farin ciki suke ciki ba musamman ma da sukaji abindasu Dadyn sukazo dashi, a rayuwar maheer shine labarin dayaji mafi daɗi a rayuwansa, don haka misalta farin cikin maheer ɗin abune mawuyaci a garni dashi gaba ɗaya,  nan dady ya shiga kiraye-kirayen wayan abokan arziƙi da manya-manyan abokansa,

Baffa umaru ne ya kira su Dadji ya sanar dasu dukkan abinda ya faru, sosai itama ta nuna farin cikinta da auren maheer ɗin, a haka zuriyar suka kasance cikin walwala da farin ciki mara misaltuwa,

Umaisa ce zaune bisa cafet ɗin dake ɗakinta  duk ta zama wani iri kamar ba ita ba, a haka Ruman ta shigo ɗakin jiki babu ƙwari ta zauna daga gefanta, tajima a zaune babu wanda yace da ɗan uwansa ƙala, Rumance tayi ƙarfin halin miƙa mata goro da alawan dake hannunta tace " wannan naki ne umaisa, haka kuma shine ze baki tabbaci wajen shaida cewar kin zama mallakin *ZAƁIN RANKI* kamar yanda kike fata, haka kuma a matsayina na ƴar uwarki inayi miki fatan alkairi a zaman dazakiyi da mijinki abin sonki, har kullum kallo ɗaya nake miki umaisa, ban taɓayi miki kallon keba jinina bace, haka kuma ina matiƙar sonki ƴar uwata!"

ƙanƙame juna sukayi itada Ruman lokaci guda kuma suka saki wani irin kuka a tare, ko kaɗan umaisa bata girgiza dajin batun Aurenta a bakin Ruman ba,  sabida tashin hankalin datake ciki ya shallake na maganar Aurenta da maheer ɗinta abin sonta!!!!

_*🎀KIYARDA DANI...!🎀*_
🎀🐾🎀

*♝ IᑎTᏋ﴾﴾IᏀᏋᑎT WᏒITᏋᏒ'ی ASSᏇ📚✍*

*💫DEDICATED: to Sis naja'art*

_*WRITING BY: Zm (CHuBaƊo)*_

*✨Special Gift for Hafsat Hafnan (my jika),.*

_Page:40_

*_Eid mubarak to all Muslim's Ummah, may Allah Subahanahuwati'Alah accept our Ibadah and forgive our sins, Ya Allah kayi mana Rahamah sannan ka wadatamu a duniyarmu da kuma lahiran mu gaba ɗaya, Ya Allah ka rufamana Asirin Duniya da kuma na lahiranmu🤲 inayiwa ɗaukakin Al'umar Musulmai barka da Sallah😀_*

___________📖 lokaci guda taji gaɓɓan jikinta duk sunyi sanyi gefe guda kuma na zuciyarta ya shiga bigawa A hankali, Hakanne ya saukar mata da wani irin yanayi me wahalar misaltawa, sakin Rumana tayi lokaci guda kuma ta dafe kanta dayayi mata wani irin mugun nauyi, murmushin ƙarfin hali Rumana ta saki tareda share tarin ƙwallar dake zubo mata tace "haƙiƙa komai na duniya yana da mujarrabinsa, haka kuma kowani Ɗan Adam na duniya yanada kalar tasa Ƙaddarar muddin a kwai Rai a cikin gangar jikinsa,

Rumana ta ƙara da cewa "muddin kai musulmi ne kuma me imani dole ne kayi imani da duk wata jarrabawa da zakaci karo da ita a rayuwarka, mekyau ko mara kyau, amma Tabbas da ace inada ikon canza wannan ƙaddarar data kunno kai kuma take barazanar Tarwatsa mana farin cikin Ahalinmu wllh dasena canzata da gaggawa Umaisa!

Share hawayen dake zubo mata Umaisa tayi da bayan hannunta sannan ta sake kallon Rumana a karona biyu tace "jarrabawar kenan Rumana! inda ace munada wannan damar wllh tunkafin wani yayi yunƙurin canza Wannan ƙaddarar nida hannuna zan Riga kowa canzata ƴar uwata, a kaina ni kaɗai Mutanen da Basu cancanta in sanyasu kuka ba yau gashi nida kaina nasasu kuka Ruman, Tun tasowata suke ƙaunata basu taɓa banbantani da ƴaƴan cikinsu ba, haka kuma sunyimin karamcin da a rayuwa Bazan taɓa iya biyasu da kamarsa ba koda Raina zan bayar ya zama fansa a garesu!! se'a yanzu nake ganin tarin wautar dana Aikata Gamida butulci me girma akan Gudan Jinin Abba da har na kasa Fahimtar damuwar Yaya Khabeer a kaina!!

Umaisa tacigaba Da cewa "A halin yanzu ji nake gabaɗaya komai ya tsayamin cak, banida wani buri wanda ya wuce insan Halinda Yaya khabeer yake ciki Ruman!!! Ta faɗa tareda fashewa da wani irin kuka me taɓa rai.

Kasa magana Rumana tayi haka kuma ta kasa rarrashinta, a halin yanzu bazata iya misalta irin

abinda takeji a Zuciyarta ba gameda Umaisan, shin haushinta ya kamata taji kokuma Uzirin ya kamata tayi mata?  Miƙewa tayi tabar ɗakin zuciyarta gaba ɗaya babu daɗi, sam bataso ta tsani Umaisa akan dalilin da Ko itace a matsayin umaisan iyakar abinda zatayi kenan, ɗan Adam yana da ikon daze sarrafa rayuwarsa amma da zarar ƙaddara ta kunno kai dole ne kayi haƙuri da canzawar  wasu al'amuran,  Dole ne kawai suyi haƙuri da abinda ƙaddarar tazo dashi na Auren Umaisa da wanin yaya Golden. A haka ta faɗa ɗakinta Tana aikin zancen zuci tareda murza keyy A ƙofar ɗakin ta faɗa gaɗo.

*_ƁANGAREN_* umaisa kuwa daƙyar ta iya miƙewa ta fito daga ɗakinta, zuciyarta na mata wani irin nauyi wanda ta kasa gane ma'anarsa balle tasan dalilin wanzuwarsa, a hankali take ɗaga ƙafafunta tana takawa harta samu nasarar isa ƙofar part ɗin Khabeer ɗin, da sallama ta shiga perlourn, tsayawa tayi cak sabida yanda ƙwayar idanunsu ta sarke cikin na juna, sun jima suna kallon junna kowa da abinda yake saƙawa a cikin zuciyarsa a gameda abokin gamin nasa, itace ta fara yin ƙasa da idanunta sabida yanda taci karoda tsantsar tsagwaron zallar sonta da kuma narkakkiyar ƙaunarta a cikin ƙwayar idon yaya Golden ɗin!  Karo na farko kenan a rayuwarta dataji  cewar ta tsani kanta, haka kuma bata cika ƴar Halak ba tunda har ta kasa sakawa ɗan mutumin daya Raineta tamkar ƴar cikinsa da soyayyarta a lokacin dayafi kowa buƙatarta ,  tabbas ita Ɗan adamce kuma butulu haka kuma wada ta kasa mayarda alkairi da kirki amma ta cike gurbinsa da Butulci, Zubewa tayi a ƙasa lokaci guda kuma ta saki wani marayan kuka wanda yafi kamada na tsantsar dana sani Da nadama mara misaltuwa!!

Murmushi Khabeer ya sakin mata wanda yafi kamada na ƙarfin hali sannan ya Tako  zuwa gareta, a hankali ya durƙusa dab da ita tareda shanye duk wata damuwa dake kan fuskarsa yace "haba ƴar Amaryan ƙanwata Kuma  ƴar gaban goshin Abbah, meyasa kike kuka irin haka? You have to know that we care for you so much  dear, be kamata kiyi kuka ba a halin yanzu your Dady is with you and Yaya Golden, ya faɗa yana nuna ƙirjinsa da babban yatsan hannunsa na dama, fuskarsa kuma ɗauke da wani ƙayataccen murmushi me ɗaukeda son bata ƙarfin gwiwa,

Ƙuri tayi masa tana kallonsa, ɗaga mata kai yayi  ta tareda faɗin "Come on Amaryan mu taso mana, ya faɗa cikeda rarrashi, amma a zahiri danne zuciyarsa kawai yakeyi sabida harga Allah baya ƙaunar zubar hawayenta kokaɗan, a duk lokacin da take kuka ji yake tamkar ana zuba masa narkakkiyar dalma a cikin zuciyarsa.

miƙewa tayi tsaye sannan ya nuna mata ɗaya daga cikin kujerun perlourn yace "zauna.

ba musu ta zauna system ɗinsa ya koma ɗaki ya ɗauko sannan ya fito ya zauna daga ɗan nesa da ita kaɗan, amma ta yanda zata iya ganin Icon ɗin system ɗin, wani adireshin yanar gizo na ƙasar Tourkey Ya shiga  nan da nan wasu rantsatsun hotunan kayan ɗakin na Royal chair's ne ƴan gaske Masu azabar kyau kala-kala suka baiyana a jikin Icon na computer ɗin, Murmushi ya saki wanda har seda beauty point ɗin gefan fuskarsa na dama ya lotsa sosai sannan ya kalleta yace "Oya zoki zaɓi wanda kikeso, a cikin nan.

narai-narai tayi da ido zatamai kuka ya haɗe rai yace "wai ina wasa dake ne dazaki sani agaba kinamin kuka? Ki sakko ki zaɓa nace bawai ki tsaya kinamin kuka ba, jikinta a mace ta sakko ƙasa tareda matsawa inda yake tana kallon kyau da tsari irinna kayan, kallonsa tayi amma setaga idanunsa Yafi karkata akan pic ɗin farko, drower ce me kyau bana wasa ba, hakama gadon shima, sam fuskar gadon ba irin ƙatuwar nan bane amma an tsarata bisa tsari inda akayi musu yarfen silver da Kuma ruwan zinare, haka kawai setaji zuciyarta tafi karkata ga wannan hoton dataga yana kallo, tabbas tasan birgeshi sukayi shiyasa ma yake kallonsu, idonta a cike tab da ƙwalla tasa hannunta akan hoton batareda tayi magana ba.

Shiru yaɗanyi kimanin 3mins sannan yace "da kyau amma kin iya zaɓe, nan da nan ya shiga tura musu kuɗaɗen kayan zuwa Asusun Companyn, seda ya gama tsab sannan taga farashin kuɗin kayan har kimanin Million 3 iya gado da kujeru kawai,

faɗawa tayi jikinsa a ranta tana mai girmama sanin ya kamata da kuma karamci irinna yaya Golden, dukda cewar taƙishi ta zaɓi wani Akansabamma sam hakan besa ya canza komaiba a tareda ita, koda ace yanzu zataga mahaifinta batajin ze iya nuna mata so samada wanda Ahalin Alhaji Mahmoud Muhammad sukayi mata.

haɗe Rai yayi sannan ya kalleta yace "ɗagani malama, So nawa zan faɗa miki cewar ki ɗena faɗomin a jiki?karfa ki manta cewar nifa ba muharraminki bane sabida bana cikin jerin waƴanda Shari'a ta yarda kiyiwa hakan,

Cikin kuka da sarƙewar murya tace "amma ai kai yayana ne!

Murmushi yayi mata me kyau sannan ya kaleta yace "tabbas ko duniya zata tashi hakan baze canza matsayinki na ƙanwa a gareni ba, sabida keɗin ƙanwata ce Umaisa.

sautin kukanta ta ƙara sabida bata da wani zaɓin daya wuce tayi kukan a halin yanzu, murmushi ya sakeyi sannan yace "oya tashi kije ki kwanda dare yayi yanzu har kusan 12:00am pa

Kasa miƙewa tayi don haka ta kalleshi tace "don girman Allah ya Khabeer kayi haƙuri , wllh ba laifina bane ƙaddara ce tazo da hakan amma na tabb...... "Tashi ki tafi kije ki kwanta pls, Khabeer ya katseta a hanzarce.

miƙewa tayi jiki ba ƙwari ta fice daga ɗakin ta koma nata zuciyarta sam babu daɗi, zama tayi a bakin gadonta ta haɗa uban tagumi sekace wadda uwarta ta mutu, ta daɗe a zaune tana aikin wahalar da ƙwaƙwalwarta (tunani) ganin datayi hakan baze wani amfaneta bane yasa ta miƙe ta ɗauro Alwala ta fara gabatar da nafilfili tareda Miƙa dukkan lamarinta ga Allah, tareda rowaƙawa yaya Golden mata ta gari wadda tafita komai a rayuwa, bayan ta gama kwarara masa addu'ar ne ta fara roƙawa kanta da Ahalin Alhaji mahmoud muhammad alkhairin duniya da kuma lahira sabida ɗimbin karamcinsu gareta, se wajen ƙarfe biyun dare wani wahalallen bacci ya kwasheta,

washe gari da sanyi safiya Abba yayi tattaki da kansa har ɗakin Mamie, inda ya sameta a zaune bisa dadduma tana tasbihi ga Ubangijin dukkan halittu (Allah) kallo ɗaya zakayi mata kasan bata cikin kwanciyar hankali, gaba ɗaya idanunta sun koɗe sabida damuwar data sakawa kanta.

zama Abba yayi a kan ɗaya daga cikin kujerun perlourn wanda take facing ɗin fuskar Mamien sannan ya fara magana cikeda dattako kamar haka "Badi'atou kada ki butulcewa Allah mana akan ni'imar dayayi miki, ya baki miji tsahon lokaci batareda wayonki ko dabarar ki ba, amma kuma a ƙarshe seya juya akalar Rayuwarki daga wata zuwa wata, ya kuma azurtaki da juna biyu wanda a zahiri zamu iya cewa shine makullin ƙofar ƙaddararki har yazama silar haɗuwata dake,

"Ashe wannan kaɗai be isa ya zame miki ishara a gameda Rayuwa ba?

tunda har kika iya karɓar ƙaddararki ta farko wadda tafi wannan zafi da ƙunci wannan ce bazaki iya karɓaba Badi'atou?

a matsayina na mijinki ina me baki shawarar cewa karki yarda kiyiwa ɗiyarki mugun furici akan aureta sabida ina jiye miki tsoron karki aikata kuskure irinna Mahaifinki Badi'ah!! A yanda na ɗauki kaina ga Umaisa ni Mahaifine kuma me ƙaunar iyalinsa, Allah ya Azurtani da rainon umaisa har hakan ya zama Rauni na sabida son da nake mata a Rayuwa, wllh ko ƴaƴan cikina bana yi musu irin son da nakewa Mamana (Umaisa) ban sani ba ko hakan yanada nasaba da tarin tausayin yarinyar danakeji ne.

"Badi'atou duk yanda kikeso Khabeer ya Auri Umaisa baki kaini son afkuwar hakan ba, amma kuma se gashi abinda ƙaddara tazo dashi yasa na ɗauki hanun ƴata na miƙashi ga wani a sanadiyar sonda take masa, ko kaɗan ban kasance uba me son kansa ga Ahalina ba shiyasa na barta ta Auri Wanda takeso sabida nagartar iyayensa da kuma ta yaron (Maheer), amma kuma ban sani ba kozaki nuna min iko ne akan Auren Umaisa dana daurane yasa kika kasa yarda da hukuncin dana yanke akanta sabida bani na haifeta ba!!!

Da sauri Mamie ta ɗago jajayen idanunta wanda hawaye suketa faman yimata zarya tunda Abba ya fara maganar girgiza kanta kawai take tana kallon fuskar Abba daƙyar ta iya buɗe bakinta tace " wllh ko kaɗan ba haka bane Alhaji! Taya zan iya aiyana hakan balle har bakina ya furta wannan mummunar kalmar a gareka? Wllh sam ba haka bane ko giyar wake nasha bazan taɓa faɗar hakan ba, ai Umaisa ɗiyarka ce ba tawaba na daɗe da sanar dakai hakan, don haka duk hukuncin daka zartar akanta wllh na amince dashi Allah kuma ya sanya mata dukkan alkhairinsa a cikin Aurenta da mijinta!

Murmushi jin daɗi Abba ya saki sannan yayi mata ƴan nasihu a gameda haƙuri dukda cewar yasan tanada haƙurin, a haka Rayuwar gidan tacigaba da tafiya babu walwala kamar shekarun baya, Sedai ko wannanesu yayi imani da ƙaddaran da Allah ya aiko musu, sedai sam yanzu

Umaisa bata iya sakewa kamar da a cikin ƴan uwnta, wasu lokutan khabeer ne da kansa yake sawa su usman da farouk suyita janta da hira har su dinga kaita yawo wai duk dan ta saki jikinta dasu su koma kamar da.

Yau ta kama Asabar ne, wanda yayi daidai da ranar  komawar Baba Gano, sosai ta jaɗasu a babban perlourn Abba dukansu tayitayi musu nasiha akan Haƙuri da rayuwa, musamman ma khabeer da Ummie inda ta nuna musu cewar Sam karsu taɓa bari wannan al'amarin Daya faru ya taɓa zaman lfyansu da juna, suyi haƙuri su manta da komai, nan suka amsa mata cikeda girmamawa,  nan aka cigaba da wasa da dariya a tsakaninta da jikokinta maza, kafinta tafi haka ta dinga jan Umaisa da tsokana har seda ta saki jikinta kamar da sannan tayi sallama dasu driver ya ɗauketa zuwa kanon Dabo.

*_ƁANGAREN MAHEER KUWA_,* sosai hankalinsa ya kwanta ya ƙara wani irin haske fiyeda yanda yake a da, komai na rayuwa yana tafiyar masa yanda yakeso tamkar ba maheer ɗin da Ya haɗu da jarrabawa ba, wani irin son umaisa yakeji a kowace daƙika na rayuwarsa Yana ratsa gaboɓin jikinsa, sometimes har mamakin kansa yakeyi akan irin muguwr ƙaunar dayakewa yarinyar, tunda yake a rayuwarsa betaɓa jin yanayiwa wani mahaluki irin sonda yake mata ba idan aka cire momy da Dadynsa (iyayensa)

wani kyakkyawan murmushi ya saki wanda ya ƙarawa fuskarsa kyau gamida kwarjini tareda zaro wayarsa ƙirar Samsung ya shiga kiran matar tasa (Umaisa) bugu biyu  aka amsa kiran cikin wata baƙuwar murya me tarin amo a cikinta wadda ya tabbatar da cewar bata Queen ɗinsa bace.  Shiru yayi kamar bazece komaiba, don haka Ruman tayi murmushi me sauti tace "kayi haƙuri surukina amaryan tana sallah ne amma da zarar ta idar zata kiraka.

se'a lokacin Maheer ya sauke wata nannauyar ajiyar zuciya batareda yace mata ƙalaba ya kashe wayar sabida tsabar miskilanci irin nasa,

Tana idarwa Rumana ta miƙa mata wayar tana murmushi tace "wannna angon naki wllh seke Umaisa gabaɗaya bashida sakin jiki da mutane muskilancinsa yayi masa yawa ta yanda har a wayama yi yake, niko zanso na ganshi a zahiri ta yanda zan samu damar nazartar halayensa gaba ɗaya.

Dariya Umaisa tayi sannan tace "tabdi lallaikuwa a kwai tarin aiki a gabanki indai har halaiyar Maheer zaki nazarta.  Shiru sukayi sabida ƙarar wayar data gauraye ɗakin, tin kafin Umaisa ta amsa wayar Ruman tayi ta kanta tabar ɗakin, sabida a cewarta wai masoya suna buƙatar sirri a tsakaninsu (ba irinsu MOMYN FADYL ƴan sa Eyes ba😂😂)

A nitse ta amsa wayar da sallamah, wata uwar ajiyar zuciya ya sauke sekace irin yaron dayaci kuka ya godewa Allah ɗinnan, nan sukaci gaba da hirarsu me cikeda wani Irin sirri a cikinta wanda ni kaina na kasa nazarta shauƙin dake taredasu balle harna fassarashi, wata irin shaƙuwace a tsakaninsu me wuyar misali balle har ayi kintacenta. Umheer kenan Maƙura a

gurin shaƙuwa da kuma nuna ƙaunarsu ga juna❤

Maheer yay shiru sannan yace " Queen kinsan wani irin so nake miki kuwa?

Queen kinsan yanda nakeji a gamedake kuwa?

Da sauri ta girgiza kanta tamkar yana kallonta tace "a'a!

Murmushi yayi me sauti sannan yace "wani irin sihirtaccen so nake miki wanda bazan iya ta'allaƙashi da so ba sedai kawai in kirashi da ƙauna, wllh ƙaunar danake miki a cikin jinina take yawo tayanda ma nakeji cewar I can't express it to anyone, nikaɗai nasan menakeji a zuciyata a gamedake, abinda na sani kawai *KE ALHERICE* a rayuwa ta kamar yanda *MALIKHA MALIK* ta zama a cikin Rayuwar *ACP SALEEM KHABEER KUMO,*  jikin Umaisa ne yay masifar sanyi don haka ta gyara zama tace " Jaan waye kuma *Acp Saleem Khabeer kumo?*

Murmushi ya sakeyi kamar tana kallonsa sannan yace "wani abokina ne wanda ya gina rayuwar aurensa akan ƙudirin fansa akan wata matashiyar yarinya mejida kuɗi gamida izzah, sabida kawai ta mareshi akan wani banzan ƙudiri nata, a ƙarshe kuma reshe ya juyeda mujiya😂

Dariya sosai Umaisa tayi sannan tace "amma naji daɗi daya faɗa tarkon malikha, amma gaskiya nikam zanso jin ƙarshen labarin *MALIKHA MALIK da ACP SALEEM KUMO,* murmushi maherr yayi sannan yace to Queen ki nemi *JAMEELAH UMAR JANAF* na tabbata tanada cikakken labarin seta siyar miki ki karanta kiji meya faru a tsakanin rayuwar mutum biyu *(Saleem da Malikha)* Saleem da kansa ya yarjewa janaf ɗin kan cewar ta rubuta labarinsu daga farko har ƙarshe ta yanda ze yaɗu a duniya kamar yanda labarin *MUZAFFAR DA RABI'ATOU* ya zagaya duniya a cikin littafin  *(BAFULATANA)*

Shiru tayi tana sauraronsa a hankali ta buɗe baki tace " JAAN!! ashe ka iya bada labari irin haka?

murmushi yayi mata sannan yace "na iya bayarwa amma wa kekaɗai kawai Queen.

Murmushi sukayi gaba ɗayansu sannan sukayi sallama da juna inda Maheer ya alƙawaranta mata cewar gobe zezo ya ganta da yardan Allah sannan kuma zatayi masa jagora zuwa cikin gidansu danya gaisa dasu Ummie da kuma Mamienta.

sosai tayi farin ciki da maganarsa ta ƙarshe dayace zezo ya gaidasu Ummie, sabida a Rayuwarta tana masifar martaba Ahalinta, a haka sukai sallama da juna cikeda tsantsar ƙauna gamida Aminci.

_*🎀KIYARDA DANI...!🎀*_
🎀🐾🎀

*♝ IᗪTɘ||IƓɘᗪT WrITɘr'ى ASSฒ📚✍️*

*💫DEDICATED: to Sis naja'art*

_*WRITING BY: Zm (CHuBaƊo)*_

*✨Special Gift for Hafsat Hafnan (my jika),.*

_Page:41_

____________📖 Bayan Maheer ya kammala wayar miƙewa yayi ya shiga cikin gida zuciyarsa fess, yareda ƙudutawa kansa cewar gobe dole ne ya gaiyaci Abokinsa Mujaheed maƙocinsu Umaisa yayi masa rakiya zuwa cikin gidan surukan nasa dan baze iya zuwa shikaɗai ba, a perlour ya sami Abdul sanye cikin wasu Ash colour ɗin kayan spot irin masu dogon wandon nan kunnensa a manne da wayarsa ƙirar iphone, taɓe baki Maheer yayi tareda sakin masa duka a saman kafaɗarsa na dama, kwaɓe fuska Abdul yayi kamar zeyi kuka yace "waiyyo Dadaji kinga wannan angon me saurin hannu ko?

Dariya yayar mahaifin nasu tayi daga cikin wayar sannan tace banishi mu gaisa da maheer ɗin, ba musu Abdul ya miƙa masa wayar se faman cuna baki yake tareda susa inda Maheer ɗin ya dakeshi.

Cikeda girmamawa maheer ya shiga gaida Dadaji, da sakin fuskarta ta amsa gaisuwan tareda yi masa jajen abinda ya faru a kwanakin baya, shafa kansa yayi yana murmushi a lokacin data tambayeshi ina Umaisa Amarya? Shiru yayi ya kasa bata amsa sabida wata irin kunyarta dayakeji, a haka sukai sallama ya jefawa Abdul wayanshi,

Kallonsa Abdul yayi sannan yace "ya Maheer when zaka kaini naga Auntyna ne don Allah?

Batareda Maher ɗin ya kalleshi ba yace "se sanda ta tare a gidana tukunna zaka ganta. Zaro ido Abdul yayi sannan ya dawo kusa da maheer ɗin yace "oh nagane muninta ne yayi yawa shiyasa bakaso na ganta dan karna ma dariya ko? Whatever koma yayane tayi sa'a tunda har ta samu nasarar Auren sadaukin yayana, ƴa faɗa yana yatsina fuska kamar wani ɗan yaro.

Hararar shi maher yayi sannan yace "ai wllh Queen tafika kyau nesa ba kusaba yaro, idanma kana ganin wasa nake ai wata rana zakanta kaida kanka zaka fahimci she's so cute wllh. "Oho dai inba tsoroba a kaini in ganta gobe mana, inyaso se'a gwada a tsakanin nida ita, Abdul ya katseshi ta hanyar faɗar hakan,

Murmushi yayi wanda ya ƙarama fuskanshi kyau yace "nika dameni wllh da yawan surutunka boy dama nasan nace Dady ya tisaka ku tafi yolan tare kaidasu Baffa Giɗaɗo.

Tabe baki Abdul yayi sannan yace "oho ɗai nasan dannace nafi waccan matan naka kyaune yasa kace na dameka, ai kaima kasan gaskiya kafin a samu handsome kamana se'an shirya, inba tsoroba kabari inyi wanka nashafa powder muje a gwada ma...... Nifoshi maher yayi a sikwane yana faɗin tunda kai ɗan daudu ne ai senaji, da wani mugun gudu Abdul yabar perlourn yana dariya.

Washe gari kamar yanda Maher ya sanar da Umaisa zuwansa, don haka ƙarfe huɗu da rabi ya faɗa toilet yayi wanka, haka kawai yakejin zuciyarsa cikin wani irin yanayi wanda ya kasance baƙone a gareshi, a gaggauce ya kammala shirinsa ya fito perlour yana gyara zaman hular dake kansa, a perlourn sukayi kaciɓus da Abdul yana gyara zaman Agogon Rolex ɗin dake hannunsa, idan ka kalleshi seka rantse ba wannan Abdussalam ɗin bane Rainon Maheer Lamiɗo, sosai kamalarsa da haibarsa suka baiyana tamkar ba yaro ɗan shekara 21 ba, sanye yake cikin wata brown ɗin shadda anyi mata ɗinkin jampa, sosai kayan ya karɓeshi tareda fito.da ainihin skin colour dinsa (launin fatarsa).

wani irin kallon Mamaki Maheer kebin Abdul ɗin dashi wanda yafi kamada na mamaki yace "kai where are you going too naga kanata wani gyare-gyaran wristwatch eh?

Taɓe baki Abdul yayi da irin salonda maheer ɗin yayi tambayar sannan yace" i don't know but I'm going to somewhere to see my brother wife Umaisa.

Wata uwar dariya maheer yayi sannan yace " your not serious boy, amma ina tabbatar maka da cewan ba inda zani dakai sedai ka nima wanda zakabi bani ba, murmushin Rashin damuwa Abdul yayi sannan yace "oh nagane tsoro kakeji kada kaje dani ta gane nafika kyau ?? Kaga yaya Maheer karka damu ai ban shafa powder ba bazataga kyauna sosai b..... Kasan Allah barani dakaiba seka zauna a gida kaita kallon kyan naka mumuna kawai.

Kwaɓe fuska Abdul yayi kamar zeyi kuka yace "im so sorry yaya heer amma nidai kam sena bika naga my Aunty, dariya yaso yabama maherr ɗin dan haka ya kama hannunsa suka fice zuwa parking lot, wannan black Range Rover ɗin na maheer suka shiga, nan da nan lawan me gadi ya wangale musu get suka fice daga gidan suka ɗauki hanyar Zone E Apo Legislative Quarters. a bakin ƙofar gidansu Mujaheed sukai perking kallon maheer Abdul yayi sannan yace " amma dai ya Maheer ba shiga zamuyi ba ko? Wllh nasan muka shiga se mamansu ya mujaheed tace na ƙara girma tasa wannan yarinyar me kan kwakwa ta raina ni.

dariya maheer yayi me sauti sannan yace"ai ba ƙarya tayi ba har yanzu kai yaro ne kuma shagwaɓaɓɓe ma kuwa, haɗe rai Abdul yayi batareda ya qara cewa komai ba sabida haushi, a haka mujaheed ɗin ya ƙaraso ya wajen motar shaheeda na biye a bayansa, da sauri Abdul yayi ƙasan sit ɗin motar dan karta ganshi, shi'a dole karta rainashi, har bakin motar ta ƙaraso kanta a lulluɓe da wani siririn mayafi wanda ya baiyana tsintsiyar wuyanta waje, dukda kasancewarta ƴar 17years tanada gogewa da kuma shegen wayon tsiya, da gaiya maheer ya sauke glass ɗin ɓangaren ɗa Abdul yake, zaro ido mujaheed yayi sannan yace "kai wa nake gani kamar Maheer

boy?

Da sauri shaheed ta matso jikin motar sosai ta leƙa wata irin dariya ta saki tareda tafa hannu tace " lah yaya maaheer wannan ɗan lukutin ƙanin naka mara ƙarfin nan ne ya zama babban saurayi haka ?

Wani malolon takaici ne ya tsayawa Abdul a wuya, a ransa yace "wannan shegiyan yarinyan batada mantuwa, amma a fili kuma seya dake yaƙi cewa komai shi'a dole ze tsare gida😂,

Bece mata ƙala ba harta gam asurutunta tabar gurin, shidai mujaheed da maheer babu abinda suke se dariya, nan da nan Maheer ya cinna kan motar zuwa ƙofar gidansu Umaisan, wangalemusu get ɗin Me gadin yayi Sannan suka kunna kai zuwa ciki, a nitse yayi perking motar zuciyarsa fess gamida ɗaukin son ganin Habibiyar tasa, yau komai nasa na musamman ne hatta adon daya ɗauka abin kallo ne ga kowa, abinka da  kyakkyawan mutum kuma farin fata, sanye yake cikin wata dakakkiyar shadda gizna Ash colour (Ruwan toka)anyi mata ɗinkin Muhammed,

Sosai kayan ya karɓi dirarren jikinsa yayi masa ɗas tamkar tare aka halicci jikin da kayan, hular dake kansa se faman ƙyalli take tana yararin tsada, a takaice dai da ka ganshi kaga ango, wayarsa ya zaro ya fara ƙoƙarin kiran Umaisan danya sanar da ita zuwansu, cikin sa'a kuwa bugu ɗaya ta amsa da sallamah, wata Ajiyar zuciya ya sauke  a hankali sannan ya sanar da ita zuwan nasu,

Murmushi  tayi sannan Tace "ina zuwa gani nan fitowa 2mints pls,

A nitse suka sauko daga motar kowa tsab dashi suna jiran fitowar tasa, cikin mintunan da bazasu haza 3 ba khabeer ya fito daga Cikin gidan  cikin shigar manya kaya waƴanda suka fitarda kwarjininsa Da kuma haibarsa, kallo ɗaya zakayi masa ka fahimci yayi Rama sosai tamkar wanda ya shekara yana ciwo, sosai fuskarsa tayi wani irin fayau da ita sabida saisayen sajen dake fuskarsa da akayi wanda ya ƙarawa fuskar nashi kyau,

Kallo ɗaya yayiwa maheer ya ganeshi sabida har duniya ta tashi baze taɓa manta mamallakin fuskar nan ba,  cikin wani irin salo na yarda da kai khabeer ya danne zuciyarsa ya nufo inda su maheer ɗin ke tsaye da wani irin murmushi a kwance akan fuskarsa yace " barka da zuwa surikina, tareda miƙa masa hannu, murmushi maherr yayi sannan yace "  Dr.!!

Nan khabeer suka shiga gaisawa dasu abdul da kuma Mujaheed  shida kansa yayi musu jagora zuwa wani ƙayataccen perlour wanda aka tanada dan baƙi na musamman.

Seda suka ɗan taɓa hira kaɗan sannan Khabeer yayi musu sallama ya fitah sabida a kwai abinda zeje ya gabatar a Hospital ansu.

Cikin min tuna kaɗan Rumana ta shigo perlourn hannunta a ɗauke da wani babban faranti

wanda aka cikashi da kayan motsa baki, sanye take cikin wata Royal blue ɗin jallabiya wadda tayi matiƙar karɓan jikinta, bakinta ɗauke da sallama Gaba ɗayansu kallon ƙofar suke tareda answer sallama ɗin nata ko wanne da murmushi a fuskarsa saɓanin maherr wanda keta faman latsa-latsen wayarsa, a haka harta ƙaraso inda suke ta ajiye farantin, da sakin fuƙa tace "lah ya Mujaheed hardakai a rakiyar angon namu?

Dariya mujaheeda yayi sannan yace Rumana yayar Amaryar maheer se'a lokacin Maherr ya ɗago ya kalleta a time ɗin da ita kuma Ruman ɗin ke kallon Abdul suna gaisawa, cikin sa'a kuwa tana juyowa suka haɗa ido da maheer wanda shima ita ɗin yake kallo, da sauri tayi ƙasa da idanunta sabida wani irin mugun kwarjini dayayi mata a ido, a daburce tace "in....ina yi..ni?

Da sakin fuska ya amsa mata sannan ya ɗauke idanunsa daga kanta,  bata sake cewa komai ba  ta miƙe tabar perlourn da sauri,  donta turo musu Umaisan. A ranta kuma tana jinjina kwarjinin wannan miji na Umaisa, yanzu duk nazarin halaiyarsa datace zatayi sun tashi a banza kenan? Ajiyar zuciya ta sauke me nauyi sannan zuciyarta tace mata" taya zaki iyayin hakan bayan gashi tundaga kallon farko da kikayi masa kika kiɗime da kwarjininsa.

a hkaa ta isa perlour ta samu Ummie ta sanarda ita zuwan surukin nasu, murmushi Ummie tayi sannan tace "masha Allah munayi masa maraba da zuwa tun kafin ya shigo ciki, kiyi sauri ki shiga ki fito da ita nasanta da shen shirita karta ɓata masa lokaci.

dariya Ruman tayi sannan tace "ummie ai bashi kaɗai yazo ba ma shida abokinsa yaya Mujaheed sukazo, da kuma wani me kama dashi ina zaton ma ƙaninsa ne.

zaro ido Ummie tayi sannan tace "ke Rumana na rabaki da irin wannan halin ta ina kikasan ƙaninsa ne bayan bashi ya gaya miki hakan ba?

dariya tayi sannna tace "wllh Ummie bakiga yanda suke kamaba, dana kallesu ma ni na kasa gane wanda yafi kyau a tsakanin....... "Dalla rufewa mutane baki mamie ta katse Ruman tana binta da wata Uwar harara tace "tomu ina ruwan mu da kyansa?

Dariya Ummie tayi sannan tace "oh Allah Badi'atou har yanzu baki dena taya ɗan naki kishin bane ?

shiru tayi bata tankaba ta koma kitchine abinta tana ta faɗa.

dafa Rumana Ummie tayi sannan tace "oya maza kije ki fito da ita nasan tsoron fitowa take sabida bala'in faɗan Badi'atou.

da sauri Rumana ta nufi ɗakin Umaisan,  a zaune ta sameta ta haɗa uban tagumi, kallo ɗaya zaka mata ka fahimci a tsorace take, dariya Rumana tayi sannan tace "dalla meye haka kin bar mutane sunata jiranki?

Narai-narai tayi da ido kamar zatayi kuka tace "Ruman tsoro nakeji sabida har yanzu Mamie na fishi take dani, miƙar da ita Ruman tayi tsaye sannan ta zaunar da ita a gaban mirror ɗin dake ɗakin, nan da nan ta gyara mata fuskarta  ta fito tayi Rass da ita,  wata haɗaɗɗiyar jallabiya ta ɗakko mata wadda abba ya siyo mata a Dubai Maroon colour ta wadda aka ƙawata da fararen stone's masu masifar haske da ɗaukar ido ta miƙa mata, ba musu ta karɓa ta sanya a jikinta,

sosai tayi kyau kamar a saceta a ɓoye, dayake mayafin rigar yanada ɗan girma sosai Rumana ce tayi mata Rolling nasa, wow abindai se wanda ya gani abinka da farar mace, takalmi Rumana ta jawo mata shima flat dashi ta saka sannan taja hannunta suka fita zuwa sit Room ɗin.

_*🎀KIYARDA DANI...!🎀*_
🎀🐾🎀

*♝IƊƬЄ𝕃𝕃IƓЄƊƬ WяIƬЄя'ی  ASSɷ📚✍️*

*💫DEDICATED: to Sis naja'art*

_*WRITING BY: Zm (CHuBaƊo)*_

*✨Special Gift for Hafsat Hafnan (my jika),.*

*_A yau ina miqa tarin godiyata gareki Sadiya sidi (sidiya the writer of BINAFA) Akhairinki gareni me girma ne, haka kuna banida bakin dazanyi godiya a gareki SIDIDIN CHUBAƊO, wllh ina alfahari dake ɗari bisa ɗari don haka na Mallaka miki wannan shafi halak malak har duniya ta tashi mallakin ki ne sidiya ta😁_*

_Page:42_

___________📖A nitse suke takawa har suka iso ƙofar perlourn hannunta a sarƙe cikin na Rumana, A haka suka shiga perlourn da sallama ɗauke a bakunansu, tunda suka shigo idon Maheer nakan Umaisa wata irin ƙaunar ta yakeji tana yawo a jinin jikinsa wadda bayajin ze iya misaltata,

A haka suka shigo Ruman ta zaunar da ita akan kujerar dake facing angon nata, dariya Mujaheed yayi sannan yace "lallai Rumana kin iya ɗaurewa ƙauna ƙafa harda wani zaunar da ita tayanda zasu dinga facing juna?

Murmushi tayi a kunyace sannan tace "a'a yaya mujaheed nidai ba ruwana kawaidai na sauƙaƙewa angon hanyar  daze kalli amaryarshi cikin sauƙine.

Zaro ido Abdul yayi sannan yace "oh nagane kenan ke connecter ce ta masoya?

Dariya sukayi gaba ɗayansu har Maheer ɗin, kallon Umaisa Abdul yayi sannan yace "amma wannan amaryar kin iya siddabaru, meyasa kika saka kaya kalar nawa? Nidai bari kiji na faɗa miki duk abinki wadda ta fiki kyau zan Auro sabida nafi mijinki kyau da komai.

Dariya sosai maheer ya keyi kamar ba wannan miskilin matashin ba, ita kanta Umaisa seda ta ɗago ta saci kallonsa kaɗan sannan ta maida kanta ƙasa, maherr "yace Mujaheed kanajin yaron nan ko?

Murmushi mujaheed yayi sannan yace "aida gaskiyarsa ko ƙanina ? Abdul ya ɗaga kai yace sosai kuwa ya Mj,

Miƙewa Abdul yayi ya canza gurin zamansa sannan ya kalli Umaisa yace " ni bantaɓa ganin amarya irinki ba wllh se faman sunkuyar da kai kikeyi sekace kazar datake tsoron yanka, kodai kinajin tsoron ganin fukata ne dan karkiga nafi mijinki kyau ne?

Ɗagowa Umaisa tayi ta saci kallon inda su Maherr suke cikin sa'a kuwa ta fahimci ba ita suke kallo ba sannan ta ɗago ta kalli Abdul ɗin sosai tace "ina koda wasa mijina yafika kyauda komai, don haka ka ɗena haɗa kanka da mijana ɗan samari.

Dariyace ta kama kowa dake perlourn ciki kuwa harda Rumana wadda ke gefan Umaisa, shima kansa Abdul ɗin dariya yakeyi sannan yace " yanzu kam na yarda zaki iya kularmin da yayana tunda har kika iya mayar min da wannan martanin, a haka hirar ta tashi Abdul na cikasu da surutu.

A nan Rumana da Umaisa sukayi musu jagora zuwa maine perlourn gidan suna biyeda su a bayansu, da sallama suka shiga perlourn dikansu hakanne yayi daidai da fitowar Farouq perlourn shima, kallonsu kawai yakeyi a zuciyarsa yana mamakin ƙannen nasa da kuma yanda akai har Umaisa ta iya kallame zuciyar wannan koɗaɗɗen mutumin a cewarsa lol, amma kuma a zahiri seya ɗan saki fuskarsa sabida ganin Mujaheed dayayi a taredasu, hannu ya miƙa musu suka gaisa sannan ya haye sama zuwa ɗakin Mamah,

A nan ma Abdul beyi shiru ba se faman kwasar Umaisa da Rumana yake kamar wasu kakanninsa yana dariya, Mamie dake Kitchine tana haɗa Abincin dare duk tana jinsu a Ranta tace "kai wannan Yaro a kwai shegen surutu sekace kenari.

Cikin mintuna da bazasu kaza 3 ba Ummie ta sakko perlourn sanye cikin wani dogon hijjabi milk colour, da fara'a kwance a fuskarta wadda take nuna ainihin murnar ganin surukin nasu, a haka Mama ma ta sakko itama cikin shigar mutunci kamarta Ummie, nan da nan su Maheer suka zube suna kwasar gaisuwa a wajen surikan nasa wanda yaji har A ransa cewar sun kwanta masa, Ummie tayi.murmushi tace "Mujaheed yau kaine a gidan namu albarkacin babban

surikinmu ko?

Wata irin kunya Mujaheed yaji sannan yace "wllh Ummie ba haka bane aiyukane kawai sukamin yawa shiyasa ban samun lokacin ziyara, murmushi Mama tayi sannan tace " yakamata dai a dinga daurewa ana yin ziyarar yafi.

"insha Allah zan ƙoƙarta Mamah, wai ina Mamie ne ban ganta ba?

miƙewa Ummie tayi  tace "tana kitchine barin mata magana.

Ummie na fita Usman yana shigowa hannunsa ɗauke da briefcase ɗinshi inda ɗaya hannun nasa kuma  ya riƙo Rigar saman suite ɗin dashi, kallo ɗaya zakayi masa ka fahimci a gajiye yake, a haka ya ƙaraso perlourn da murmushi dukda cewar besan su waye a perlourn ba, zubewa yayi akan ɗaya daga cikin kujerun perlourn sannan suka shiga gaisawa dasu maheer ɗin,  kallon Mamah Usman yayi sannan yace " Mama sannu da gida baƙi mukayi ne haka?

murmushi Mama tayi sannan tace "ai waɗannan ba baƙi bane ƴaƴa ne, mijin cry-cry ɗin Abbane yazo gaisuwar surukai.

kallon Umaisa Usman yayi sannan ya miƙe ya nufi inda take zaune ya wani watse mata kunne, lokaci guda ta saki ƙara tana kiran Abba, dariya Usman yayi sannan yace "wayace kiƙi faɗa min zuwan nashi eh??

to idan baki saniba ma to dani aka bada Aurenki nine nan waliyi a matsayina na yayan Amarya.

dariya Mama tayi sannan tace "kunfi kusa kaida ita indai Umaisa ce bame shiga tsakaninku yaji kunya.

Dariya Ruman tayi sannan tace "yauwa mamah Ashe kin kuwa gane, indai yaya Usman ne sunfi kusa shida ita.

Dariya yayi sannan yace "to azugwai kar dai kisa in saki layi a gaban surikin ƙanina.

Zaro ido Ruman tayi sannan tace "kai yaya Usman manyance.

Dariya kawai Abdul da mujaheed keyi shiko maheer sedai Murmushi kawai yakeyi a ransa yana misalta barkwanci irinna Usmsn,

se'a lokacin Usman ya maida kallonsa ga Abdul, lokaci guda kuwa ya shaidashi don haka yace "wa nake gani kamar cry-cry ɗin abokina na Sushmer Hospital?

Dariya sosai Abdul yayi sabida shina ya ganeshi sarai sannan yace "oh gaka kaikuma baka mantuwa kamar wannan surikin naku, ya faɗa yana nuna maheer da hannunsa,

dariya sukayi gaba ɗayansu nan suka shiga hira dukda cewar maheer ɗin be wani saba da Usman ɗin ba amma haka kawai seyaji ya kwanta masa a ransa,

maheer ya kalli Usman yace Amma senake ganin kamar da gajiya a tareda kai ko?

murmushi yayi tareda sassauta necktie ɗin dake wuyansa yace "Hmm kaidai bari, wllh yau har abinda yafi gajiya ma nayi, wani aikine yasha kaina a office wanda yasa gaba ɗaya naji na sare da al'amarin, seda nasha wahala sosai.sannan  kuma daga baya nasamu nasarar kammalawa. mujaheed yace "ai dama indai mutum baya koɗuwa a office baya sanin mahimmancin aikinsa inji momyna,

murmushi Usman yayi sannan yace "hajiya momy ai kodan ta tsokaneka zata gaya maka haka mujaheed.

A haka sukaita tattaunawa akan abinda ya shafi harkan aikin Usman ɗin.

Ɓangaren Ummie kuwa babu yanda batayi da Mamie ba ta fito su gaisa amma fir mamie taƙi yarda har seda Ummie tayi fishi ta fita tabarta a kitchine ɗin ta koma perlourn,   duk abinda mutanen perlourn ke faɗa Mamie tanaji kamar a kitchine ɗin suke hirar,  idan suka faɗi wani abin sedai ta taɓe baki wani kuma tace "hm a haka su Ummie suka dinga hirarsu gwanin shi'awa,

Usman kallon Ummie yayi sannan ya karya kai yace "Ummie na baki min oyoyo ba fa,

Daƙuwa tayi masa tana harararsa, kallonaheer yayi yace "kaga Ummie nan ko kullum haka muke fama da ita sam bata bani seaport.

dariya ummie tayi tana kallonsa, sabida inda sabo yaci ace ta saba da  shakiyancin Usman,

Charaf Abdul yayi yace "Eyyah aboki nima haka nake fama da wannan ya nuna maheer sannan yaci gaba da cewa "sam nima baya bani seapo..... "Amma ai kanema ka samu yafi ka rasa mahimmanci boy. Maheer ya faɗa yana murmushi.

kofin glass ɗin dake hannun Mamie ne ya faɗi ƙasa a lokacin dataji sauƙar wannan kalmar a kunnenta, nanda nan idanunta suka fara wata irin yana wanda hakan ya haifar mata da ɗaukewar ganinta na wucin gaɗi,  cikin wani irin fitar haiyaci ta taka glas ɗin fasashshen kofin dake gabanta ta nufi perlourn har tana karo da ƙofar kitchine ɗin,

Tana fitowa perlourn tayi ido huɗu da maheer. Cikin sassark'ewar murya da rud'ani take nuna maheer da ya tsaya, bakin ta har rawa yake wajen furta...

"wan .. wan.. wannan way?????

Maheer da hankalin shi ke kan wayar da aka kira shi minti biyu daya wuce, ya d'ago dan ganin me Kiran nasa. Waigowar da zeyi suyi Ido hud'u da mamie.
Tsananin rud'u da firgici ne had'i da tsoro ya mamaye mamie, saboda abunda idanuwan ta ke gane mata a yanzu. tsabar kaɗuwa lokaci guda mamie ta sulale ƙasa sumammiyah.

A lokacin da maheer ke kokarin tantance mamie, inaaah! Ai har takai k'asa.

gaba ɗaya ilahirin jama'ar dake parlour - n suka furta

Innanillahiwa'inna'ilaihirraji'un!!!!! A tare sukayo kanta

Hankalin kowa yayi matuk'ar tashi over, baran ma umaisa, ummie da Ruman. Har rige-rigen kai wa inda mamie ta fad'i k'asa suke yi.

Jijjiga ta suka shiga yi, suna furta

"mamie!!! Mamie!!! ". Cikin yanayi me nuna Tsananin tashin hankali.

Ummie ce tayi hanzari tashi ta shiga kitchen, ta d'auko ruwan roba, ba shiri ta shiga antaya wa mamie su a fuska, Amma ba alamar zata farfad'o.

A b'angaren Maheer kuwa ya kasa Gano komai, gashi yana so yaga fuskar mamie Amma hijabin ta ya rufe mata fuska, Wannan ne ya kasa bashi daman tantance ta. Gaba Ki d'aya kowa ya shiga shock, kan kowa ya tushe.
Kallon tuhuma samarin suka fara bin maheer dashi alamun suna buk'atar Jin daga gare shi, ganin Wannan baze fish-she suba yasa kabiru furta

"ummie ku d'auko ta, kusa ta a mota muje asibiti"

Toh! Shine kawai abunda ummie ta iya furtawa, cikin hanzari ta ta mik'e, da taimakon kabiru suka tallabi mamie suka saka ta a mota, sauran jama'ar kuma suka bi Bayan su a motar maheer.

Motar su Usman da faroug ce ta fara tsayawa, kafin tasu maheer su iso, har an fiddo mamie a mota, a shiga da ita, kai tsaye emergency aka wuce da ita, saboda yadda jikin ya tsananta.

A tare maheer, Abdul da mujaheed suka fito daga mota, dikkan su cikin Tsananin damuwa, cikin Asbitin  Waige-waige suka tsaya yi  Cikeda son su Gano inda aka bi da mamie,

 Khabeer suka hanga  ya rufa wa wasu nurses baya da suka gunguro injin oxygen, cikin tsananin zafin nama gamida bajinta khabeer ya dasa mata oxygen ɗin cikeda fafutikar son ganin ya samu daidaituwar numfashin ta.

Basu yi Wata Wata ba suka bi Bayan su suma, cikin kid'ime wa...

Cabdi! Ana wata ga wata🤔  masu karatu ku biyomu  a cikin Shafi na gaba dan Jin yadda zamu warware muku Wannan sark'ak'iyar...

_*🎀KIYARDA DANI...!🎀*_
🎀🐾🎀

*♝ IÐTɵ||IƓɵÐT WrITɵr'ى  ASSɷ📚✍️*

*💫DEDICATED: to Sis naja'art*

_*WRITING BY: Zm (CHuBaƊo)*_

 *✨Special Gift for Hafsat Hafnan (my jika),.*

_Page:43_

___________📖 Koda suka shiga Reception ɗin guri suka samu suka zauna kamar yanda sukaga su ummie sunyi,  jigun-jugum sukayi aka rasa wanda zece ƙala ko wanne da abinda yake saƙawa a cikin zuciyarsa a gameda ciwon na mamien,

Suna cikin haka Abba ya ƙaraso cikin Asbitin cikeda tashin hankali Shima, babu abinda yake ƙara ɗaga masa hankali dayi masa yawo a kunnensa tamkar an kunna ansa kuwa  kamar maganar Dr. Abbas muhammad ta ƙarshe daya gaya masa, kan cewar muddin suka sakeyin sake ciwon  Mamie ya sake tashi tofa zasu iya rasata! Sabida yanda matin ciwon nata yakai,

Kasa magana yayi balle harya samu ƙarfin gwiwar tambayar menene maƙasudin faruwar hakan,  ƙarfin hali kawai Abba keyi dan haka a daddafe ya iya gaisawa dasu Maheer wanda yakewa kallo a matsayin suriki.

Seda suka shafe awa biyu cur sannan suka samu nasara wajen daidaituwar numfashinta ya

dawo dai-dai,

Allura suka kafa mata wadda zata sanyata dogon bacci sabida ta rage mata damuwa,  sannan zaratan likitocin guda uku suka fito fuskarsu a ɗauke da murmushi na musamman wanda ke baiyana alamar nasarar da suka samu.

Gabaɗayansu office ɗin Dr. Viru suka wuce, wata matashiyar nass ce ta tsaya a gurinsu Abba ta sanar dasu cewar an samu nasaran shawo kan matsalar mamien don haka Dr. Voru  yana buƙatar ganin Abba a office ɗinsa yanzu,  tun kafin Abba ya iso ƙhabeer ya fito daga office ɗin yana ƙoƙarin zare hanglove din dake hannunsa,  kacibus sukai da Abba wanda ke ƙoƙarin shiga, murmushi khabeer yayi sannan yace "Abba no need ma ka shiga, kawai ka faɗama su ummie su wuce gida insha Allah komai zeyi daidai tunda yanzu mun gano bakin zaren komai.

Wata nannauyar ajiyan zuciya Abba ya sauke sannan yace "to Amma dai babu wata matsala dai ko a tareda Badi'atoun?

Ɗaga masa kai khabeer yayi tareda bashi tabbacin hakan.

Nan suka ɗinguma da Abba da khabeer ɗin zuwa indasu Ummien ke zaune, basu wani sha wahalaba khabeer yayi musu bayanin komai cewar jikin mamien da sauƙi  tunda har gashi an samu yanxu tana bacci.

Ajiyar zuciya duk suka sauke a tare tareda furta kalmar godiya ga Allah, sannan suka miƙe sabida sanin cewar Asbitin ba'a buƙatar me jinya.

A  harabar Asbitin mujaheed yayiwa maheer sallama yabi su  Usman suka kama hanyar gida tunda anguwansu ɗaya ne,

A motar ma jikin Abdul a matiƙar mace yake cikeda damuwa ya kalli maheer yace "ya maheer wai me yake shirin fariwa ne haka?

"ni wllh jikina yayi sanyi sosai da ganin irin condition ɗin da matar nan take ciki! Ni babban abinda ma yafi bani mamaki guda ɗaya ne da matar, yanda naga tana wani nunaka cikeda jin haushi koma in kira hakan da tsana.

Murmushi kawai maheer ɗin yayi sannan yace nima kaina a duhun nake kamar kai Abdul! Tayanda ma nakejin gaba ɗaya jikina yayi sanyi sabida a sanadina matar mutane ta samu kanta a halin data tsinci kanta a ciki,

Shiru Abdul yayi kamar wanda keson gano wani abin  sannan yace " ya maheer  be kamata mubar Umaisa a halin da muka barta a gidansu ba,  kamata yayi ka zauna da ita kozata  samu sauƙin damuwar dake damunta, wllh ya maheer zuciyata ta kasa nutsu akan halin da mukabar umaisa a ciki, musamman idan na tuna yanda take kuka a lokacin da aka fita da mahaifiyarta

zuwa Hospital!

Shiru maheer yayi tareda zare hular dake kansa yace "ni kaina inajin hakan Boy, sedai babu yanda zamuyi don mu hanata kuka akan ciwon mahaifiyarta, insha Allahu nan zuwa gobe zan koma Hospital ɗin kodan naga halin da mara lafiyan ke ciki.

da haka suka ƙarasa gida zuciyoyinsu duk a dagule.
_*🎀KIYARDA DANI...!🎀*_
🎀🐾🎀

*♝ IᗪTᏋlllGᏋᗪT WrITᏋr'ى ASSฌ📚✍️*

*💫DEDICATED: to Sis naja'art*

_*WRITING BY: Zm (CHuBaDo)*_

*✨Special Gift for Hafsat Hafnan (my jika),.*

_Page:44_

___________📖Washe gari tun da safe Dady yayiwa Maheer waya ya Gaya masa cewar yanada baƙi na musamman waɗanda ze gana dasu a ƙasar Turkey, Dan haka shi baze samu damar zuwaba maheer ɗin ya shiya ya hacci taron bunƙasa kasuwancin na mahaifin nasa.

Babu yadda maheer ya iya dole a Ranar ya shika kimtsawa tafiyar dama besan da itaba gaba ɗaya, bayan ya kammala wayar zuciyarsa babu daɗi ya miki ya fara shirin tafiyar sabida ta nan Abuja se tashi, ɗakin dake kusada nasa ya shiga Wanda a Abdul yake zaune yanzu a ciki, fuskarsa babu walwala Ya nufi gadon da Abdul ɗin ke kwance a kai yanata kwasar baccinsa.

Murmushin mugunta maheer yayi sannan Yasa hannunsa ya matse masa hanci ta yanda baze iya shaƙar numfashi ba, ba shiri Abdul ya buɗe ido da sauri yana turo baki Yace "haba yyaa maheer don Allah! mutum yana baccinsa kazo ka tasheshi.

Hararanshi maheer yayi sannan yace "oya malam tashi ka haɗa komatsanka ka wuce Kaduna, nima kaina gaba zanyi Dady ya turani Qasar ISTANBUL zan wakilceshi akan buƙasa hannun jarinsa a ƙasar, tareda halattar wani babban taro na ƙarawa juna sani.

Firgigit Abdul yayi ya mike zaune tareda dafa kafaɗar Maheer ɗin yace "why ya maheer don Allah?

"sam yanzu be kamata kaje ko ina ba kabar Aunty Umaisa, becouse kai kaɗaine ƙarfin

gwiwanta, nasan yanzu she's so sad Akan halin da mahaifiyanta ke ciki, ni kaina i can't explain how I feel when I seen her mother condition, wllh har muka dawo inajin tausayin maman nata a raina, to ka misalta idan kaine a halin data tsinci kanta taya zaka fara Expressing ma wani ?

Shiru maheer yayi batareda ya iya ce dashi ƙala ba, wata uwar ajiyan zuciya ya sauke sannan ya iya buɗar baki yace " hakane boy, but dukansu suna da mahimmanci a cikin rayuwata, now Umaisa she's my wife but how can't I tell Dady bazan Iya zuwa inda ya turani ba?

"toba gani ba ya maherr ai zan iyayin dukkan abinda ya dace a taron, I will do all my best naga mun cimma dukkan wata nasara da Dady yake fata, nidai babban fatana shine Stay with her and you give her all the happiness she deserves for you, that's all Yaya heer!

Shafa kansa maheer tayi sannan yace "baran iya turaka ba boy, because this meeting is the only oppotunity Da muke dashi, don haka karka damu insha Allah komai zeyi daidai, da wannan maganar hirar tasu ta ƙare sannan Maher ya fita ya koma ɗakinsa tareda kunnan system ɗinsa yayi booking jirgin daze kaishi ƙasar ISTANBUL ɗin,

Tiket ɗin Qarfe goman safe ya damu don haka ko zarafin samun Yin sallama Da umaisan ma be samu ba, sedai yayi ƙoƙarin kiranta amma bata answer kiransa dan dole ya rabuda ita, Abdul ne ya tuƙashi har zuwa air pod, a mota ya kira Abban Umaisa ya sanar dashi uzirinsa tareda tambayarsa jikin mamie.

Da sakin fuska Abba ya amsa masa tareda yi masa Addu'ar alkhairi ta sauka lfy.

Koda suka isa air pod seda maher ya sake jaddadawa Abdul cewar ya tattara ya wuce kaduna Amma fir yace wallh baze tafi ba har se sanda maheer ɗin ya dawo sa koma tare, tareda bashi tabbacin cewar kullum ze dunga zuwa yana duba lafiyar Auntynshi da mahaifiyarta dake Asbiti.

Kallonsa kawai maheer keyi batareda yace dashi ƙala ba ya wuce yabarshi a nan, seda Abdul yaga tashin jirgin nasu sannan ya bar air pod ɗin.

Wannan kenan.

A ɓangaren mamie kuwa sosai jikinta ke ƙara samun sauƙi, a ƙarƙashin kuƙawar Dr. Khabeer da kuna Abdullah, kusan kullum Ruman da Umaisa suna hanyar Asibitin, Don haka Abba ya takawa umaisan birki kan cewar sintirin zuwanta Asbitin yayi yawa, Gidan mijinta zata tattara su kaita Bazema jira maheer ɗin ya dawo daga tafiyar dayayin ba, Garasu tattara ta su miƙata gidanta shi baze iya da wannan zaryan ba, kuka umaisa ta dingayi duk a dalilin maganar da Abba yayi na ze mayar da ita gidan wani.

Koda suka koma gida Abba ya sanar da ummie itama tayi farin ciki sosai, ko babu komai idan umaisa ta tafi gidan mijinta zata samu Hankalin gwarzon ɗanta Khabeer ya kwanta har shima ya fitarda matar Aure tunda yaƙi Beebah.

Da wannan hukuncin Abba ya koma side ɗinsa ya shiga kira wayar Baba donya danar da ita cewar Jibi ze turo Driver ya ɗaukko ta sabida ranar juma'a da yardan Allah za'a kai umaisa gidan Aurenta.

Sosai baba taji daɗin hakan don haka ta dinga sanyawa lamarin albarka tareda yiwa sauran zaratan jikokinta fatan samun mata nagari.

Kamar yanda Abba ya faɗa hakane Kuwa ya kasance, tunda sanyi safiya ya tura Bala Driver ɗinsa donya ɗakko baba daga Gano, Nan ma ba ƙaramin artabu sukai da baban Gano ba wai ita ala dole bazeyi gudu da ita ba, babu yanda Balan ya iya dole yabi abinda baban tace, aiko basu sukakai Abuja ba se ana sallar magrib.

Sosai Umaisa tayi murna da ganin Baba hakama Rumana, su Usman da Farouq kuwa ji sukai tamkar anyi musu mutuwa sabuda zuwan Baban, tsaki Usman yayi wanda ke zaune biya kan Daining yayi tareda ajiye spoon ɗin dake hannuɓsa yace "Oh ya Rabbi!! Shikenan ciwon kai tazo.

Hararарsu Rumana Farouq Yayi sabida ganin yanda suketa faman rawar kai akan Baban Gano, taɓe baki yayi sannan yace "wannan ai ta wuce ciwon kai tunda idan tazo gidan mutane seta addabesu ta hanasu sakat.

Daƙuwa Baba tayi masa sannan tace "Ubanku Mamuda ne addababbe bani ba, tareda wa Ƴannan, ta faɗa Tana nuna su Mama da Ummie dake zaune suma sunacin Abinci,

Ɗakinta ta nufa su Ummie na biye da ita sannan su Ruman, tana zama ta fara tambayarsu ya jikin Badi'atou n?

Murmushi mama tayi sannan tace "ai jikin da sauƙi sosai, wata ƙila ma kiga an sallamota daga Asibitin yau ko gobe, washe baki Baba tayi sannan tace "to masha Allah bari na shiga wanka konaji daɗin jikina tunda har jikin nata da sauƙi, dama Naso senaje Asibitin na dawo sannan nayi wanka naci Abinci.

"Baba waye ze kaiki Asibitin to? Rumana ta tambayi Baban

Mujaddadi Usmanu mana, ta faɗa tana murmushi

Tabb Allah ya sauwaƙe in ɗaukeki a motana, Usman ya faɗa yana Kasa shigo ɗakin Yana ƴar dariya.

Dariya Ummie tayi sannan ta miƙe tace "Baba barina kawo miki abincin nan kafin ki fito daga wankan, da to Baba ta amsa mata tareda sanya masu albarka gabaɗayansu.

_*🎀KIYARDA DANI...!🎀*_
🎀🐾🎀

*♝ IᗪTɵ||IƓɵᗪT WrITɵr'ی ASSѡ📚✍️*

*💫DEDICATED: to Sis naja'art*

_*WRITING BY: Zm (CHuBaDo)*_

*✨Special Gift for Hafsat Hafnan (my jika),.*

*Haqiqa naji daɗi sosai akan irin Tarin qaunar da kuka nunamin akan wannan littafi me taken KIYARDA DANI, Allah ubangiji yabar qauna tareda zumunci me ɗorewa, Sonso Fisabilillah❤*

_Page:45_

__________📖 A kwana a tashi babu wuya a gurin Allah yau tayi daidai da ranar da aka sallami mamie daga Asbiti Sakamakon doguwar jinyar datayi, don haka gaba ɗaya Ahalin Na Alhaji Mahmoud Muhammad suka kaure da Tarin farin ciki da samun Ifiyar Mamien, sedai har yanzu zukatansu a cike suke tab dason sanin maƙasudin shigar Mamien cikin wannan Mawuyacin yanayin data shiga a lokacin datayi arba da surikin nata wato Maheer, sedai babu me ƙwarin gwiwar daze iyayi mata wannan tambayar don gudun sake afkuwar wani abun na daban ga Ifiyar mamien.

Tunda Mamie ta fito daga Asbiti har xuwa yanzu addu'a kawai takeyi Allah yasa abinda idanunta suka gane mata ba gaskiya bane Gizo ne kamar yanda idanunta sukeyi mata a kowace rana, lallai dole ne tayi wani abu guda ɗaya ta haka ne kawai zata tabbatar da abinda take zargi akan abinda idanunta suka gane mata ɗin a tareda Maheer, ajiyar zuciya ta sauke me nauyin gaske wadda taja hankalin Abba zuwa gareta wanda ke kwance rungume da Ameerah wadda ke bacci yace " Badi'atou!!

Ɗagowa tayi tareda maida kallonta ga Abban batareda tace dashi ƙala ba,

A nitse Abba ya fara magana cikda dattako yace "Badi'atou har zuwa wani lokaci zaki ɗauka kina wahalar da zuciyarki gamida addabarta da dogon tunani ne?

"kin sani sanin kanki cewar a halin yanzu condition ɗinki ya tsananta fiyeda na kullum ko? Me kika tanadarwa kanki a gaba da kike ƙoƙarin kashe kanki a banza duk a sanadin abinda kika gina akan zargi?

Kallonsa kawai mamie keyi tunda ya fara magana batareda tace dashi ƙalaba seda ta tabbatar da cewar ya gama faɗar abinda zece sannan tace " Alhaji duk yanda zan gaya maka cewar

nima ba'a son raina nake shiga wannan yanayin na yawan tunani mara amfani ba bazaka taɓa yarda ba,  amma ya kamata ka fahimci cewar nima ɗiyace ga wasu kuma wadda takeda burin gyara alaƙarta da mahaifinta tun kafn mutuwa ta riskeni nasan zakayimin uziri fiyema da yanda nake zato.    Ta faɗa idanunta na zubar da hawaye

Daƙyar ta iya dakatar da kukan dake shirin kufce mata tacigaba da cewa "taya zan kwantar da hankalina bayan na rabuda mahaifina tsahon shekara 20 batareda na sanyashi a idanuna ba? Wllh wannan kaɗai ya isa ya zama ajalina ma ba iya rashin kwanciyar hankali ba!!!!!

Ta faɗa tana sakin kukan data daɗe batayi irinsa ba.

Sosai jikin Abba yayi masifar sanyi, inda kuma wani ɓangare na zuciyarsa yacika da tsantsar tausayinta,  janyota yayi zuwa jikinsa sannan ya shiga rarrashinta da tausasan kalamai masu ratsa zuciya tareda yi mata alƙawarin cewar ze koma yola a karo na biyu kodan ya bin ciko mahaifinta wata ƙila itama ta samu farin ciki kamar kowace ƴa a doron duniya,  da wannan zancen ya samu nasarar shawo kanta  tabar kukan sabida Condition ɗinta.

A hankali Mamie ta zare jikinta daga na Abba sannan ta Miƙe a hankali Batareda tace dashi ƙala ba ta buɗe ƙofar ɗakinta ta fita, a nitse take sakkowa daga kan step ɗin, kallo ɗaya zakayi mata ka fahimci irin Ramar da tayi sakamakon ciwon data kwanta.   Harta gama sakkowa bataga kowa a perlorn ba se Khabeer dake ta faman dannar System, cikeda girmamawa ya gaisheta tareda tambayarta ya ƙarfin jikin nata?

Murmushi Mamie tayi wanda ya baiyana ramar dake tattare da ita sannan tace "jiki Alhamdulillah Babana daga haka bata sake cewa ƙala ba sabida sam yanzu bata iya jurar yin doguwar magana dashi sabida illar da ɗiyarta tayi masa kansa taji kunya yayinda take magana dashi ɗin, a nan perlourn ta barshi ta nufi ɗakin Umaisa wadda tundaga ranar da Abba yabada Aurenta ga Maheer  Lamiɗo ta ɗauke ƙafarta se A yau.

Zaune take bisa gefan gadonta sekace wata munafuka kunnenta ɗauke da wayarta suna hira da Maheer Kamar haka 👇

"ina fatan jikin Mamien yayi sauƙi sosai ko Queen?

Da uhmmm kawai ta amsa masa tamkar an mata dole, gaba ɗaya ji take hirar dukta gundireta, tun daga lokacin da Mamien ta ta kwanta rashin lfy a sanadiyar Ganin  maheer yasa ta canza masa matsayi, bata jin hakan zesa ta tsaneshi sabida wani irin so take masa wanda batajin zata iya misaltashi ga kowani mahaluki a duniya, tafi yarda da cewar a jininta son yake.

Katseta yi  yace "Queen gobe nefa ranar dazamu kasance da juna a ƙarƙashin inuwa ɗaya, shin bakya farin ciki da hakan ne?

Fashe masa tayi da kuka tace "uhmm ni bana farin ciki Sabida zaka rabani da Yaya Khabeer

ɗina, ni a halin yanxu dashi kaɗai nakeso na zauna, wllh banajin zan jure rashinsa a tareda ni! Ta faɗa cikeda rashin ƙwarin gwiwa.

Cikin sigar Rarrashi Maheer yace "haba Queen kefa matana ce, khabeer kuma yayanki ne nasan dole wata rana ze dinga zuwa yana ganinki, Kuma Aurena dake bawai yana nufin kawo ƙarshen alaƙarki da ƴan uwanki ba Yazu dai don Allah kiyi shiru bana son Inajin kukanki.

Ƙara sautin kukanta tayi Sabida ganin gaba daya ma be fahimci inda zancenta ya dosa ba, rarrashinta ya dingayi tareda gaya mata kalamai masu sanyi gamida tsayawa a rai sannan tayi shiru, seda suka ɗan taɓa hira sannan yace " queen barina barki haka time ɗin tashin flight ɗin mu yayi,

Addu'ar sauka Ify tayi masa sannan ta ajiye wayar wanda hakan yayi daidai da shigowar Mamie ɗakin, tsayawa tayi tana kallonta kima nin mintuna biyu sannan ta shiga da sallama.

Miƙewa Umaisa tayi tsaye tana kallon mamin da mamki Kwance a kan kyakkyawar fuskarta, sabida idan har zata iya tunawa daidai mamie tafi wata biyu batazo ɗakinta ba, murmushi Mamie tayi lokaci guda kuma murmushin ya ɓace ɓat daga kan fuskarta, takawa tayi har xuwa gaban dresing merior ɗin dake ɗakin tace " Ina Fatan ba wannan yaron da sukazo da mujaheed bane zaɓin Ran naki?

Kasa magana Umaisa tayi sabida yanda tambayar mamien tazo mata a bazata, gabaɗaya daburcewa tayi sabida rashin sanin takamaiman ta inada zata fara bata amsar tambayan nata.

"dake nake magana Fatimah!!

Jikinta ne ya qara masifar sanyi tunda taji Mamie ta faɗi Ainihin sunan ta, tabbas tasan yau a kwai magana a bakin mamien don haka a sanyaye ta sunkuyar da kanta tace "shine Mamie,

Shiru mamien tayi kimanin wani ɗan lokaci sannan tace " masha Allah da kyau Fatimah Allah ya sanya alkhairi, idan kunyi waya dashi inaso ki sanar dashi cewar ya gayawa iyayensa su fara shirin karɓar baƙuncin ki a matsayin suruka a cikin satin nan.

Da wani irin sauri ta ɗago da fararen idanunta waƴanda ƙwallah ta cikasu tab tana kallon mamien, sosai idanunta suka baiyana irin kaɗuwar da Umaisan tayi duk a sanadin furucin mamie wadda ke tsaye tana kallonta, da sauri ta isa ga Mamie ta riƙe ƙafafunta tana me sakin kukan daya taso mata tace " don girman Allah Mamie kiyi haƙuri kiyafemun laifin dana aikata a gareki, wllh mamie kuskure da ƙuruciyane suka sa na saɓa miki harna Auri mutumin da Ba shine zaɓin daya dace da ra'ayinki a kaina ba Mamie na!

Nasani na tabka kuskure me girma dana bijire miki amma ba laifina bane laifin ƙaddarar data gifta a tsakani na da maheer ne...! Ta faɗa tana fashewa da wani irin kuka me taɓa rain duk wanda ke sauraronta

jikin mamie ne ya ƙarasa sanyi a lokacin da kunnuwanta ke sauraron ɗiyar tata, don haka tasa hannu ta ɗagota cikin wani irin yanayi me baiyana shaƙuwa irinta ɗa da mahaifi tace " it OK dear wipe your tears maminki ta daɗe da yafe miki kukan ya isa haka nan, dukda irin kukan da takeyi hakan be hanata sakin murmushin jin daɗin kalaman mahaifiyar tata ba, ko babu komai yanzu ta rake kaso 80 a cikin damuwar dake damunta.

Washe gari da safe gaba ɗayansu Ahalin gidan na Alhaji Mahmoud muhammad suka hallara a makeken daining table ɗinsu suka gabatar da breakfast ɗinsu ciki kuwa harda Baban gano tamkar babu wani abou daya faru a cikin gidan.

Sosai Umaisa kejin kunyar Ummie da Abba duk a sanadin abinda ta aikatawa gudan jinin ɗansu naƙin amincewa da Aurensa ta Auri wani can daban, a haka kowa ya watse ya koma ɗakinsa akabar khabeer kaɗai da Umaisa wadda keta faman juya tean dake gabanta tana haɗawa da satar kallonsa, kasancewar yau lahadin ƙarshen mako ce Babu aiki,

shan tean sa kawai yakeyi yanata faman ɗannar wayar dake hannunsa batareda yama lura da wata aba me rai wai ita Umaisa ba, takaici Da baƙin cikine sukayi mata dirar mikiya a lokaci guda, mata irin mayatacciyar soyayyar khabeer ce take cinta kamar zata zauta ta, miƙewa tayi jikiba ƙwari zatabar gurin taji sautin Husky voice ɗin sa yace "wa kika barma wannan tean da kika gama yima ƙazanta a nan ya shanye miki?

kukan datake dannewa ne ya samu nasaran ƙwace mata, miƙewa yayi cak hannunsa ɗauke da mug ɗin tean dayake sha ya bar mata gurin sabida bayaso ta fahimci rauninsa a kanta.

Durƙushewa tayi a gurin tana aikin gursheƙen kukan da baze taɓa canza ƙaddarar da Allahɓya aika mata a cikin rayuwarta ba.

********

*_ƁANGAREN MAHEER KUWA_*, basu suka sauka a Nigeria ba se wajen ƙarfe 3:00pm tun kafin ya iso ƙasar Abdul ya kasa ya tsare a babban filin jirgin na Dr. Inamdi Azikwe dake babban birnin na taraiya Abuja, a lokacin dayayi Arba da ɗan uwan nasa wanda ya maye masa gurbin mahaifiya a gareshi ba ƙaramin daɗi yaji ba, cikeda farin ciki ya isa gareshi ya ƙanƙameshi yana me baiyana farin cikinsa, shima a ɓangaren na Maheer Lamiɗon hakan take a haka suka rankayo zuwa gida, tun kafin su shiga gidan mamaki ya baiyana a fuskar Maheer ƙarara sabida duk inda ya kalla a cikin gidan seyaga an sanya wata alama tayi masa barka da dawowa ta hanyar sanya wasu irin ƙayatattun fure masu launin Ja da Ruwan ɗorawa Sunyiwa wani babban allo kawanya wanda akayi rubutu kamar haka a jiki *_"WLCOME HOME MY DARLING SOM MAHEER LAMIDO!,_* Wani irin farin ciki ya samu zuciyarsa a ciki yayinda yayi arba da wannan allo da kuma rubutun dake jikinsa, tabbas koba'a faɗa masa ba yasan aikin Dadynsu ne sabida shi kaɗaine ze iyayi masa hakan, nan da nan kewar momynsu ta dawo masa sabuwa a cikin zuciyarsa, wata irin ƙwallace ta cika Zagayayyiyar ƙwayar Idanunsa a lokacin daya hangi Dady da sauran danginsu na Adamawa sun fito tarbarsa, Rabon dayaga an taru haka da sunan tarbarsa tun sanda ya kammala karatunsa na scondry schl, a hkaa suka ƙarasa cikin

gidan kowa yana nuna farin cikinsa akan nasarar da Maheer ɗin ya samo,  bayan lafawar komai ne Maheer yaja Abdul Yace " Boy wai wannan taron duk na menene haka?

Kashe masa ido ɗaya Abdul yayi sannan ya kalli mutanan dake falon yace "ga wata tambaya amma inji Maheer Lamido ba inji ni ba wai duk wannan taron daya gani na jama'ar yolo duk na menene haka ?

Abdul ya faɗa yana Dariya tareda kallon maheer wanda yaji kamar ya nitse A gurin sabida abinda qanin nasa ya Faɗa,

Da wani irin gudu Maheer ya nufi Abdul nan suka nufi ɗakin da Abdul ɗin ya nufa yana ihun kiran Dady.

Dariya jama'ar falon sukayi zuciyar kowa a wanke tass suna masu shi'awar irin qaunar dake tsakanin Brothers ɗin.

*******

Bayan kwana huɗu, kamar yanda mamie ta faɗa kuwa hakance ta kasance, don haka yau mutanan gidan suka tashi da hidimar taron biki kamar yanda Abba ya Zartar akan ɗiyar tasa Umaisa,  tunda sanyin safiya Ummie tasata a mota itada Rumana da Aunty Maryam yayar Beebah ƴar ƙanwar Ummie suka tafi gidan Hajiya ƴar borno don Ayi mata gyaran jiki,  sosai Umaisa ke zubawa Ummie darun ita bazatayi wani gyaran jikiba a ƙyaleta haka nan batason komai,  seda Ummie taci ƙaniyarta sannan aka samu ta nutsu ta shiga motar suka kama hanyar gidan Hajiyar dake Gwarinpha 35 road opp fifth Avenue Abujah.

Sosai Hajiya Asma'u ta gyara Umaisa ciki da waje, cikim ƴan awanni Umaisa ta fito tayi wani irin mugun kyau fiyeda ynda take se faman shaining take kamar walƙiya,  cikin ƴan awannin da bazasu gaza uku ba jikin Umaisa  ya kama ƙamshi.

Bayan ta gama mata dilkan da kuma halawan ta shiga toilet ɗin dake ɗakin ta haɗa mata ruwan wanka me ɗan ɗumi wanda aka ƙawatashi da wasu sunadarai na musamman a cikinsa masu fitarda wani irin ni'imtaccen ƙamshi me zaburar da zuciyar duk wani wanda ya shaƙeshi.  Tana fitowa ta kalli Umaisa  tace "Amarya tashi ki shiga kiyi wanka ki fito mu ƙarasa na gaba kuma, turo baki Umaisa tayi tana ƙunƙuni ta shige toilet ɗin.

dariya Aunty maryam tayi sannan ta kalli Ruman tace "huh Kuna fama da rikicin ƴar gidan Abba, ta faɗa tana dariya

Dariya Rumana tayi sannan tace ai mun kusa hutawa da rikicinta taje can tayiwa mijinta  kuma.
_*🎀KIYARDA DANI...!🎀*_
🎀🐾🎀

*♝IDTєƖƖIƓєDT WrITєr'ى  ASSѡ📚✍*

*💫DEDICATED: to Sis naja'art*

_*WRITING BY: Zm (CHuBaDo)*_

*✨Special Gift for Hafsat Hafnan (my jika),.*

_Page:46_

NOTE EDITED🙅‍♀️
___________📖 dariya sukayi gaba dayansu ciki kuwa harda Hajiya Asma'u ƴar Borno A haka Umaisa tafito se faman tura baki takeyi, murmushi Aunty maryam tayi sannan tace "zo da sauri ki shirya ƙanwata kar mutane su fara taruwa babu Amarya, ƙwallace ta ta cika idanunta batareda tace dasu ƙalaba ta nufi gefan inda Aunty maryam ɗin ke zaune tace "Aunty ina kayan to dazan saka?

Dariya Rumana tayi tareda tarar numfashin Aunty maryam tace " Ran Amarya ya daɗe Ai ga kayan can akan kabbasa Ana turara miki shi da special turaren da aka tanada domin Amaren da iyayensu ke matiƙar jidasu, ta faɗa tanayi mata dariya irinta tsokana.

Narai-Narai tayi da ido zata fara kuka da sauri Aunty Maryam tajata jikinta tareda gallawa Rumana harara tace "Ruman banson iskanci fa kinji ko.

Haɗiye dariyarta Rumana tayi batareda ta sake cewa ƙala ba, a haka Hajiya Asma'u ta fito hannunta ɗauke da wani ƙayataccen mai me masifar ƙamshi na musamman sannan ta miƙawa Umaisa tace shiga ciki ki shafe duk ilahirin jikinki dashi amma banda privet part ɗinki, karɓa tayi har lokacin bata dena tura baki ba ta nufi ɗakin da Hajiya Asma'un ta nuna mata, cikin mintunan da bazasu gaza 3ba ta fito sanye da wata rantsattsiyar Doguwar riga baƙa wadda aka ƙawata da rantsatsun Fararen stons masu masifar ɗaukar ido tamkar madubi, sosai rigar ta baiyana kyawunta gamida hasken fatarta tamkar daga tsatson larabawa ta fito ba'a jinsin baƙaƙen fata ba,

"Masha Allah! Shine kawai abinda Aunty maryam ke faɗa a ƙarƙashin zuciyarta, ƙarfe biyu daidai sukabar gidan Hajiya Asma'u suka nufi inda za'a rangadawa Amarya kwalliyar kece Raini, wata katafariyar plaza suka nufa dake Wuse 2 Abuja, wani ƙayataccen shago suka wanda Akayi rubutu cikin wani irin salon na burgewa a samansa kamar haka *_SUSHMAH GLAM,_* A nan na fahimci cewar shagon shahararriyar makeup artist ɗinnan me matiƙar jida kanta gamida iya kwalliyar kece raini sukaje, a hankali suka tura ƙofar glass ɗin ta buɗe wata matashiyar mata suka gani a zaune da budurwar ɗiyarta wadda aka caɓawa uban ado se baza kyau da sheƙi takeyi, seda suka matso dabdasu sannan Rumana ta washe baki tace "La Aunty

Rumaisa kece yau nake gani a gabana?  Rumana ta faɗa with so much surprise at her face

Da mamaki su Umaisa suka kalli Rumana cikeda som sanin inda Rumana ɗin tasan ta, dariya Rumana tayi sannan tace *_RUMAISA SALMAN CE fa jarumar cikin littafin Rumaisa Salman mallakin Hauly (maman khausar)_* murmushi matar da aka kira da Rumaisa tayi wanda haka ya ƙara baiyana kyanta tace " banyi mamakin jin sunana danayi a bakinki ba tunda nasan cewar labarina ya bazu a duniya tayanda ni kaina ban taɓa tsammani ba balle zaton  hakan.  Ta faɗa tana murmushi

Gaisawa sukayi dasu Aunty maryam sannan sukai sallama da juna RUMAISA SALMAN ta tafi ta barsu da begen halaiyar ta ta kirki da kuma son jama'a.

Zama sukayi sannan Aunty maryam ta sanar da Sushmah irin kwalliyar datakeso ayiwa Umaisan, murmushi kawai tayi sannan ta kalli maryam da fararen idanunta cikeda yarda dakai tace "indai wannan ne bakida matsala my sister, zan fito muku da Amaryarku kamar yanda kuke fata koma fiye da hakan.

cikin mintunan da bazasu gaza biyar ba aka sanyawa Umaisa wata rigar leda don gudun kar'a ɓata a bayar ta shiga fesa mata kwalliya ta kece raini, cikin abinda baze gaza awa guda ba ta gama mata wanda hakan yayi daidai da kammala kwalliyar da akewa Rumana itama,  roling Sushmah tayiwa Umaisa me wani irin filawas kamar toban a samansa wanda hakan ya ƙara fito da kyan kwalliyar sosai.

baki Ruman ta saki tana kallon Umaisa a lokacin da aka fito da ita daga ɗakin kwalliyar bayan an kammala mata,  ƙuri tayi mata da ido tana kallon irin kyan da Umaisan tayi, tabbas tasan Umy tanada kyau amma bata taɓa zaton kyanta ya zarta zatonta ba seda aka fesa mata wannan adon ya ƙara fito da ainihin izharin kyanta da be baiyana ba tun farko. ( niko nace ikon Allah Ashe kyauma yanada izaharinsa shima 😂😂)

duk wannan abin a cikin awa ɗaya akayishi ba wani ɓata lokaci, babu abinda ke tashi a shagon se ƙamshi mayatacen turaren dake tashi a jikin Umaisa,  A haka Aunty maryam ta fito da bunch ɗin 1k  ɗin da Ummie ta bata ta miƙawa Sushmah tana murmushi tace "mun gode sosai haƙiƙa kin cancanci da abaki lambar yabo sabida kinsan aikinki.

murmushi Sushmah tayi mekyau sannan tace "nikeda godiya Amarya Allah ya sanya alkhairi kinji.

Itadai Umaisa batace komai ba su Rumana ne suka Amsa sannan  suka fita zuwa parking space suka shiga mota Driver yajasu suka Nufi Gidansi dake Zone E Apo legislative Quarters.

Koda suka iso gida duk muta nan Ba wasu mutane sosai   duk an gama kwashesu zuwa babban Event Center ɗin dake central area inda za'a gabatar da walimar a can,

******

A ɓangaren su Maheer ma sosai suketa hada-hadar zuwa gurin walimar shida abokinsa Mujaheed da kuma Abdul,  sanye Maheer yake cikin wata ɗanyar shadda gizna maroon se faman yararin tsada takeyi, kansa sanye yake cikin wata dakakkiyar hula me tafiya da zamani irinta yƴan meduguri  (Zanna bukar) itama maroon amma da ratsin milk sabida aikin dake gaban babbar rigar shaddar dake jikin nasa, ƙafarsa sanye take cikin wani tsadadden takalmi ƙirar Batozy wanda yayi daidai da kalar kayan dake jikinsa.

A gogon Rolex ɗin dake hannunsa yaketa faman fafutukar ɗaurawa sannan Mujaheed ya kalleshi yace "hey dude duk wannan adon fa bakasa turare bafa.

Da sauri Abdul buɗe drower ɗin maheer ya zaro wani tsadadden  turare *_ORIFLAME PRODUCTS  GIORDANI_* ya fara feshe Maheer wanda ke tsaye  dashi, kafin kace me tuni ƙamshi ya gama buɗe ɗakin,  masha Allah sosai Ango maheer ya fito yayi masifar kyau kamar a saceshi a gudu.

Abdul ma ya fito yayi kyau dashi sosai abinku da yaro ɗan ƙwalisa lol

Ƙarar wayar maheer ce ta kaure ɗakin da wani irin kiɗa me taushin gaske, miƙewa Abdul yayi ya isa ga wayar yana murmushi,   daga ɗan nesa dashi Maheer yace "who is calling boy?

Dariya Abdul yayi sannan ya kalli screen ɗin wayar yace " *ACP SALEEM KHABEER KUMO* ne yake kira.

Dariya mujaheed yayi yana kallon Maherr yace " lallai mijin *MALIKHA MALIKH* wata ƙila ya iso gari ne yasa yake kiranka yaji inda muke ne.

Sushmah✍️

Chubaɗo

_*🎀KIYARDA DANI...!🎀*_
🎀🐾🎀

*♝ IᗪTЄ|||GЄᗪT WrITЄr'ى  ASSɷ📚✍️*

*💫DEDICATED: to Sis naja'art*

_*WRITING BY: Zm (CHuBaDo)*_

*✨Special Gift for Hafsat Hafnan (my jika),.*

_Page: 47_

Not edited🙅‍♀️

____Murmushi Maheer yayi sannan ya ƙaraso ya karɓi wayar yana me faɗaɗa murmushinsa ya manna wayar bisa kunnan sa na dama, tun kafin yayi magana *_ACP SALEEM KHABEER KUMO_* yace " pls dude you should be fast mana don Allah wllh kowa ya taru kukawai muke jira kaida Amarya.

Jim kaɗan Maheer yayi sannan yace " You mean wai har ka iso Abuja?

Ae mana amma ni kaɗai nazo sabida ma'am batajin daɗi shiyasa na barta a gida tareda yara, yanzu dai don Allah ku hanzarta ku fito jama'a duk sun taru kaida Amarya kawai ake jira.    Da to maheer ya amsa sannan ya katse wayar yana murmushi,  a hanzarce suka gama shirin sannan suka fito se faman baza ƙamshi sukeyi

Mujaheed ne ke tuƙa motar Abdul kuma na a gaba se maheer wanda ya hakimce a baya shikaɗai,  cikin mintunan da bazasu gaza goma ba suka iso ƙofar gidansu Umaisa, seda suka tsaya sukai sallar magrib sannan Mujaheed ya kira Rumana yace Su fito da Amarya.

Murmushi Rumana tayi sannan ta katse wayar ta kalli  Aunty maryam tace "tofa Angwaye sun iso ɗaukar Amaryarsu  suna ma waje suna jiran fitowarta.

Dariya Aunty maryam tayi sannan ta miƙe ta ɗago Umaisa wadda ke zaune bisa Daddumar data idar da sallah tace, Oya tashi kisa mu ƙarasa shiryaki tun kafin Maheer ya shigo da kansa, hawaye ne suka cika ƙwayar idanunta  da sauri Ruman ta dafata tace "haba kekuwa don Allah karkiyi kuka mana ki ɓata kwalliyarki.

Banza tayi mata se faman tura baki takeyi a haka suka kammala shiryata Maryam ta rangaɗa mata wani ubansun Roling dayake itama gwana ce a wannan fannin, kafin kace me Umaisa ta fito  tayi wani irin kyau tamkar bala'rabiyar ƙasar misirah.

Hannunta Suka kama zuwa falo a nan sukaci karoda Ya Usman da Farouq suma Sunci uban ado cikin wata dakakkiyar Gizna Ash se faman yararin tsada da kyau takeyi,  tsayawa sukai suna kallonsu  lokaci guda suka saki murmushi tareda ƙarasowa garesu,  hotuna suka dinga ɗauka sannan Aunty maryam ta tisata suka fice sabida idan tabi tasu Usman da Farouq to wllh Zasuyita ɓatawa su Maheer lokaci ne.

A nitse suke takawa suna riƙe da hannunta,  seda suka kusa dabda motar sannan Umaisa ta tsaya cak taki tafiya,  ɗaga haɗaɗɗen mayafin da Aunty Maryam ta Rufa mata tayi sannan ta

kalli Ruman tace "bazan iya tafiya ba indai banga Ya golden ba, tana kaiwa nan ta juya da gudu tayi cikin gida direct part ɗin ya Khabeer ta nufa tareda buɗe ƙofar perlourn duk a lokaci guda,

A falon ta sameshi yana gyara zaman Hular dake kansa, dukda cewar baya cikin kwanciyar hankali da nutsuwar zuciya sam hakan be Hanashi yin kyau ba,  sanye yake cikin wada dakakkiyar farar shadda ƴar ubansu wadda ta baiyana ainihin kalar fatarsa da kuma haibar dayake tare da ita.

Tsayawa suka cak idanunsu ya sarƙe cikin na juna,  kowa da abinda yake saƙawa a zuciyarsa a gameda ɗan uwansa, da wani irin mugun gudu ta tafi ta faɗa jikinsa ta Rungumeshi,  wata irin nannauyar ajiyar zuciya ya sauke a boye sannan ya zarota daga jikinsa sabida sam bayaso ta fahimci Rauninsa, murmushi ƙarfin hali ya saki sannan ya tallafi fuskarta yace "Masha Allah sis you look so pretty, don Allah karki bari kiyi kuka kodan karki ɓata kwalliyarki, Oya muje nasan suna nan suna jiranki.

Ya faɗa yana Ruƙo hannunta suka fita waje, a harabar gidan ya samu su Ruman se faman jiranta suke ya kalli maryam yace " kuyi haƙuri don Allah kinsan ƙanwar tamuce bata girma kullum abin yara takeyi.  Ya faɗa yana lakuce mata hanci

Har bakin motarsu maheer ya kaita yana riƙeda Hannunta sannan ya  buɗe mata murfin motar ta shiga ta Zauna se faman kallonsa takeyi idonta a cike taf da ƙwallar ƙaunarsa da kuma nuna tausayawarta a gareshi.   Da sakin fuska ya miƙawa maheer hannu sukai musabaha juna yana me ƙara faɗaɗa murmushin dake kwance a kan kyakkyawar fuskarsa yace "kuyi haƙuri fa mun ɓata muku lokaci.

Murmushi maheer yayi sannan yace "no my In-law karka damu wllh ba komai.

Cikeda tsokana Abdul yace " ai wllh Dr. Karka yarda da zancen ya Maheer kawai faɗa yayi, tun ɗazufa yake ce mana shi wllh idan ba'a fito masa da matarsa ba ciki ze biyota ya ɗakko abarsa, amma shine yanzu daya ganka ze wani canza mag.........  Duka maheer ya kai masa a bayansa dole yasa Abdul yayi shiru yana danne dariyarsa.

Murmushi kawai Khabeer yayi sannan ya juya ze bar gurin,   da sauri ta kama hannunsa na dama tareda langaɓar da kanta , wani irin kuka ne ya taso mata amma sedai taƙi ta bawa kanta damar yin kukan kodan karta ɓata kwalliyarta kamar yanda Ya golden yace da ita tayi kyau sosai kuma don Allah kartayi kuka.

Dawowa yayi da baya yana sakin mata wani irin ƙayataccen murmushi yace "banace karkiyi kuka ba?

Nima Dr. Abdullah nake jira da zaran ya iso muma zamuzo gurin.   Ya faɗa yana zare hannunsa daga nata sabida bayaso tana kusanta kanta da gangar jikinsa.

Dariya Abdul yayi sannan ya kalli Khabeer yace " lallai Amaryanmu yar gata ne dama nine ita wllh, ya maheer ka gani kuma ka koyi yanda ake tattalin ƙanne ba irin yanda kake tafida naka salonba.

Murmushi kawai Maheer yayi batareda yace dashi ƙala ba,  rufe musu murfin motar khabeer yayi sannan ya juya zuciyarsa a matiƙar raunane.

Cikeda ƙarfin hali yasa hannunsa na dama ya dafe saitin zuciyarsa sabida wani irin zafi da take masa batareda ya bari kowa ya lura dashi ba, Farouq ya kalla yace "ku tafi tareda Ruman da Maryam seku ajiyesu sabida be kamata kubar Maryam ta tuƙa mota a daran nan ba.

da mamaki Maryam ta kalleshi sannan tayi dariya  tace " lallai Dr. Ka raina ƙwarewa ta, ai wllh badan karkace na zaƙe dayawa ba to dase nace kokai bazaka nuna min ƙwarewa a gurin iya tuƙi ba ballan tana waƴan nan.    Ta faɗa tana nuna su Farouq

Dariya suka fashe mata dashi gaba ɗayansu sannan suka shiga motar Usman ɗin sukabar harabar gidan suna masu marawa motar su Maheer  baya Suka nufi inda ake gudanar da taron liyafar.

*A CLASS PARK METAMA  ABUJA*

A cikin ɗaya daga cikin manyan tantinan bikin dake gurin na hangi dandazon jama'a da dama a wannan guri, kowa yana wane wannan Baban Gano ma dana ganta sam ban gane ta ba, sanye take cikin wani ɗanyen leshi na nunawa sa'a hakama su Ummie da Umma Suma kowa ya Cakare cikin dakakken leshinsa, can na hango Mamie Zaune bisa ɗaya daga cikin kujerun da aka jera sabida baƙi ta hakimce a kai sekace ba Uwar Amarya ba,  itama irin leshin jikin su Ummie ne a jikinta sedai banbancin kala kawai, su Ummie da Umma ne kawai suketa faman hada-hada amma banda Mamie itadai kawai se kallo takebin kowa dashi,  gabaɗaya zuciyarya babu nutsuwa a cikinta tanaga Khabeer wanda ta tabbatar da cewar dauriya kawai yakeyi akan Rasa Umaisa dayayi, shiyasa gaba ɗaya komai na gurin bayayi mata daɗi.

Can na wallafa ɓangaren dangin ango maheer suma sun ci uban adonsu kamar baza'a mutu ba, abinku da masu hannu da shuni, se faman hada-hada mutanan yola sukeyi musamman ma Dadaji da gwaggwannin Maheer ɗin sautin dake tashi a cikin maque ɗin ya canza sabida zuwan Amarya *_UMAISA MAHMOUD MUHAMMAD DA ANGONTA MAHEER NASEER LAMIƊO_*

Nanfa al'amari ya canza aka fara ruwan kuɗi bana tsiya ba kafin kace me guri ya kacame da masu liƙa abin arziƙi.

Suma su Ummie da  Umma basuyi ƙasa a gwiwa ba  suka buɗe bakin jaka  hakama su Farouq da Usman  inda kuka san bada guminsu suka nema ba.

Itadai Mamie tunda ta zauna bata tashi ba har Amarya da ango suka isa kan kujerar da aka tanadar musu wadda ko wace budurwa take hari inda sukeyi mata laƙaɓi da ((Kujerar muna fama))😂😂

Bayan lafawar komai ne aka fara gudanar da shirye-shiryan da aka tanada a gurin,   Rumana aka kira ta fito donta bada tarihin amarya Umaisa. A nitse Ruman ta fara bayaninta cikin nutsuwa harta gama,  tana ɗagowa suka haɗa ido da Abdul  kawarda kanta tayi sannan ta nufi mazauninta ta zauna,  bayan ta koma ta zauna ne aka Kira Abdul shima ya fito donya bada tarihin Rayuwar Yayansa Maheer inda ya fara magana kamar haka

"Assalamu'alaikum warahmatullah, kamar yanda aka buƙaci cewar na fito na bada tarihin waye yayana Maheer cikin ikon Allah kuwa zan gaya muku wayeshi.

A taƙaice ɗai Maherr Naseer Lamiɗo mutum ne me matiƙar sauƙin kai gamida girmama duk wanda Allah ya haɗashi zama ɗashi, din hak babu abinda zance a nan   illah Amaryar Umaisa kinyi dace da samun miji na gari.

Mamana kullum tana gayawa Yayana maheer cewar *_KANEMA KA SAMU YAFI KANEMA KA RASA MAHIMMANCI_*

Wata irin zabura Mamie tayi daga kan kujerar da take zaune zuciyarta na wani irin harbawa kamar zata fito waje,  a matiƙar kiɗime ta miƙe ta isa har gaban Abdul ɗin ta tsaya tana binsa da kallo bakinta na wani irin karkarwa tace " A...A'iii....na  kasan wannan kalaman hikimar??

Da mamaki Abdul yake kallonta sannan yace "a bakin yayana nasansu, kullum seya gayamin waƴan nan kalaman hikimar tun ina ɗan ƙarami a lokacin dayake Rainona har zuwa yau danake tsaye a gabanki sabida yanda yake matiƙar son Mahaifiyarmu.  Banajin a kwai Ranar da gari ze waye Yaya maheer bemin zancen Momyn mu b......

Cakumeshi Mamie tayi lokaci guda kuma ta shiga girgizashi da dukkan ƙarfinta tana faɗin "waye yayan naka tana faɗa tana wani irin kuka kamar zata shiɗe?

Shiru holl ɗin yayi tamkar babu wasu halittu masu Rai a cikinsa, tuni Maheer ya miƙe tsaye yana binsu da wani irin kallo wanda yafi kamada na zallar kaɗuwa.

Hannu Abdul ya ɗaga ya nuna mata Maheer daga inda yake tsaye,  sakin Abdul ɗin Mamie tayi da sauri ta nufi inda Maheer ke tsaye, direct babbar rigar dake jikinsa ta fuzge da ƙarfin tsiya, lokaci guda kuma ta yaye rigar dake jikinsa gaba ɗaya farar fatar dake bayansa  ta baiyana, ƙurawa bayan idanu tayi lokaci guda kuma tayi karoda tabon ƙunar dake bayansa ta kwiɓinsa na dama  lokaci guda kuma ta zube a ƙasa kan gwiwoyinta ta fashe da wani irin kuka tana me riƙe ƙafafun Maheer ɗin.

Cikin mintunan da bazasu gaza 2 ba Numfashinta ya ɗauke ƙaff.

Hakanne yay daidai da shigowar yaya Golden, da wani irin mugun sauri ya nufi inda mamien ta zube ya fara jijjigata yana kiran sunan ta amma ina babu inda yake motsi a jikinta.

Wani irin kuka Maheer keyi wanda ya jima beyi irinsa ba, daga tabawar da Mamie tayi masa a wannan lokaci yaji irin abinda ya daɗe beji irin sa ba tun yana yaro ɗan shekara tara a duniya.

Tabbas yanaji a jikinsa cewar a kwai alaƙa me girma a tsakaninsa da wannan baiwar Allah wadda yake kallo a matsayin Surukarsa.

Bakajin sautin komai sena kukan Umaisa da Maheer , da sauri Umaisa ta dafa kafaɗar Khabeer tace "pls ya Golden help my mom I don't want lose her don girman Allah yayah!!!!!!

Hawaye ne suka cika idon khaberr sabida tausayin Umaisan, shin ta ina zd fara sanar da ita cewar Mahaifiyarta ta Rasu?

Dr. Abdullah ne ya ƙaraso gurin sabida yanda yaga yanayin abokin nasa ya fara duba Mamie wadda ke kwance, jikinsa ne yay masifar sanyi  bashida wani zaɓi dole ya ɗago yana kallomsu yace "there's nothing we can't do Umaisa I'm sorry!!!!!!!

Wata irin ƙara ta saki tana me faɗawa kan Mamie tana kuka.........
_*🎀KIYARDA DANI...!🎀*_
🎀🐾🎀

*♝ IᗫƬɵ|||ɪƓɵᗫƬ WɼɪƬɵɼ'ی  ASSoɷ📚✍️*

*💫DEDICATED: to Sis naja'art*

_*WRITING BY: Zm (CHuBaDo)*_

*✨Special Gift for Hafsat Hafnan (my jika),.*

*_O'o qorafinku akan wannan littafi yasa naji qaimi a cikin jikina, sannan kuma yasa na fahimci cewar Rubutunka kansa a qaunaceka qauna kuma irinta Fisabilillah❤️   Alkhairin Allah har bayanku mabiya wannan littafi_*

_Page:48_

______📖Sandarewa Umaisa tayi lokaci guda kuma ta saki wani irin kuka me ban tausayi Lokaci guda kuma ta zube a kan gwiwoyinta, Maheer ne yayi ƙarfin halin ɗagota ya Rungumeta yana rarrashinta, Sabida har zuciyarsa yakejin kukanta gabaɗaya nutsuwarsa tayi ƙaura daga gangar jikinsa zuwaga Mamie wadda ke kwance babu Numfashi,  nan da nan  Cikin hanzari Su Ummie suka ƙaraso gurin suna kiran sunanta lokaci guda kuma idanunsu suka shiga zubar da ƙwallar tausayin   Mamien.

Cikin hanzari  Dadaji yayar Mahaifin Maheer ta iso gurin Itama cikeda ƙarfin gwiwa Tana faɗin "ku matsa mana ta dinga samun iska Karku rufeya in ba haka ba ai se zafi yayi mata yaw....... Kasa ƙarasa maganar tayi Sabida arba datayi da Fuskar Mamie, da wani irin Karaji tace *"BADI'ATOU!!!!!!!.*

dirƙusawa tayi  bisa Kan gwiwoyinta sannan ta tallafo kan Mamien ta ɗora bisa kan cinyarta Hawaye nabin Fuskarta.

Duk wannan abinda akeyi Gaba ɗaya Abdul ya kasa motsin kirki illa bin mutanan dake gurin da kallo Kawai dayakeyi, Tun lokacin da Mamie ta dora hannunta bisa wuyan rigarsa yaji wani baƙon al'amari yana ratsa duk wata gaba dake jikimsa.

cikeda Ƙarfin hali Khabeer ya Fara giji-gijin ɗaukar Mamien Amma kuma ya kasa yin Hakan Sabida zazzaɓin dake tareda shi, koda Maheer yaga haka a hanzarce yayi gefe da Umaisa wdda keta uban kuka Sannan ya naɗe hannayen rigar dake jikinsa ya sunkuya ya ɗauki Mamien, direct ƙofar fita da Maque ɗin ya nufa Khabeer da Abdullah suna take masa baya,  a motarsa ya sanya ta sannan ya buɗe mazaunin Driver ya shiga ya zauna gaba ɗaya duk yabi ya Ruɗe Yama rasa meya kamata yayi, a Irin halin dayake ciki bayajin ze iya banbance irin Ruɗanin da zuciyarsa da tunaninsa suke ciki,  wani irin kuka ya saki tareda ɗora kansa bisa sitiyarin motar cike da rashin sanin makama, Bashida wani zaɓi wanda ya wuce yayi hakan meyasa ƙaddararsa take zuwa a haka ne?

Dafa kafaɗunsa Khabeer yayi tareda bubbuga bayansa alamar rarrashi Yace "kayi ƙoƙari ka ƙarfafi zuciyarka akan wannan baƙon al'amarin da ƙaddara tazo maka dashi Maheer, Karka bari zuciyarka taja akalar rayiwarka a duk lokacin da ruɗani ya Sameka, na tabbata idam kayi hakan watarana zakaci ribar haƙurin ka Lamiɗo,  so pls be patient insha Allah komai zeyi daidai sakko na tuƙa motar,   ba musu Maheer ya fito daga motar ya koma baya tareda ɗora kan Mamie bisa cinyarsa, a hankali yakejin matar tana ƙara samun kusanci da zuciyarsa se'a yanzu da ya ƙare mata kallo sosai ya  tabbatarwa da Kansa cewar  Tabbas yanada wata alaƙa da ita.

A shekarun daya shafe ba tareda Mahaifiya  ba abu ne mawuyaci Manta tsatson mahaifiyarsa Kokuma  kamanninta tun da yana da ƙaranci shekarun da ƙwaƙwalwarsa bazata iya riƙe hakan ba.

Buɗe gaban motar Dr. Abdullah yayi ya shiga Cikin hanzari sannan Khaber ya figi motar suka nufi Asbitinsu da ita.  Cikin mintunan da bazasu gaza 10 ba suka iso Cikin Asbitin abinka da masu abu da abunsu tuni nurses suka fito da gado suka ɗauketa zuwa ciki babu alamar Nfashi a tareda ita.

A wannan lokacin baiyana irin tashin Hankalin da Maheer yake ciki abu ne mawuyaci a gareni amma daga yanayinsa zaka fahimci baya cikin kwanciyar Hankali.

Zubewa yayi dirshan a ƙasan tiles ɗin dake Reception na Asbitin tareda dafe kansa da dukkan hannayensa biyu, babu abinda yake firtawa se "Innanillahiwa'inna'ilaihirraji'un!!!! Duk addu'ar datazo bakinsa yinta kawai.yakeyi batareda ɗorata a muhalinta ba

*******

*_ƁANGAREN ƳAN BIKI_* kuwa tuni aka watse kowa yayi ta kansa Masu tsegumi nayi masu kuka nayi  ahaka duk aka watse ya zamana  babu kowa se Makusantan Ango da kuma na Amarya ne kawai suka Rage a gurin,  kowa yayi jigum cikeda Rashin sanin madafa,  Dadaji  ce ta kalli su abdul tareda sauran jama'ar dake gurin tace " ya kamata mubi bayansu dan musan Halinda Badi'atoun take ciki.

Har lokacin Abdul ya kasa motsin kirki balle har ya iya  motsa wata gaba dake jikin sa sabida yanayin tashin hankalin dayake ciki,  hawaye ne suka fara zubo masa Se'a lokacin ya samu zarafin magana ya kalli Dadaji sannan yace "pls Dada tell me the truth who is she?  "inaji a jikina cewar tamkar inada wata alaƙa ta jini a tareda ita, a lokacin da hannunta ya taɓa jikina naji zuciyata da gangar jikina duka sun Amsa a lokaci guda, wani irin baƙon yanayi na sabo da kewa nkeji suna ƙara kusantoni, all i know is Zuciyata ta yarda da ita Kuma ina matiƙar sonta fiyema da Rayuwata gabaɗaya..!!!           Abdul ya faɗa yana  Rushewa da kuka tareda faɗawa jikin Dadaji.

Rarrashinsa ta shigayi tareda kama Hannunsa tace " tabbas dole ne a samu irin wannan yanayin a yayin da kewar wani babban abu me mahimmanci ta ziyarci zuciyar mutum, musamman ma idan akace Ƴar Uwar  mahaifiya.

Ajiyar zuciya ta sauke a hankali  sannan taci gaba da cewa "Abdul wannan maganar bata nan bace kayi haƙuri ka bari mu isa  Asbitin muga Halin datake ciki tukunna   inyaso mayi maganar daga baya  bayan komai ya daidaita.

Duk wannan Jawabin  da sukeyi kallonsu kawai Su Ummie da Mama keyi. Umaisa kuwa banda kuka babu abinda takeyi  gabaɗaya hankalinta ƙanin baya jikin ta ne, cikin kuka ta nuna Abdul tace " kadena wasu yi mana wasu kalamanka na yaudara malam, tunda na haɗu da ɗan Uwanka Rayuwata take shiga cikin matsala har zuwa Ranar da iyayena suka shaida Aurena dashi, wllh  sam Haɗuwata daku ba alkhairi bane tunda har kuke ƙoƙarin kashemin mahaifiyata duk sanda ta ganku se ciwonta ya tashi waya sani ma nan gaba ko kune Ajalinta kaida

yay........!!!!!   Kasa ƙarasawa tayi sabida wani irin kuka dayaci ƙarfinta

Farouq ne yayi ƙarfin halin Jawota jikinsa sannan ya kalli su Dadaji yace "kai wai duk way̯an nan maganganun da kukeyi masu kamada jirwaye me kamar wanka duk ina suka dosa ne ? "Se faman wata magana kukeyi wadda gaba ɗayanmu hankalin mu ya gaza fahimtar inda zancenku ya dosa gabaɗaya,  kun barmu a duhu ya kamata ku warware mana komai.     Ya faɗa yana bin Mutanan yolan  da wani irin kallo wanda yafi kamada na tsana.

"aa farouq wannan maganar bata nan bace kamar yanda ta faɗa kayi haƙuri mu isa gida tukunna, yanzudai abinda yafi mahimmanci shine lafiyar Mamie inyaso duk wata magana ta biyo bayan samun lafiyar nata.   Usman ya faɗi hakan ta hanyar dakatar da ƙudirin Farouq ɗin

"Amma Usman ai ya kamata musan komai ko, ka duba fa kaga tun daga ranar da wannan mutumin ya fara zuwa gidan mu na fahimci zuwansa ba alkhairi bane a Rayuwarmu, shiyasa tun farko ba wani soshi nake ba har Rain........... "Farouq!!!!!

Ummie  ta dakatar dashi ta hanyar daka masa wata uwar tsawa sabida takaicin maganganunsa, a hasale tace "karufewa mutane baki nace  ka barmu muji da abinda yake damun mu..

Shiru yayi yanajin wani irin takaici a zuciyarsa, wannan wace irin masifa ce haka?    Tunda Maheer ya fara zuwa gidansu yaji sam be kwanta masa ba, to yauma ga abinda ganin nasa ya sake haifarwa nan a kan mamien, nan gaba kuma wayasan meze faru

Damƙe hannun Umaisa Rumana tayi a lokacin da su Usman ke ƙoƙarin fita daga holl ɗin, sannan ta janyeta daga jikin Farouq zuwa nata ta rungumeta.

Fitowa sukai gaba ɗayan su suka shiga motocinsu sannan Usman yayi musu jagowa zuwa Asbitinsu yaya Golden ɗin.

Tun kafin su isa Asbitin Dadaji ta ɗaga waya ta shiga kiran wayar Baffa Giɗaɗo, zaune suke a babban falon Dadaynsu Maheer shidasu Baffa Umaru gabaɗayansu Suna hirar, ƙarar wayarsa ce ta kauraye ɗakin babban abinda yaja hankalinsa kenan  musamman dayayi arba da sunan Dadaji yana yawo bisa screen ɗin wayar, a nitse ya ɗauka gamida tattara duk wata nuysuwarsa yace " Jaɓɓanduna Dada?

Dada tace "jam Giɗaɗo Noisare?

"Jam Alhamdulillah Dada ya taron kuma?     Shiru ta ɗanyi sannan ta sauke ɓoyayyiyar Ajiyar zuciya tace "taro Alhamdulillah dama fɗaa maka zanyi duk yanda za'ai gobe inason ganinku gabaɗayanku  A nan  Abuja gidan Maheeru  Sabida a kwai mahimmiyar maganar da zamu tattauna A Kai daku me matiƙar mahimmanci a nan ɗin.

Cikeda girmamawa ya Amsa mata da "to Dada Isha Allahu goben zamuzo ɗin kamar yanda

kikace sannan sukai sallama da juna.

*****

Zaune yake dirshan a ƙasan tiles ɗin dake Asbitin idanunsa sunyi jajir sabida tashin hankali lokaci- lokaci yakan ɗaga kai ya kalli ƙofar ɗakin da aka Shiga da Mamien zuciyarsa na harbawa da wani irin Sauri, Babu abinda yake illa kiran sunan Allah Haka kuma duk Addu'ar datazo bakisa yinta yake fatansa kawai Allah ya tashi kafaɗar wannan baiwar Allah.

A haka su Usamn Suka iso Asibitin suka sameshi, har kusan ƙarfe ɗayan dare babu wani bayani da aka samu daga bakin likitocin akan mara lafiya, dole tasa Usman ya rarrashi matan suka mayar dasu gida duk irin kukan da Umaisa keyi seda suka maida ita gida kan cewar gobe zasu dawo da ita da safe, shiko Maheer da Farouq a nan sukaja tunga lokaci-lokaci yakan zabgawa Maheer harara tamkar shiya ɗowa mamin ciwon a haka har gari ya waye suna zaune tim tamkar an dasasu. Masallaci suka wuce sukayi sallah sannan suka dawo Reception ɗin wanda hakan yay daidai da fitowar su khabeeer ko wanne fuskarsa ɗauke da murmushin samun nasara, da hanzari suna isa gareshi suna tambayarsa yame jikin?

Dafa kafaɗar Maheer khabeer yayi Fuskarsa dauke da murmushi sannan yace " don't worry about it Lamiɗo she will be fine insha Allah tunda har mun shawo kan matsalar numfashin. Ya faɗa yana wucesu da sauri sabida lokacin sallah ya fara wucewa.

Sushmah💋

_*🎀KIYARDA DANI...!🎀*_
🎀🐾🎀

*♝ IᎠƬɵʟʟIƓɵᎠƬ WrIƬɵr'ى ASSϖ📚✍️*

*💫DEDICATED: to Sis naja'art*

_*WRITING BY: Zm (CHuBaƊo)*_

*✨Special Gift for Hafsat Hafnan (my jika),.*

BANYI EDITING BA🙅‍♀️

_______📖Sosai hankalin Maheer ya kwanta dajin abinda Khabeer ɗin ya sanar dashi miƙewa yayi cikeɗa ƙwarin gwiwa yabar Reception ɗin zuwa parking lot na Asbitin, motarsa ta buɗe ya shiga ya zauna lokaci guda kuma yayi mata key yabar harabar Asbitin zuciyarsa a cike taf da tarin al'hini, so yake kawai ya ganshi a gida Gaban dadaji sabida tsabar Ruɗanin daya Addabi tunaninsa a haka harya iso gidan horne me lafiya ya zabga da hanzari me gadi ya wangale masa ƙofar shikuma ya danna hancin motar zuwa cikin gidan, a nitse ya fito daga motar cikin takunsa na isa da ƙasaita ya nufi ƙofar maine falon dake gidan, se'a lokacin ya lura da tarin takalman dake bakin ƙofar wanda kobe tambaya ba yasan nasu Baffa Giɗaɗo ne da kuma na Dadynsa.

Jiki a mace ya tura ƙofar haɗe dayin sallama gabaɗayan  mutanan dake falon suka juyo suna kallonsa musamman ma Dadynsa, sakin handile ɗin ƙofar yayi lokaci guda kuma ya sinkuyar da kansa tareda ƙarasowa cikin falon ya nufi ƙofar bedroom ɗinsa ze shiga  batareda yace da kowa ƙala ba,  Dadaji ce ta miƙe da Sauri tace "Ya jikin Nata Maheeru?

Tsayawa yayi cak batareda ya juyo ba yace "Da sauƙi. Ya shige ɗakin ya kulle da mukulli, Drower bagon dake ɗakin ya nufa lokaci guda ya cire babbar rigar dake jikinsa ya jefarta gefe guda sannan ya buɗe Drower ɗin da mukullin dake Hannunsa, ba komai a ciki se wata ƙatuwar a kwati duk tayi ƙura da yana sabida Rashin buɗetan da ba'ayi, janyo a kwatin yayi ya fito da ita lokaci guda kuma ya tsaya cak yana kallonta zuciyarsa na azalzalarsa akan ya buɗe kodan ya tabbatar da zarginsa, mukullin dake jikin a kwatin ya ɓalle da ƙarfin tsiya har hannunsa na jini sabida

Babu komai a cikin a kwatin se manyan Frams an juya bayansu ma'ana fuskar frams ɗin dana kallon ƙasa ne, zarosu yayi da dauri lokaci guda kuma hawaye na wanke masa fuska a sakamakon tuna lokacin da Dady yasa masu aikin gidansu su fitar masa da duk hotunan Momyn su dake gidan su ƙonasu duk a ƙarƙashin jagorancin Makircin Hajiya Murja.  Waƴan nan hotunan uku ne kawai basu ƙona ba sabida suma ya ɓoye ne shiyasa suka tsira.

Fito dasu maheer yayi dika waje yana kallon hotunan yana kuka Momynsu ce zaune se kuma Dady daga gefanta  shikuma Maheer yana jikinta lokacin tana da cikin Abdul akayi hoton dukansu suna dariya,  ɗayan kuma yana ɗan shekara 12 a duniya sukai Hoton shida ita se kuma Abdul wanda ke ƙaramin yaro ɗan shekara 4 shima duk suna dariya,  ɗayan kuma ita kaɗaice A jiki da tsohon ciki a jikinta  tana Murmushi, to Anan ne fa Maheer ya ƙura mata idanu ya tabbatarwa da kansa cewar tabbas Matar dayakewa kallon Suruka Fa Mahaifiyarsa ce. Wani irin ihu ya kurma wanda yasa gabaɗaya gidan ya Amsa

Da gudu Su Dady suka nufo ɗakin bayan Dadaji ta gama zaiyane musu duk abinda ya faru a gurin Walimar tareda shaidawa Dady cewar Tsohuwar matarsa BADI'ATOU fa tana Raye bata mutu ba, be gama dawowa daka mamakin daya sha kansa ba sukaji ihun Maheer, kuka kawai Maheer keyi zuciyarsa nayi masa zafi tamkar zata fashe

Wato dama Mahaifiyarsu tana Raye amma shine sharesu ta manta da cewar tana da ƴaƴa har guda biyu a wataduniyar bata taɓa zuwa ta gansu ba koda so ɗaya ne ? "What kind of mother she is?  Maheer ya faɗa cikin ɗaga murya lokaci guda kuma ya shiga jifa da hotunan tamkar sabon mahaukaci

Buga ƙofar sukaita yi amma fir yaƙi buɗewa se faman kurma ihu yake sekace me hawa iska, juyawa Abdul yayi da sauri ya ɗaukki wuƙa a khitchine ya fara ƙoƙarin kwance Handle ɗin ƙofar, cikin ikon Allah kuwa ya samu nasarar buɗe ƙofar suka kunna kai zuwa ciki,  gadan2 Dady ya nufi inda Maheer ke tsaye ya dafe kai da dukkan hannayensa ya ɗago da sauri yace " don't come near me Dad you are the  responsible for everything, don haka kar ka ƙaraso ida nke a halin yanzu dukankubana buƙatarku a Rayuwata sabida baku ɗaukemu ƴaƴa  ba, bazan taɓa cewa na tsaneku ba sabida kuɗin iyayena ne  but lemme tell you something Daddy I will leave this House write know kuma wllh both of you daga kai har ita  you will never see me again nida ɗan Uwana!!! Ya faɗa yana miƙewa yaja hannun Abdul da ƙarfi zasu bar ɗaki

Baffa Umaru dake jikin ƙofar ɗakin yana tsaye yana kallon dukk haukan da maheer keyi lokaci guda ya ɗaga hannu ya zabga masa wani Uban mari me lafiya, tun kafin ya dawo daidai ya ƙara kwasa masa wani marin  Sannan ya nunashi da yatsa yace " don  Ubanga Nasiru dake tsaye idan ka fasa tafiya kaiba ɗan halak bane, karka manta gabaɗayan mu nan babu wanda be haifeka ba kai harma da wanda yayi jika dakai, lemme tell you something Maheeru iyaye ba abin wasa bane duk ɗanyan kanka wajibi ne ka saukesu kayi musu biyayya, sannan ya sassauta murya yace "kaifa ba yaro bane yanzu kaika minzalin da har ka ajiye mata Maheer ya kamata ka dinga danne zuciyarka kodan karta kaika ga halaka, mu kanmu babu yadda muka iya da  abinda ƙaddara tazo dashi Maheer dole ne mu karɓa

Zubewa Maheer yayi a gurin ya dinga gurzar kuka har seda yayi me isarsa sannan ya miƙe ya ɗauki mukullin Motarsa batareda yace da kowa ƙala ba ya fara ƙoƙarin fita, Riƙeshi Dadaji tayi tareda fizge mukullin motar. Rarrashinsa suka dingayi mutanan dake ɗakin shiko Dady babu abinda yakeyi se kuka

Abdul ma kukan yakeyi tamkar baze  dena ba. A haka dai gidan ya kasance babu walwala a safiyar Ranar gabaɗayanta

*****

Can Asibiti kuwa Mamie bata farka Se wajen ƙarfe 11:00am  na safe tana farkawa da Sunan Maheer ta fara tana kuka,  sosai hankalinsu Dr. Khabeer ya tashi suka Rasa yanda zasuyi da ita

Wayarsa ya zaro  ya shiga kiran Abba donya Sanar dashi Halin da ake ciki,  bugu ɗaya Abba ya amsa tareda yin Sallama, gaidashi khabeer yayi sannan ya shiga zaiyana masa abinda ke faruwa, hankalin Abba dake Adamawa ba ƙaramin tashi yayi ba akan batun Badi'atoun don Haka yace "ka kwantar da hankalinka Khaber insha Allah nima ina hanya yau zan biyo jirgin

shabiyun Rana zuwa Abuja insha Allah  sannan ya katse kiran

Kamar yanda Abba ya faɗa kuwa hakanne ya kasance ƙarfe ɗayan Rana a garin Abuja tayi masa kasancewar bashi kaɗai bane yasa ya fara zuwa gida ya sauke bakin nasa sannan ya ɗauri niyar Zuwa Asibitin,  ko ɗakin da Mamie take Abba beje ba Direct office ɗin khabeer ya nufa da sallama ya tura ƙofar.  Zaune ya sameshi da file a gabansa

Ajiya file ɗin yayi sannan ya kalli Abba yace "Sannu da zuwa Abba ka dawo Ify?  Lafiya lau khabeer Abba yace hakan sannan ya sake kallon khabeer a karo na biyu yace "Son ina fatan matsalar Badi'atoun ba ciwonta bane ya tashi? Khabeer yace "Ae abba ba ciwon bane kawai firgita tayi wanda har hakan yasa ya  suma bayan hakan ba wata matsala nanda Anjima zamu Sallameta zuwa gida.  Ajiyar zuciya Abba ya sauke sannan yace "to babu matsala to whynot ku bamu sallamar yanzu mu tafi kawai.

Shiru khabeer yayi sannan yace "to Abba bara na duba naga ko drip ɗin da aka saka mata ya ƙare. Ya faɗi hakan ya miƙewa yabar office ɗin, seda sukai Sallar Azahar sannan suka kama hanyar gida har khabeer ɗin, tun kafin Su isa gida kiran  Baffa Giɗaɗo  ya shigo wayar  Abba da kulawa ya ɗaga  babu wanda yaji abinda yace masa illa kawai amsar da Abban ya bashi yakamar haka "to se kunzo Giɗaɗo Allah ya kawoku Ify. Ya faɗa tareda katse wayar.......

_*🎀KIYARDA DANI...!🎀*_
🎀🐾🎀

*♝IDTΘ|||GΘDT WrITΘr'ی  ASSდ📚✍️*

*💫DEDICATED: to Sis naja'art*

_*WRITING BY: Zm (CHuBaDo)*_

*✨Special Gift for Hafsat Hafnan (my jika),.*

🔚🔚🔚🔚🔚🔚

_Page:50_

______📖Tunda Motarsu Abba ta sako kai cikin gidan Gaban Mamie keta faɗuwa dama ga tashin hankalin data samu kanta a ciki na daran jiya , Gabaɗaya komai ya denayi mata daɗi ta rasa inda zatasa zuciyarta taji ɗaɗi shiyasa gabaɗaya ta ɗinke bakinta ba magana sedai kallo kawai,

A halin datake ciki a lokacin babu abinda takeso tayi kamar kuka amma kuma ta kasayin hakan,

a yau kam Mamie ta yarda da cewar yin Kuka ma idan damuwa tayi maka yawa shima solution ne. a haka Abba ya faka motar suka fito zuwa cikin gidan jefa ƙafa kawai Mamie keyi tamkar idanunta zasu rufe ta zube a ƙasa a haka suka shiga cikin gidan kowa se farin ciki yake da samun sauƙin nata musamman Umaisa wadda ta miƙe da sauri ta nufi Mamien ta rungume ta ƙam, ita ko Ameerah tana jikin Ummie tana bacci ta gama rigimar ita Mamien ta zataje har tayi bacci.

Sama Mamie ta hau ta buɗe ɗakinta ta shiga ta zauna lokaci guda ta fashe da wani irin kuka wanda ta daɗe batayi irinsa ba, kukan kawai takeyi sabida rashin kwanciyar hankalin datake ciki a haka Abba ya shigo ɗakin ya sameta, ko kaɗan beyi yunƙurin hanata kukan ba har tayi me isarta sannan ta haƙura tayi shiru.

Ƙarfe Uku daidai gidan Alhaji Mahmoud muhammad ya sake karɓar baƙuncin shahararren ɗan kasuwarnan Alhaji Nasir Lamiɗo a karo na biyu dashi da Familynsa gaba ɗaya, a babban falon gidan aka saukesu shida bataliyarsa Abdul na Riƙe da Hannun Maheer wanda ko idanunsa baya iya buɗewa sabida azabar ciwon kai, sam beyi niyar zuwa ba seda Baffa Umaru ya tilasta masa sannan ya biyosu don a cewarsa baya ƙaunar ya sake ganin fuskar Mamie ko'a mafarki tunda harta iya barinsu tsahon shekara Ashirin batareda ta waiwayi inda suke ba, wannan dalilin ne yas yaji ta gama fice masa a rai gabaɗaya

Bayan sun shiga sun zauna ne Abba ma danasa Ahalin suka hallara a falon Gabaɗayansu Except Mamie wadda ke ɗaki tana ta faman gurzar kuka, komawa Abba yayi cikin gida har ɗakin mamie ya taho da ita sannan ta fito suka nufo falon tare, da sallama suka shigo ɗakin idanun ƙasa batareda ta kalli kowa dake gurin ba harta zuna sannan ta ɗago idanunsu ya Saƙe guri guda Dana Dady, a zabure ya miƙe yana nunata yake faɗin "BADI'ATOU kece ? Ashe dama inada rabon ƙara ganinki a cikin Rayuwata batareda ƙasa ta rufe idanuna ba?

Badi'atou meyasa kikai nisa da Rayuwarmu irin haka? Ban taɓa zaton zaki iyayin nisa damu kamar yanda kikayi ba dukda cewar nine ummul'aba'isin komai....... Dady ya faɗa yayin da ya fashe da wani irin kuka

Gabaɗaya falon babu wanda be girgiza ba musamman Ahalin Alhaji Mahmoud Muhammad tundasu dama can su Dadaji sunsan komai. Ita kanta kukan takeyi mamien sannan ta buɗe baki tace "idan har ka zargeni akan barinku danayi Bawuro bakayi min Adalci ba a Rayuwata, kada fa ka maɓta kaine da kanka ka datse igiyar Aurena dakai batareda ka tausayin kokuma cikin dake jikina ba, haka ka rabani da ƴaƴana sannan ka koreni a cikin dare batare da kayi tunanin irin halin da Rayuwata zata shiga ba, sannan yanzu har kake iya kallona kace meyasa nayi nisa daku bayan kaine ka nisantani daku da kanka Bawuro!!! Bayan rabuwata daku ban ƙara yin Rayuwar farin ciki ba, kullum tunanina shine ya zanyi insan Halin da Yarana suke ciki da Mahaifina? A sanadin wannan baƙin cikin da kuma yawan tunani yasa zuciyata ta kamu matsanancin ciwo duk a sanadin kewar ƴaƴana data mahaifina, duk sanda nayi tunanin na koma gida kalmar babana ta ƙarshe ce keyimin yawo a kunnuwana dayace "muddin na kashe Aurena karna koma masa gida idan har na dawo masa gida be yafe min ba. Wannan dalilin

shine ya ƙarasa nayi nisa daku batareda nasan halin da ƴaƴana suke ciki ba Bawuro, yanzu babban takaicina shine bansan a wani Hali mahaifina yake ciki ba shin yana Raye ne kokuwa ya mutu?

Gabaɗaya mutanan dake falon babu wanda baya hawaye can daga gefan Abba taji ance " kamar yanda kika Rayu da baƙin ciki tsahon shekaru 20 nima da haka na Rayu duk a Rashinki Badi'atou. Malam Bashir me Babban Allo ya faɗi hakan yayin da kuka yaci ƙarfinsa

Da hanzari Mamie ta isa ga Mahaifinta ta riƙe hannayensa tana kuka kamar kamar bazasu daina ba, duk wani me imani dake gurin dole ne ya tayasu kuka, nan take me Babban Alo ya dinga roƙon badi'atou yafiya akan abinda yaja mata na nisanta ta dayayi duk a sanadin kalamansa sannan Baffa Umaru ya fara magana kamar haka" To Alhamdulillahi da komai yazo mana da sauki batareda wata kwaɓar ta sake afkuwa ba dan gane da Auran Maheeru Da Fatima (Umaisa) shaidu ƙwarara sun nuna cewar Aure baze taɓa yuwuwa a tsakaninsu ba donsu haɗa Uwa ɗaya a tsakaninsu don haka wannan Aure An warwareshi, tsura masa ido Umaisa tayi batareda tace dashi ƙala ba, gabaɗaya kanta ya gama kullewa da maganar da mutumin nan ya faɗa, hakama su Usman da Farouq kai gabaɗaya ma Ahalin na Alhaji Mahmoud Muhammad.

Dadaji ce ta karɓi maganar ta hanyar cewa"tabbas maganar Umaru haka take wannan yarinya babu maganar Aure a tsakaninta da Maheeru har Abada dimin kuwa ƴar uwarsa ce ta jini, murmushi ƙarfin hali kawai maheer yayi sannan yace "tun Ranar dana fara ganinta naji a jikina cewar tabbas inada wata alaƙa da ita, haka kuma duk irin son danake mata ban taɓa jin inayi mata so irin na Aurataiya ba har zuwa ranar da aka ɗaura mana Aure da ita, nidai kawai inajinta a raina kwatan kwacin yanda nakejin Abdul a cikin zuciyata, ban Fahimci hakan ba se Ranar da mukazo gidannan nida Abdul muka Haɗu da Rumana ƴar uwarta to a nan ne na Fahimci Rumana itace zaɓin raina ba Umaisa ba. Itadai kawai Ina sonta har Raina ne sabida jinin ƴan uwantakar dake yawo a cikin jinina dana ne

Kabbara kawai jama'ar dake falon sukeyi Abdul kuka kawai yakeyi wanda yafi kamada na farin ciki Sannan Baffa Giɗaɗo yace " Alhaji Mahmoud muna baka haƙurin bisa warwarewar Auren ɗanmu da ƴarka Umaisa sannan muna roƙonka Arziƙi a karo na biyu ka bawa ɗanmu Maheeru Auren ƴarka Rumanatu.

Zaro ido Rumana tayi tana kallon Abba sabida tsabar yanda ta kaɗu dajin batun tana jira taji irin Amsar da Abban ze basu. Murmushi Abba yayi sannan yace "indai wannan ne baku da matsala dani wllh na bashi Aurenta idan da sadakinku seku bayar yanzu mu shaida batun auren tunda duk waliyan yaran muna nan, haka kuwa akayi cikin mintunan da bazasu gaza biyar ba aka ɗaura Auren Rumana Mahmoud Muhammad tareda Maheer Nasir Lamiɗo akan sadaki Dubu hamsin.

Babu wanda beyi farin ciki da wannan Auren ba, ɗago kai Mamie tayi tana kallon Umaisa tace "kamar yanda kika daɗe kina tambayata Mahaifin ki Umaisa yau gashi Allah ya kawoshi har

cikin gidanan ta faɗa yayin da take nuna mata Alhaji Nasir Lamiɗo  wanda ya kafe Umaisan da kallo, miƙa mata hannu yayi alamar tazo gareshi aiko da gudu ta miƙe ta nufeshi ta rungumeshi tana kuka haka suma Abdul da Maheer suka nufi Mamie suka rungumeta a lokaci guda suna kukam farin ciki

Farouq ne yaɗan sosa kai Yace "Abba tunda sun nemi Auran Rumana ka basu ba tareda shakka ba meze hana muma mu roƙesu su bamu Auran ƙanwarmu Umaisa tunda sune masu Ruwada tsaki se shima Yaya Golden mu shaida Auransa da ita.

Dariya gabaɗaya ƴan falon suka saki sannan Abba ya miƙa buƙatarsa gasu baffa Umaru na newa ɗansa Auren umaisa, take suma aka shaida nasu Auren akan sadaki nera dubu Hamsin wanda Alhaji Nasir mahaifin Umaisa ya biya masa, nan dai koya ya yafewa ɗan uwansa  taron ya watse, fir Abdul yaƙi tafiwa waishi ze zauna tareda Mamiensa dole suka hakuwa suka barsu har maheer ɗin

Ba ƙaramin farin ciki Khabeer yayi ba don harga Allah ya daɗe da fidda rai da auren Umaisa amma se gashi Allah ya sauya ƙaddarar zuwa wata ta daban wadda be taɓa zato ko tsammani ba. Allah kenan me yadda yaso

Se bayan sati biyu sannan su Umaisa suka tare a gidajensu bayan Ummie ta gama tsumasu da magunguna na musamman alhaji Nasir ne yayi musu kayan ɗaki gabaɗayansu sannan ya danƙawa kaberr mukulin gida da ƙatuwar mota a  Asokoro shida maheer.

A gurguje pls

Umaisa ce zaune gefan Gadon da aka ajiyeta Khabeer ya shigo ɗakin cikin wata dakakkiyar shadda brown wadda tayi masifar karɓar jikinsa, a hankali ya zauna daga gefanta yace "inayiwa matata kuma ƙanwata murnar shigowa gidan mijinta khabeer wanda yayi mata tanadin farin ciki marasa adadi a zamantakewar da zasuyi da juna. Ya faɗa yayin da ya ajiye ledar dake hannunsa daga gefanta,  miƙar da ita yayi suka nufi toilet sukai Alwala tare sannan suka fito yajasu salla don nuna godiyarsu ga Allah mabuwayin sarkin daya azurtasu da auran juna.

Bayan sun idar da sallar ne ya shiga jera mata tambayoyi akan abinda ya shafi addini  tana bashi amsa, daga bisani ya dafa kanta yay shiga jero musu addu'oi

Bayan ya kammala addu'ar ne ya jawo ledar daya ajiye ya buɗe mata yace "oya maza kici ki ƙishi ki bani ledar. Turo baki tayi kamar zatayi kuka tace "ni na ƙoshi yaya bazan iya ci ba. Ta faɗa tana kallon ƙasa

Murmushi yayai sannan ya jawota jikinsa ya fara bata kazar tana ci tana kauda kai  harta ƙoshi sannan ya zuba mata fresh milk ɗin a cup ya mika mata  yace " oya sha ki bani cup ɗin. Ba musu ta karɓa ta ɗan sha sannan ta ajiye Ragowa shi kuma ya miƙe ya fita daga ɗakin ya koma nasa

Wanka ya shiga sannan ya fito ya shirya cikin lausasan kayan baccinsa na companyn pj mas sannan ya dawo ɗakin ya sameta harta kwanta, murmushi yayi kawai batareda yace mata komaiba ya kwashe kayan da sukaci yakai khitchine sannan ya dawo ɗakin ya kashe musu ƙwai ya kwanta daga bayanta ya janyota zuwa jikinsa.

Doguwar rigar baci ta sanya jaki ta ko bushewa beyi ba tasa rigar ta kwanta don karyazo ya sameta, dariya yayi sannan ya sanya bakinsa saitin kunanta yace "meye na saurin hawa gado yarinya yanzu zan baki abinda kike buƙata, be jira cewarta ba ya haɗe bakinsa da nata, kissing ɗin dayake gudanarwa a gareta zazzafa ne hakakuma wasanni dayake aikawa ga sauran gaɓoɓin jikinta, baiyana irin yanayin Umaisa ta Samu kanta a wannan lokacin abune mawuyaci haka shima a ɓangaren Khabeer ɗin, Sosai ta firgije masa nanda nan jikinta ya ɗauki rawa sabida bakon lamarin da yay mata dirar mikiya.

Wani irin Abu takeji yanayi mata yawo a tsakiyar kanta  tamkar wadda ake jonawa lantarki, ganin dayayi rigar jikinta na neman wahalar dashi ne yasa ya rabata da ita ya jefarta gefe, daga nan ne fa yaya Golden ya fara losing control ɗinsa, nan take ya fara aika mata da zazzafan Saƙo daga wuyanta zuwa ƙirjinta wanda hakan yasa ta dinga banƙaro masa ƙirjin alamar ya ɗora daga inda ya tsaya, seda ya tabbatar da ya gama rikita ta sannan ya fara neman hanya daze kutsa ciki.

A zaton umaisa wannan daɗin me ɗorewa ne nan take ido ya Raina fata ta shiga ƙoƙarin ƙwatar kanta, cikeda zumuɗi gamida zazzafar ƙauna Golden ya jefa ƙwallonsa a raga, haka kuma be Sarara mata ba seda ya tabbatar da cewar ya maida ita cikakkiyar mace .

Wannan daran Umaisa tayi Dauriyar da khabeer betaɓa zaton zatayi kamarta ba a iya sanin dayayiwa rakin ta,  shida kansa ya taimaka mata ta gyara kanta sannan ya ɗakkota cak ya dawoda ita saman gadon ya kwantar da ita kanta a bisa ƙirjinsa yace " Allah yayi miki Albarka Fatima ya kuma sanyaki a cikin aljannarsa Firdausi maɗaukakiya.

Kasa magana tayi illah sauke numfashin wahala datakeyi, to abinka da matar likita nan da nan ya haɗa mata allura ya buga mata ita nan da nan wani gajiyayyen Bacci ya ɗauketa.  Zuba mata idanu yayi tamkar baze dena kallonta ba  sannan ya ƙanƙameta lokaci guda kuma ya ja bargo ya Rufesu  dashi daga nan kuma nima nayi ta kaina naja musu ƙofar nayi hanyar gidan Maheer lamiɗo.

Duk yanda naso na shiga gidan kasawa nayi sabida ko ina maheer ya garƙame da mukuli babu damar chubaɗo ta shiga ta kwaso muku Rahoton Daransu na farko shida Rumanatun sa, sedai dukda hakan na ɗan jiyo ihunta kaɗan yayin da oga maheer ke shirin kai ziyara Babban birnin na Rumana. Daganan kuma na kwaso ƙafafuna nayo waje. Lol

3years latter : wata kyakkyawar yarinya na hanga wadda bazata wuce shekara 2 ba se faman

tura baki takeyi a kusa da wani farin Dattijo, Dattijon ya kalleta yace "meya faru kuma noor badai fatan kuka sakeyi ba?  Yarinyar da aka kira da Noor ta sake turo baki tace "ba Lamiɗo bane ya ƙwace min abin wasana ba. Ta faɗa tana fashe masa da wani irin kuka.

Ummie ce ta ƙaraso gurin hannunta ɗauke da bottle water  tace "wllh bari Ubanku yazo ya tafi daku bazamu iya jaraban magana ba, ita Rumana ai dayake mejin magana ce mijinta yazo ya kwashe yaransa amma banda Umaisa da khaberr to wllh bazeyu ba suzo su ɗauki ƴaƴansu su tafi dasu.

Turo baki Noor tayi sannan tace "ai nima nafinson gidan mu akan nan dama grandpa yafi son mu ko Lamiɗo ?  Ta faɗa da ƙarfi tana kiran lamiɗon kamar badashi suka gama faɗa ɗazun nan ba.

Duk abinda sukeyi Mamie na kallonsu ta window ɗin dakinta tana dati daga sama.

Sosai khabeer ke nunawa Umaisa soyayyah shiyasa kullum take ƙara naike mai shi kuma yana biye mata, duk wani abou datake so yanayi mata shiyasa nan da nan tazama babbar mace kamar ba Umaisan nan me yawan shagwaɓa ba.........

Janta khabeer yayi suka faɗa kan gado suna dari lokaci guda kuma ya haɗe bakinsu guri guna suna masu kissing ɗin juna, nan da nan suka afka cikin wata duniyar me cikeda tarin albarkatu...

*Tammatbi'hamdullah A nan na kawo ƙarshen wannan littafi me taken KIYARDA DANI, abinda na faɗa daidai Allah ya bani ladansa kuskuren dake ciki kuma Allah ka shafemunshi.  Ya ubangiji kasa mu amfana da darussan dake ciki Ameen.*

*Ina miƙa godiya ta musamman ga Sisters Ɗina na Intelligent writers Association gaba ɗaya tareda Addu'ar ubangiji ya ƙara haɗa kanmu.*

*Haka kuma ina miƙa saqon godiyata gareku TAMBARI WRITERS  ASSO ubangiji ya ƙara ɗaukaka gabaɗaya*

*Semun haɗu daku a littafina me taken BAFULATANA RETURN🥰*

Sushmah